Qarfe uku na yammaci ta tashi tayi sallar azahar tana idarwa taji ana Kiran la'asar itama ta miqata ta zauna kan sallayar tana wasa da yatsunta taji an taba qofar ta dago suks hada ido Saida gabanta ya Fadi ganinsa cikin shigarsu ta sojoji fuskarnan a murtuke kamar bai taba dariya ba tsayawa yayi akanta mazantakar ta motsa ganin yanda duk ta firgice yasashi sassauta fuskarsa yace “ki kula da kanki zan fita wani aiki maybe sai gobe zan dawo akwai yaron gidannan Gebral duk abinda kike buqata ki fada masa banason yawo ki zauna a gda ki kula da kanki kinji?" Jinjina masa kai tayi tayi masa fatan Alkhairi ya fice yaja numfashi itakam mugun kwarjini yakeyi mata cikin kayan soji ko kadan batason ganinsa da kakinnan, tana gama abinda takeyi ta tashi ta gyara sakinta ta shiga dakinsa ta gyara masa ta fito ta gyara parloun ta zauna da karambani ta kunna kayan kallo tana kallon arewa24 batayi aune ba taji Kiran magrib ta miqe tayi ta dawo ta zauna.
Bata jima da zama ba taji ana buga qofar ta miqe ta bude da girmamawa qaramin sojan ya bata kayan hannunsa yace “Ogane yace akawo miki ki duba idan da wani abu da kike buqata ki fada" bude ledar tayi shirgin kayan zaqi ne sai ksyan tea tayi murmushin jin dadi tace “bana buqatar komai" juyawa yayi ya tafi ta kulle falon ta zauna tanashan sweet din da biscuits tana kallo bata tashi a falon ba sai 11:20pm taje ta kwanta.

Sunci gaba da rayuwarsu da Baffa'am dinta a garin Maiduguri komai yagani ya rakito daughtersa duk Wanda yasansa a wannan ritsin to yasan yarsa Meenah a tsarin tahowar da sukayi daga Jos wata guda zaiyi a Maiduguri ya koma Amma yanayin aiki ya zaunar dasu gashi har sun tafi wata biyar a cikin wata biyar dinnan gabadayanta bai zauna a gida yakai na wata guda ba ya yau Yana can gobe Yana can,
Fuskanta yayi yartasa tana shigs damuwar kadaici hakan yasa ya daukar mata malami take zuwa har gda yanayi mata lesson na boko dana addini, sunada maqota badon ransa naso ba yabata damar shiga maqotan dake sunada yarinya da bata wucce tsararta ba, daga lkcn data fara fitar ne abubuwa suka soma lalacewa sojojin sunga jar yarinya yar duma² kowa tambaya yakeyi itan wacece? Wadanda suka san gskyr lamarin sukan ce yar riqoce a wajensa wasu Kuma suce qarya ne satota yayi yayi Camping nata suke zaman zina wasu Kuma suce a barikinsa yayiwa wata ciki ta Haifa masa ita.
Duk yanajin wannan hasashen na mutane baisa komai aransa ba balle ya dameshi iyakar saninsa shidai jinta yakeyi a cikin jininsa qauna yakeyi mata ta gskyr da da mahaifi duk da a mafi yawan lokuta shaidan yakan qawata masa surar yar tasa koda baya gari ya rinqa ganin tanayi masa gizo.

Haka yake yaqarsa ya danni zuciyarsa a hankali wutar sha'awarta take ruruwa a zuciyarsa har ya kasance idan baiji ko ganta ba yakan rasa nutsuwarsa gabadaya akwai ranar da baya mantawa ya dawo Yana kwance a falo itakuma tana kitchen kasancewar yanzu batada aiki saidai tayi masa list na kayan girki wai ya siyo mata girkin yan gayu take koya gurin Maman Humaida to shima dake dan zuga gwaiwa ne ta hau qaya haka zaije ya lodo mata duk abinda ta buqata.
To yau dinma hakance ta faru takanas saboda siyayyar ta ya dawo yana bata ta fice a gdan bata shigo ba sai gaf da magrib gabadaya hankalinta yayi gaba tama manta da Baffa'am din nata yana gidan tana shigowa ta yage hijjab din ta jefar daga ita sai towel din da bai rufe mata cinyoyinta ba wani shocked ne ya hadu a jijiyoyinsa lkcn data kunna hasken daya kashe na falon yabi santala² santalan cinyoyinta da kallo yanajin tsartsatsin wutar azabar feeling yana bijiro masa.
Juyowar da zatayi suka hada ido taja baya da sauri tace “lah Baffa'am dama kananan" bai iya bata Amsa ba saboda yanayin da yake karba ya wucce tunani bin sassan jikinta kawai yakeyi da kallo abubuwa suna bijiro masa wawuyar kam bata gane komai ba tazo ta zauna kusa dashi tace “yau shinkafar zuma Mmn Humaida ta koyamin da miyar qwai Baffa'am in kawo maka zakaci?" Tana mgnr tana maida hankalinta garesa idanunsa daya jima da lumshewa tun zamanta ya bude akan qirjinta ya janyesu zuwa kan fuskarta suka shiga cikin nata sun wani qanqance sun kada sunyi jawur hakan yasata saurin zamewa takai hannunta cinyarsa tace “Baffa'am bakada lfy ne?"

Janye hannunta yayi cikin yanayi na dimuwa da tashin hankali ya miqe zaune gabadaya tsigar jikinsa ta gama tashi tana jorner masa hannunta sai yaji kamar ta ninka masa yanayin da yake ciki idanunsa suka qara qanqancewa jikinsa har wata rawa yakeyi shi kansa idan ya shiga irin wannan yanayin tsoron kansa yakeji da sauri ya miqe yabar gurin zuwa dakinsa saboda saqar da zuciyarsa takeyi masa ba mai kyau bace, ci gaba da ganinta a haka zai iya janyo afkuwar komai, tunda Allah ya hadasa da ita yake addu'ar kada Allah ya kawo ranar da hankalinsa zaikai gareta harma yaji wani abu game da itan Amma Ina ya makara.
Key yayiwa dakinsa ya fada katifarsa cikin yanayi na gushewar hankali ya rinqa miqa Yana shafa mararsa zuwa twins dinsa yana danna saman dick dinsa a hankali tare da mulmula kanta yana nishi Yana jan numfashi, ya dauka dogon lkc a haka kafin ya samu relief ya sake gyara kwanciyarsa rigingine Yana mayar da numfashi zuwa lkcn ya fara azabtuwa da feelings Yartasa tabbas idan yaci gaba da kadaicewa tsakaninsa da ita to kuwa zaayi abin kunya wanda baya fata burinsa bai wucce yaga ya samu damar aurar da ita da qimarta ba zaiji kunya zaiyi kaico ace shine ya zama silar lalata amanarsa da Allah ya dauka ya bashi.
Juhud ta jima a tsugunne a gurin tana tunanin abinda damun Baffa'am din nata duk jikinta yayi sanyi ko kadan batason taganshi cikin yanayi daba na walwala ba, miqewa tayi ta shige dakinta ta Sanya rigarta ta zauna tayi tagumi tana tunanin halin da Baffanta yake ciki miqewa tayi ta fita ta nufi dakinsa ta qwanqwasa ta jima tana bugawa kafin taji an murda qofar an bude ganinta a tsaye yasashi furzar da iska yace mata.

“Ya akayi? Yanayin da yayi mgnr yasata dagowa tayi saurin sunkuyar da kanta bazata iya kallon idanunsa ba yau bataga alamun rahama a tattare dashi ba, tsawa ya daka mata data sanyata ja baya da sauri tayi qwalqwal da ido hawaye ya balle mata ya cafki hannunta yace “ba mgn nakeyi miki bane?" Cikin in...Ina da rawar murya tace “bansan laifin da nayi maka ba Baffa'am am don Allah kayi hqr bazan qara ba banason ganinka da fushi bayayi maka kyau...." Yanda ya kafeta da idone yasata katse maganar ta zauna a gefen katifar ta kama shusshura qafa tana kuka, abin ya bashi dariya yarinyar kullum qara sangarcewa takeyi ya lura shagwabarta bata tashi sai taganshi cikin yanayi kawai ta mayar dashi wani qaramin yaro shima Kuma da sakarci sai biye mata yakeyi.
Ganin da gaske takeyi ba shiru zatayi ba indai ba rarrashinta yayi ba yasashi zama yace “to me kikeso nace miki ne na fada miki banason kina zama tsirara ki rinqa suturce jikinki Meenah kinqi gani kikeyi kamar takura miki nakeyi haba don Allah kasheni kikeson yi ko?" Dagowa tayi da mugun sauri tace “kisa Baffa'am nidin?" Daga mata kai yayi da karsashi yace “Yeah indai kikaci gaba da nunamin kanki a yanayin da kika zomin yau zan hadiye zuciya na mutu ko Kuma naje nakai kaina gurin yan boko Haram su kasheni Kinga kin huta sai kiyi rayuwarki ke kadai......." Baiyi aune ba yajita a jikinsa ta maqalqaleshi tana kuka tana cewa “ka daina fada Baffa'am banason ka mutu ni ka daina Allah na daina kaji?"

Sosai yaji yanayi a jikinsa tabbas lkc yayi daya kamata ya nisanta kansa da Meenah shaidan ya fara galaba ga zuciyarsa falsafa tana neman qwace masa dole ya nemi wata mafitar, janyeta yayi yace “shikenan na daina cewa kema ki daina tashi kije dakinki ki kwanta dare ya fara Saida safe" miqewa tayi har taje bakin qofar ta dawo tace “bazaka mutu ba ko?" Jinjina mata kai yayi yana kallonta tayi dariya ta fice ya miqe ya rufe qofar ya dawo ya zauna Yana tunanin mafitarsa ta gaba.
Wayarsa ya dauka ya lalubo number mahaifinsa bugu biyu ya daga cikin barkwancinsa yace “soja marmari daga nesa yau ranar tunawa da iyaye ce ta duniya kenan?" Murmushi yayi a kunyace shi kansa bazai iya tuna rabon da ya Kira mahaifin nasa ba kusan tun farkon dawowarsu Maiduguri daya kirasa yake fada masa yayi masa mata a daura yar sarki Badamasi yayansa me rasuwa tun ranar ko Mai martaba ya kirasa baya dagawa shi a dole yayi fushi, Ajiyar zuciya yaja yace “dama wata alfarma nake nema gurinka Abba don Allah karkace aa nasanka me tausayi da jinqai ne kai Kuma nasan idan kaji zaka jinjinawa qoqarina wajen ceton rayuwa da nayi" murmusawa Mai martaba yayi yace “inajinka Abdulrasheed meye Kuma ya faru?" Nan ya zayyanewa mahaifin nasa komai a qarshe yace “so yanzu wata tafiya ce ta tasomin zuwa Benin shine nake neman amincewarka na kawota nan gida Katsina suci gaba da rayuwa dasu Ya'isha da Amrah Abba inajin yarinyar a cikin jinina banson wani abu ya taba martabarta shiyasa kaga inata takatsantsan wajen kiyaye amanarta" shiru Mai martaba yayi

Yana nazarin kalaman dannasa can yaja fasali yace.

“Kayi ganganci Rasheed ka zauna da yar Amana dagakai sai ita Ina tunaninka ya tafi da tun farko bakaji a ranka Bari ka kawota cikin yan'uwanka ba haba Son wannan tunanin naka na quruciya yaushe zai barka kawai ka dauki yarinya kuyita yawo a daji babu lissafi haka, shi da da dukiya ai na kowa ne Allah kadai yasan me morarsu sannan shi riqon maraya alkhairansa yawa gareshi, yanzu kam dare yayi Amma gobe lallai ka taho da ita itama zatafi samun sakewa cikin yan'uwanta mata"
Dadi sosai Rasheed yaji ya miqe yace “ok Abba na gde sai kajimu" kashe wayar yayi ya fita daga gdan bashi ya shigo ba sai wajen daya na dare da kaya niqi² ya ajiye a falo ya shige dakinsa ya kwanta, batasan bikin da akeyi ba tun asuba ya tashi cikin bacci taji ana buga qofar ta tashi ta bude masa baiko kalleta ba yace “kije kiyi wanka ki shiryo tafiya ce ta sameni ta gaggawa zan kaiki Daura zaki zauna a gdanmu nasan zaki samu sakewa fiye da nan"

Tunda ya fara mgnr zuciyarta ta karye hakanan taji tafiyar bata kwanta mata ba Amma jin yace gdansu saita dan samu nutsuwa ta juya ta shige bathroom din ta sakarma kanta ruwa tayi brush tayi sallah suka dauki hanyar Katsinan Dikko tunda suka taho babu me cewa wani qala kowa da abinda yake saqawa a ransa baitaba kawo cewa masomin faruwar komai zai fara ne daga zuwanta Masarautar Daura ba tunaninsa baitaba bashi zuwan nata zai zamo makullin kullewar duk wata nutsuwarsa ba.
Balle ita da batasan komai itadai kawai taji jikinta yayi sanyi ne da tafiyar ba sanin ko Ina tayi ba don haka batasan iya lkcn da suka dauka ba kafin su shiga cikin garin Daura itadai taga sun nufi wani shararren titi yanata maka gudu har suka shiga qwaryar birnin Daura ya nufi wata hanya da zata sadashi da gdan nasu babban gidane ginin sarautar zamani da aka qawatashi da fentika na daukar hankalin me kallo tun daga qofar farko ta shiga gdan taga ana zubewa ana gaishesa Yana daga mawa mutane hannu itadai bin bangarorin gidan takeyi da kallo tana mamakin girma da tsaruwar gdan har sukakai harabar asalin gdan sarautar yayi parking ya bude ya fita ta saman bene Ya'isha ta hangosu ta sauko a guje tana “ga Yaya ga Yaya" da gudu Amrah ta fito itama suka fito Yana ganinsu ya daure fuska duk sai sukaja suka tsaya daqyar Ya'isha tayi qarfin halin matsawa ta kama hannun Juhud tace.

“Masha Allah Yaya babyn kyakkyawa jiya har mafarki nayi da Mai Martaba ya kiramu ya fada Mana zamu qara yawa munyi sabuwar sister"
Sakin fuskarsa yayi da yaji kalamanta Amrah ta kama dayan hanun tace “ki saki jikinki a

gdannan rayuwar yanci akeyi babu me takura miki saidai in ke kika takurawa kanki" shidai bai kulasu ba yasa aka dauki kayan suka rankaya ciki Addah Abulle ce ta miqe ta tari Juhud da fara'arta tana cewa “lale lale sannu da zuwa Aminatu barka da zuwa Sarki Waziri Fam" sunkuyar dakai tayi tare da rusunawa ta gaisheta, Dagowar da zatayi idonta ya sauka kan Mom hakanan taji wata faduwar gaba ta musamman tayi qasa da kanta murmushi Mom tayi tace “masha Allah kamar sarauniyar Aljanu wannan ya taka Rasheed dakyau take" shafa sumarsa yayi Ikcn da yake zama yace “wlh Mom kinganta nan sai wahalar dani takeyi daughter ga Mom dina ki dauketa matsayin kakarki kinji?" Dariya sukayi dukkansu Mai Martaba dake saukowa daga sama yace “Iyee kai Ina jikar tawa take zo ki bani kudin goro" rufe fuskarta tayi tana dariya ta fada jikin Rasheed ya shafa kanta yace “kunga fah matsalarku zaku tsoratamin ya da maganarku"momy ce ta sakar masa ranqwashi tace “qaryan banza wai yarsa ko kunya baiji baba babu mata kekam Amina kinyi sa'ar uba aure sai inda hali yayi Kuma an shiga kwale$^{2}$ yo uba baiyi ba ya isa ya takurawa yarsa tayi ne" kafin wani yayi mgn Kareem da Muntaz suka shigo Muntaz yayi wani ihu yace “hyeee My Bro ashe kan...na.....han....ya....." Mgnr a rarrabe ta qarasa fita idanunsa nakan Juhud inda Kareem yayi murmushinsa me tsada yace “ Barakallahu ahsanal Khaliqin, tabbas ubangiji ya kyautata halittarsa" Bro wannan babyn fah?" Cewar Muntaz wani mugun kallo Rasheed ya watsa masa zaiyi mgn Ya'isha ta cafe da cewa “kayy kama kanka wannan babbar kadara ce yar Big boss ce wlh kanayin wargi harsashi zaiyi nutso a kwanyarka"...........

_Hmmm akwai kwantacciyar qura cikin wannan gda ga Juhud a tsakiyar zakuna uku fah kowa zuciyarsa na aika masa da saqo akanta🤔_

*THIS BOOK IS NOT FREE... REGULAR GROUP 300  VIP 600 VIA BANK ACCOUNT 0255526235 FAUZIYYA TASIU UMAR GTBANK OR CARD FOR THIS NUMBER  09013718241 ONLY WHATSAPP OR VTU ONLY FOR DIS 09031307566*

*DON ALLAH IDAN KIN/KA TURA KUDINKA BANA BUQATAR DOGUWAR GAISUWA KAWAI EVIDENCE OF PAYMENT DA SUNAN LITTAFIN DA KIKESO NAKE BUQATAR GANI KO BANA ONLINE KIBARMIN IN NA HAU ZAN GANI KUMA ZANYI ADD NAKI A GROUP DINA COURSE MUTANEN DA YAWA.*

*Shares Please*

*Oum Hairan*
[7/17, 5:59 PM] Oum Hairan: *JUHUD*

*(OUM HAIRAN)*

*(Pure love sex nd romantic story)*

*LAST FREE PAGE TEN 10*

*Qarshen Free page na labarin nan kenan idan baki biya ba kiyi sauri ki hanzarta biya ta wannan hanyoyin dake qasa*
*Regular group 300  VIP 600 via bank Account  0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank  or card for This number  09013718241 only WhatsApp or vtu only for dis 09031307566*

*DON ALLAH IDAN KIN/KA TURA KUDINKA BANA BUQATAR DOGUWAR GAISUWA KAWAI EVIDENCE OF PAYMENT DA SUNAN LITTAFIN DA KIKESO NAKE BUQATAR GANI KO BANA ONLINE KIBARMIN IN NA HAU ZAN GANI KUMA ZANYI ADD NAKI A GROUP DINA COURSE MUTANEN DA YAWA.*

*_Sorry fans dazu an samu kuskuren editing a wancan page 10 din wani bangare na labarin ya yanke ga cikakken nan_*

*CIGABA*
Zama yayi kusa da Rasheed Yana shafa kansa yace “Big Boss Ina kasamo wannan ba'indiyar yarinyar......" Mgnr ce ta maqale saboda kallon da yaga Yana watsa masa yasan tsaf zai fashe masa baki, miqewa yayi sumsum yabar gurin ya nufi dakinsa Yana saqa abubuwa a ransa, baitaba ganin kyawawar halitta irin wannan yarinya ba tabbas zaa huta da ita saidai idan mugunta tasa ta hanashi sakewa.
Addah Abulle ce ta janyeta daga jikin Rasheed ta dubi Amrah tace “ku kaita dakinku ku bata ruwa tayi wanka kuzo ku hada mata abinci idan taci ta huta don Allah kada ku dameta da surutunkun nan kubarta tayi bacci ko na awa daya ne miqewa sukayi su biyun suka riqe mata hannu sunyi nisa ta juyo da sauri idanunta akan Rasheed tace “ayyah Baffa'am Amma ba tafiya zakayi ba ko?" Dagowa yayi daga kallon wayarsa ya dubeta sosai yace “bakison na tafi ne?" Dagansa kai tayi cikin karyewar zuciya tace “idan ka tafi waye zaike bani abinci waye zaike koyamin karatu sannan waye zaike daukana Yana zagawa dani gari Kuma waye zaike rarrashina?"

Dukkansu ta Sanyaya musu jiki Kareem dake zaune yace “na dauki wannan nauyin zanke koya mata karatun qur'ani Dana bokon zanke daukarta Ina kaita tana ganin garin duk inda takeso zuwa a garin Katsina na dauki wannan alqawarin....." Dagansa hannu yayi yace “na riga na bawa su Ya'isha wannan damar sune zasuke daukarta suna zagawa da ita kai aikinka koya mata karatun qur'ani da tajweed tunda kai balarabe ne shikuma wancan mashiriricin ka fada masa ya zama malaminta na turanci bayan wannan Kuma banson wata alaqa tsakaninsu" jinjina kai Kareem yayi yana tuntunin alaqar Muntaz da wannan baquwa gabadaya Muntaz ba mutum ne me alqibla ba Amma hakanan zai qyaleshi kowa yayi aikinsa,
Miqewa yayi ya fice ya nufi bangarensa ya bude ya shiga an gyara masa shi tsaf ya cire kayansa ya shiga wanka ya fito ya zauna yana duba wasu abubuwa a wayarsa wata baiwa ta shigo ta gaisheshi ta aje masa abinci ta fita bude abincin yayi ya lumshe idonsa Addah Abulle tanaji dashi abinda yafi qauna ne tayi masa tuwon shinkafa miyar danyan kubewa ya kuwa ci abincin sosai ya kwanta ya huta bai fito ba sai yamma da shirinsa tsaf ya fito cikin shirinsa na tafiya Illorin zuciyarsa gabadaya babu dadi sai yanzu yakejin kewar tafiya yabar yartasa.

Cikin gidan ya shiga Momy ya tarar a falo suka qara gaisawa yana rarraba ido bai hango koji motsin yammatan ba ya dubeta yace mom Ina su  Ya'isha" murmushi Mom tayi tace “sun shiga gari ya qamshin bararraken daddawa" da sauri ya dago yace “harda daughter?" Yagar apple dinta tayi tace “itama ai akarada ce sunanan suna hirarsu wancan mashiriricin yace su tashi suje kallon ruwa tace itama zata carton biyu sun zama uku dama sai abinda ya qaru ai Mai Martaba da daurewa qarya gindi dubu hamsin yabasu wai ko zasuga wani abun suyi sha'awa a

hanya"
Zuciyarsa ce ta karya ya taho da qwarin gwiwarsa yace “banason yawon nan Mom don Allah asa ido kanta Kinga itadin amanace riqon maraya yanada wahala abu kadan zaka karkace ka fada hallaka" tabe baki tayi tace “to Isah Wazirin Kano zaa kiyaye" yasan gatsali tayi masa ya juya idanunsa ya ciko da qwallah ya miqawa Addah Abulle dake saukowa daga sama wata takarda yace “ki bawa daughter Addah naso muyi sallama da ita  hakan bata samu ba don Allah Adda ki kulamin da ita Amana nabarta gareku" dariya abin yabawa Addah Abulle tace “oh Ni Zainabu Abu Abdulrasheed abunnaka azimun ne wannan ya taka da matsayi take saboda rabuwa da ita kake kuka to kayi hqr guda ka bari guda zakazo ka tarar insha Allahu"
Murmushin jin dadi yayi ya juya ya fice driver yajashi sai Kano daga Kano jirginsa ya daga sai Illorin zuciyarsa gabadaya babu dadi ji yake kamar yaje ya dauko yarsa suci gaba da rayuwarsu tare, daqyar yake cusawa zuciyarsa dangana saboda yasan wannan matakin shine kawai gatan da zaiyima Meenah kenan yabarta a Daura a cikin ahlinsa ko ba komai zatayi karatu koda baya gari Kuma zata samu kulawa.

Koda ya sauka Benin zuciyarsa kasa nutsuwa tayi hakanan da ya tuno da Meenansa sai ya nemi nutsuwarsa ya rasa  zamansa kwanciyarsa tashinsa Meenah ce keyi masa gizo da salon shagwabarta me tsayawa a rai da Hana zuciya sukuni ya rasa irin shaquwar da yayi da ita da bayajinta akan sauran qannensa, da taimakon addu'a ya samu damar ci gaba da aikinsa ya dangana saboda yasan duk nacinsa yanzu bazai samu damar karbarta hanun Mai Martaba ba.
Itama farkon tafiyarsa gabadaya rikice musu tayi suka kasa gane kanta saita zauna tayita kuka idan aka tambayeta meye sai tacce Baffa'am dinta take tunani idan kaga ta saki jiki to Mai Martaba ne ya kirata yasata a gaba yake zolayarta to yanzu zata ware ta kama harkokinta a haka har ta saba da kadaicin rashin Baffanta ta saduda ta saki jiki cikin yan'uwanta Ya'isha da Amrah.
Ya kasance duk safiyar duniya idan su Ya'isha sun tafi makaranta Kareem zaisa a kirata su zauna suyita karatunsu yanajin dadin koya mata saboda nandanan take daukewa a falo suke zama gaban kowa har Mai Martaba suyi karatun indai kaga sun kebe to baqi akayi hayaniya bazatabar karatu ya shiga ba, shiko Muntaz duk sanda zai koya mata saidai yajata Garden su kebe ya rinqa koya mata karatun bokon shima yanajin dadin koya mata Amma dake yasa almundahana a ransa duk yanda zatakai da ganewa sai yace bata gane komai ba haka zatayita qunci ta Hana kanta sakewa saita iya turanci saboda baqin nacinta har tafi mayar da hankali akan bokon fiye da karatun addinin Amma kullum a bata iyaba take.

Hikimarsa shine idan ta matsa da son saita iya to zaiyi amfani da damar wajen cimma burinsa, babban abinda yake damun Muntaz yanda Kareem yake sanyawa duk motsita idanu sau tari idan suna garden din suna darasi shikuma sai yaje can gefe ya kama buga qwallo Sarai Muntaz

ya fahimci sabodashi yakeyin hakan  wannan dalilin yasa ya tattara koyarwar ya watsar.
Tayi nacin tayi nacin harta hqr gashi jarabawar WAEC din da zasu zana da Baffa'am dinta yasa Mai Martaba ya biya mata takusa dama da lesson din take gane abubuwa. Tanason bawa Baffa'am dinta mamaki musamman da yace indai batamai da hankali taci WAEC ba rugarsu zai mayar da ita wannan abu ya qara tashin hankalinta  ta rasa abinda keyi mata dadi.
Yau ma kamar kullum suna zaune a daki Ya'isha na chat Amrah na karatun novel itakuma ta rafsa uban tagumi sai tsiyayar hawaye takeyi batason tayi asarar wannan damar Amma ta lura damar batasonta kufcewa zatayi.......

Dagowa tayi tana sauke numfashi Ya'isha tace “kina damun kanki da karatun nan nifa da Mai Martaba zai yarda Allah inayin candy aure zanyi miqewa Amrah tayi tace “mema kikaji da son aure  bakiga kaya ba Nifa ko a yarda ko kar a yarda Allah sai anmin aure na gaji da cin na Allah ya isa" tabe baki Ya'isha tayi tace “waisu tsoffin nan so suke su mayar damu bahuna nifa Allah badon kin takura ba da babu abinda zaisa na zubar da cikina gara susan mun girma munsan dadin maza su auraddamu ko su dauki jikokin soyayya"
Katsesu Juhud tayi da cewa “nikam don Allah kubani mafita Allah nafison karatun da komai ni nasan ma Baffa'am dina bazaimin aure ba" miqewa Ya'isha tayi tace “common baby tashi muje Ni nasan bro gajiya yayi da aikin banza" da jin dadinta ta miqe suka rankaya zuwa dakin Muntaz Yana kwance samsn gadonsa da system a gabansa Yana kallon wani BF suka shigo.
Rufewa yayi ya lumshe idonsa cikin yanayi me ban tausayi Juhud tace “duk da bansan laifina gareka ba Ya Muntaz Ina mai baka hqr don Allah ka taimaka kaci gaba da yimin lesson dinnan wlh Baffa'am dina yace idan na Fadi jarabawa saiya mayar dani rugarmu Kuma idan na koma kasheni zasui......" Murmushin jin dadi yayi dama tazo masa har daka ya tashi zaune yana sake zubawa qaramin bakinta idanu yanda take sarrafashi ya bashi sha'awar ya tsotsa ya lashe lips dinsa ya miqe zaune yana kallonta harta gama yaja numfashi tare da shafa sumarsa yace.
Karatun addini shine akeyinsa kyauta ko sadaka Amma na boko dole sai an kashe kudi masu nauyi  Juhud bakida kudin biyana anma kinada kadarar da tafi kudi a gurina idan kin amince zaki mallakamin kanki da lkcnki nikuma na amince zan dauki duk wani lkc na na baki shi domin samun damar cin jarabawar WAEC din da zaku zana amatsayinki na mara background din nunawa saa ba iyakar lesson ba hatta abubuwan da suka shafi kudi zanyi mikishi daga naira daya har zuwa fan taba sama indai kin amince......"

Kallonsa  sukayi da rashin fahimta suks kslli juna Ya'isha da alamu suka nuna ta fahimci wani abu tace “Amma ya Muntaz ai ba ita tasaka aikin nan ba Big Cele ne kai kana ganin hakan zai yuwu idan yasani kana ganin zakaksi labari?" Miqewa yayi yana murmushi yace “to saime don ya gane ai yasan baa aikin banza a duniya bayan hakama shidin meye bayayi akwai ma dan bariki irinsa ne da idons nashs kamasa ya dannewa mace kai Yana soka mata wutsiya idan nayi

yunqurin tonawa yace zai fasamin kai da Gum balle ma ni bazan taba shigarta ba kawai zan hutane da ita common Ya'isha ki ganar da ita itama zataji dadi rayuwar duniya daga Kano sai Habuja aljanna tamai raboce"......

Bai jira abinda zasuce ba ya fice daga dakin yabarsu zaune da sakakken baki suna kallon kallo ta kalli Ya'isha tace “meye yake nufi da inada kadarar da tafi kudi Ya'isha don Allah Amrah idan kun gane ku ganar dani nikam daqiqiya ce ban gane komai ba" wata iska Ya'isha ta furzar tace “akwai matsala ne Juhud muje rabuda wannan dan iskan ni dama nasan abinda yaketa yiwa raragefe kenan" fita sukayi har zuwa lkcn kanta a kulle yake kalaman nasa sunayi mata yawo a qwanya saidai ta kasa gane inda zatayi musu matsugunni Baffa'am dinta bariki yana taba bariki? Meye ma ma'anar barikin?"
Da wannan tunanin suka shiga gda tun daga nesa suka hango Kareem tsaye jikin mota ya zuba musu ido kamar me nazarinsu har suka qaraso suka giftashi kowa da abinda yake saqawa a zuciyarsa “Aminah" taji an kirata da asalin sunanta turus sukaja suka tsaya dukkansu ya tako cikin takunsa na isa ya iso gabanta ya kalli qannen nasa dukka suka watse ya rage daga ita saishi, hannu yasa ya dago kanta ta lumshe idonta tana shaqar qamshin turarensa me tsayawa a rai yaja numfashi tare da furzar da wata iska me zafi yace “duk da kasancewata abin gudu a gurinki saboda Ina doraki akan tafarkin daidai Aminatuh bazan fasa fada miki ba Babu biyayya gurin abokin halitta wajen sabawa ubangiji zanso Kuma zanyi alfahari idan ya kasance nasihar da nakeyi miki daga ranar da kika tsinci kanki cikin wannan ahli me rangwamen tarbiyyar islama ta zame miki abar tunawa a duk lkcn da wani abokin halitta ya gayyaceki domin aikata sabon Allah.
Nasani cikin watannan da kika samu goyan baya daga Momy kin fara biyewa su Ya'isha kina binsu kuna fita chilling kune har Dikko Club wai abin takaicin hardake a cikin yan shiga rawa bama ki tsaya iyakar kallo ba"

Kallonsa tayi da sauri idanunta ya ciko da qwallar da tun dazu take maqale jikinta ya dauki rawa, murmushi yayi yace meye naki na firgita bayan Baffa'am dinki baisan rayuwar da kika zabawa kanki ba?" Sake firgita tayi bakinta na rawa tanason mgn ya katseta da hannunsa yace “karkicemin komai Aminah kinji dadin zuwa club har kina bada tabbacin gobe ma zaki koma ko?"
Girgiza masa kai tayi haqoranta na rawa tunaninta Ina yasan wannan sirrin da sukayishi iyakar su uku sukayi alqawarin bazasu fadawa kowa ba?" Murmushi yayi ya kama hannunta yace “inasonki da gasken gaske Juhud meye ribarki idan aka tashi mahaifanki aka nuna musu ke matsayin yar rawar Club?"
Girgiza masa kai tayi jikinta duk yayi sanyi tace “Allah Amrah ce tajani tace dole saina shiga Kuma Dana shigama tsayawa nayi ban iya irin rawar da sukeyi ba"

Zubanta ido yayi Yana kallon yanda duk ta tsorata yaji dadin hakan ya shafa kansa yace “da nayi niyyar fadawa Baffa'am dinki Amma idan kikayi alqawarin bazaki qara zuwa ba to zan rufa miki asiri ke qilama ya sani fah don duk motsin da zakiyi abune me sauqi su sani din" batasan sanda tace “insha Allahu baima sani ba bakuma zai sani ba bazan qara zuwa ba"
Yaji dadin hakan yace “ok meye kukaje yi a dakin Muntaz?" Nan taji wani dukan saukar aradu ta dago suka hada ido mugum kwarjini ne dashi shima kamar Baffa'am dinta duk iyakar zille zillensu idan aka hadasu dashi basa iyayi masa qarya, cikin in...Ina tace “ha....hqr mukaje mubashi yaci gaba dayi Mana lesson shine yace wai saidai na rinqa biyansa Wai banida kudin biyansa Amma inada kadarar da tafi kudi ni na kasa gane me yake nufi Ya Kareem ko kai ka gane?......"
“Wht?" Ya furta da qaraji ta dago da sauri ga mamakinta sai taga gabadaya ya hargitse jikinsa har wata rawa yakeyi idanunsa sun kada sunyi jawur ya dafe kansa yace “innanillahi wa innah ilaihir raji'un"
Daidai lkcn Muntaz ya fito cikin shirinsa na tafiya qwallo hangosu tsaye yasashi daure fuska ya nufi motarsa ya bude zai shiga Kareem ya daga murya ya kirasa ya tsaya batare daya juyo ba, matsawa yayi bayansa yace “bantaba tunanin akuyancinka yakai ka rinqa farautar lalata rayuwar Aminatuh ba sai yau so inason kasani wlh tallahi idan naji ko naga wani abu akasin daidai ya faru da Juhud billahil lazi saina tona maka asiri dan iskan banza dan iskan wofi duk kuyangin gdannan da bayi Basu isheka ba saika tsallaka kan yar Amana......." Dakatar dashi yayi yace “dakata Mal kaima fah abinda nakewa shine kakeyiwa duka dodo daya mukewa tsafi aikin banza kaine kake tunanin ci da addini ni tun tuni na dade da fahimtar ka dade da lalube......." Wani gigitaccen mari ya sauke masa ya shaqesa suka kama kokawa ya rinqa gwara masa kai a jikin bishiya Mai Martaba dake tahowa ya hangosu ya iso da sauri shida dogaransa daqyar ya bambare hannun Kareem daga wuyan Muntaz, duk da haka Muntaz bai rusuna ba cewa yake wlh ko kanaso ko bakaso tunda nayi niyya saina aikata qarshen kishi kasa a daura maka aure da ita yau dinnan ko a gdanka take saina mayar da yawuna saidai idan mutuwa nayi"............

*THIS BOOK IS NOT FREE... REGULAR GROUP 300  VIP 600 VIA BANK ACCOUNT 0255526235 FAUZIYYA TASIU UMAR GTBANK OR CARD FOR THIS NUMBER  09013718241 ONLY WHATSAPP OR VTU ONLY FOR DIS 09031307566*

*DON ALLAH IDAN KIN/KA TURA KUDINKA BANA BUQATAR DOGUWAR GAISUWA KAWAI EVIDENCE OF PAYMENT DA SUNAN LITTAFIN DA KIKESO NAKE BUQATAR GANI KO BANA ONLINE KIBARMIN IN NA HAU ZAN GANI KUMA ZANYI ADD NAKI A GROUP DINA COURSE MUTANEN DA YAWA.*

*Oum Hairan*
[7/18, 6:49 PM] Oum Hairan: *JH011*

*(Pure love sex nd romantic story)*

*Free page ya qare idan kinsan baki biya ba don Allah kada ki karanta, bansanki ba bare na yafe miki haqqina dake kanki*

*Regular group 300  VIP 600 via bank Account  0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank  or card for This number  09013718241 only WhatsApp or vtu only for dis 09031307566*

Cikin fusata Kareem yake qoqarin qwacewa yana huci Yana cewa “an fada maka kowa ma irinka ne mara Imani mara tsoron Allah Wanda zina tayiwa kanta cikin rayuwarsa" rirriqeshi suka sakeyi Dogari Ado ya kama Muntaz yasa a mota suka fice asibiti yakaishi akayi masa dressing din wajen da Kareem ya faffasa masa kai suka juyo sai huci yakeyi Yana furzar da iska baqin ciki ya hanashi furta ko kalma daya, Wai akan wannan tsintacciyar yarinyar Kareem ya fitar masa da jini wani huci ya furzar ya dunqule hannunsa ya daki dayan dashi yace “wlh saina wargaza wannan yarinyar tunda abin ya zama  rashin mutunci ni zaaciwa mutumci akan wata banzar bafulatana mara galihu"
Shidai Ado bai kulasa ba har sukaje gda fada suka wucce domin amsa Kiran Mai Martaba acan suka tarar da Kareem suka watsawa juna wani mugun kallo na kiyayi kanka, Mai Martaba ne ya nunawa Muntaz guri ya titsiyesu akan su fada masa meye ya hadasu har suke neman illata junansu?" Kareem irin mutanen nan ne masu baqar zuciya idan ransa ya baci baya mgn shikuma Muntaz ko hauka yake bazaice don yayiwa Juhud tayin shaidana bane yasa aka illatashi, tsawa Mai Martaba ya daka musu yace “ku tashi ku bani guri tunda bazakuyi mgn ba sakarkaru kawai" miqewa sukayi kamar zasu bangaji juna suka fita a daidai inda zasu rabu kowa ya shiga bangarensa Muntaz ya dafa Kareem yace “mu hadu a filin qwallo sabon wasa zan take leda ko ta tsiya kota tsiya tsiya"

Murmushi Kareem yayi sai yanzu zuciyarsa ta fara sauka yace “bazan hanaka mummunan tunaninka ba saidai inaso kasani ita zina yado takeyi idan kayi da yar wani zaayi da taka idan kayi da matar wani zaayi da taka kazalika idan kayi da qanwar wani zaayi da taka wannan kadai ya ishi me hankali nutsuwa Aminatuh ba kowa bace marainiya ce me rangwamen gata idan da

Allah yaso ta lalace saiya barta tayita galantoyi a duniya har ta samu abokin lalacewarta so baiso hakan ba saiya jefata hannun Big Cele duk da gurbatar yanayinsa ya kawar dakai gareta domin riqe amanar Allah kullum abinda yake fada a kula da ita itadin tanada qarancin hangen nesa kaico abin tur wai ace a gdannan zata lalace......"
Dakatar dashi yayi da cewa “Dama kaje ka dauki speaker ka fara tafsir a masallacin fada qila da ka samu sadaka Dan m qauye kawai da ya kasa fahimtar rayuwa" shigewa yayi part dinsa ya banko qofar yabar Kareem tsaye cikin tsananin mamakin wannan qazamar rayuwar ta yan'uwansa qwafa yayi ya shige dakinsa ya fada gado Yana juyi tabbas akwai aiki a gaban maza shikam da Abba zai barshi daya nemi auren Juhud cikin lkc qanqani kodon ya tseratar da ita daga sharrin Muntaz Amma yasan abune ma bame yuwuwa ba tunda bai gama karatunsa ba a burin irin na Mai Martaba ba mazaba yaransa mata na bayayi musu aure sai sun hada degree certificate maza kuwa sai sunyi Masters degree ya samawa kowa gwaggwaban aikin yi.

Lumshe idonsa yayi cikin yanayina tausayin kai da Kuma abar qaunar tasa shikam zaiyi qundunbalar furta mata koda bazaa Basu damar soyayya ba Allah ya jarabceshi da muguwar qaunarta baiji a ransa zai iya sakacin Bari ta kubce masa ba, da wannan tunanin yaji ana Kiran sallar magrib ya tashi ya fita domin zuwa masallaci ya jima a masallacin sannan ya tashi ya nufi cikin gdan a falo ya tarar dasu dukkansu suna kallon wani Indian series gabadaya hankalinsu ya bayu ga kallon da sukeyi duk cikinsu babu me motsin kirki.
Ya jima tsaye akansu bai gano Juhud ba can ya hangeta kwance a kujera da littafi a hannunta da alamun nazari takeyi, zuciya yaja ya nufeta inda Momy tabisa da kallo ya tsaya akanta ya sanya hannu ya zare littafin ta dago idanunta ta saukesu akansa ta kawar dakai, sake jan numfashi yayi ya zauna a gefenta yace “Ina Ya'isha da Amrah?" Miqewa tayi zaune ta duba bata gansu ba ta dawo da dubanta gareshi tace “bansan sanda suka fita ba" jinjina kai yayi yace “wato Addah kun qyale yarannan suna abinda sukeso babu me iya tsawatar musu basuda aiki saidai suyi wanka su fice su kwaso wannan su kwaso wancan samari saikace budurwar karya idan anyi mgn Momy tace farin jini ne don Allah wannan wacce rayuwa kuka zaba musu a matsayinsu na mata da zasu tafi gdan wasu?"
Dubansa Addah tayi tace “nikam bansan da wanne yare zan ganar dakai ka gane ba Abdulkareem wlh nafika jin ciwon wannan abin da yarannan sukeyi to baka isa kayi mgn bane kawai sun samu daurin gindi daga Mai Martaba abinda sukaga dama shi sukeyi kayi mgn suje su fadaka dashi yazo yayita fada shiyasa na tattara na zubansu ido kaima yanzu nemanka yakeyi sunje sunce masa kaine ka hana Aminatu zuwa chilling"

Jinjina kai yayi ya bude littafin ya fara dubawa ya dubeta yace “ni ba turanci na karanta ba Amma zanyi bakin qoqarina wajen ganar dake abinda Allah yasa na fahimta ki tsara lkcnki da safe zanke miki darasin addini da dare Kuma na boko hakan yayi miki?" Rufe fuskarta tayi tana

dariyar jin dadi tace “wlh yayi Ya Kareem na gde Allah yabarmana kai" murmushi yayi yace “dole saiya kasheni tashi muje ki nunamin assignment dinku na qarshe da Muntaz nagani saina samu gabar dora miki"

Miqewa tayi tayi tsalle ta rungume Addah Abulle tace "idan na zama gwamna Ya Kareem zan fara kaiws makka" dariya sukayi Momy tace “baki rabo da shirme me sunan yaya to Ina kika baro Baffa'am din naki ni kwana biyu ma banjinsa ko yanayin aikin ne?" Cokalo baki tayi tace “bayan ya daina sona ko waya ya Kira baya cewa abani" murmushi Mom tayi tace “ai kedin ce da hayyata kimbi kin damesa yaushe zai dawo naji yace saura wata biyu ya samu hutu ya dawo gida" tsallen murna ta kamayi tace “na kusa na kwanta a jikin Baffa'am dina me dadi Allah duk duniya banga Wanda yafi Baffa'am dina iya rarrashina ba sai Ya Kareem da yake kwatantawa......"
Fuzgarta yayi yace “kin cika surutun banza Amina to shidin muharraminki ne da zakike kwanciya a jikinsa dan wauta idan kinyi a baya yanzu shima yasan kin wucce wannan shirmen dubeki fah mace daya da rabi haba wannan ai shirme ne" murguda masa baki tayi tace “eh dai dan baqin....." Bugu yakai mata suka zuba a guje yana cewa sai kin fadamin waye dan baqin ciki yarinya itakuma tanayi masa gwalo da haka har bangaren Mai Martaba tana shiga ta shige bayan Mai Martaba tana dariya shima dariyar yayi ya janyota ta lafe a jikinsa yace “ya akayi ne Aminatu sarkin wasa kekam kamar ba yar soja ba" tana haki tace “ba Ya Kareem ne yakemin baqin cikin hawa cinyar Baffa'am dina ba don Mom tace saura wata biyu ya dawo" murmushi Mai Martaba yayi yace “aifa kaima ka taro March inakai Ina shiga tsakanin ya da ubanta wannan ai sai Allah" gwalo ta qarayi masa yace “to kagani fah Mai Martaba gwalo takemin" daquwa ya watsa mata yace “tayi din kaine babban kwabo ai" zama yayi shima suka fara karatun anan inda batayi daidai ba ya ranqwasheta kafin su gama duk ya tara mata gajiya ta narke tace ita bacci takeji dakansa ya rakata har qofar falon Muntaz na tsaye a harabar gdan fuska duk tayi dameji yayi qwafa ya shige dakinsa shikuma ya qarasa rakata ta shiga dakin nasu sukayi sallama.

Goma da rabi Amma babu kowa a dakin daga Amrah har Ya'isha kayanta ta cire ta daura towel ta fada wanka tayi wankanta cikin nutsuwa ta bude qofar zata fito taga duhu dakin tace “subhanallah An dauke wuta Bari na jira a kunna inj....." Mgnr qin qarasa fitowa tayi qirjinta ya doka da qarfi jin motsi a dakin cikin rawar murya tace “Am...rah.... Ya'isha yaushe kuka daw....." Nan ma kasa qarasawa tayi jin an rungumeta ta baya a razane tace “please Amrah nace miki banson wannan wasan ki daina Allah zan fadaki......" Wutar jikinta ce ta dauke jin an Sanya hannu an janye mata towel din jikinta an dora hannu saman qirjinta ta bude baki tasa ihu nandanan taji an saketa daidai lkcn da su Ya'isha suka banko qofar da sauri Amrah a lkcn ne Kuma wutar ta dawo tayi tsaye sangalgal babu komi a jikinta sai rawar baki data jiki takeyi da sauri Ya'isha ta matsa ta dauki hijjab ta zura mata suka dubeta sukace “yadai Baby meye ya

faru?" Sai Ikcn kuzarinta ya dawo ta fara dube$^2$ a dakin cikin firgici suma dube$^2$n suka fara suna tayata ta fara bankada labule itane har qarqashin gado Amma bataga kowa ba suka dubi juna Ya'isha tace “wai meye kike nema?"

A wahalce tace “mutum" kallon juna sukayi sukace “mutum Kuma?" Jinjina kai tayi sai Ikcn taji hawaye ya qwace mata tace “wanka na fito kawai naga wuta ta dauke Ina tunanin kune naji an rungumeni ta baya kafin na gama saita natsuwata aka yagemin towel shine inayin ihu naji kamar an fita da gudu Kuma sai gaku kun shigo don Allah ko kune kuka tsorata Ni?"
Numfashi suka sauke a tare Amrah tace “wlh bamu bane muma da muka shigo ihunki ne yasamu takowa da gudu wannan gdan wani banzan gdane kowa Yana bangarensa sai a saceka ma baa sani ba"
Zama tayi cikin mugun tashin hankali suma suka zauna Amrah na binta da kallo tace “kece da shekiyar gardamarki da kin bimu Aida bakiyi gamo ba Kuma ko banza kyaga gari" numfashi ta sauke tace “to waiko inada Aljanu ne?" Dariya abin yabasu Ya'isha tace “to waye ya sani ni Amrah fito Mana da qwalam dinmu mu dan lasa Amma wlh yau Shafiq ya wahalar dani shege inaga magani yaje yasha ya gaji da miyar da nakeyi masa baya qosar dani" Amrah ce ta cafe da cewa “ke yau ni kinsan sabon kamu nayi wani alhajin birni infada miki quarter million yasamin a account yace next week zai dawo" tafawa sukayi itadai tana zaune tana kallonsu suka dauko ledojin da suka shigo dasu suka baje Ya'isha tace “sauko kici rabonki" girgiza kai tayi suka miqe sukace “aikuwa baki isaba yarinya dole kici" danna mata tsiren sukayi a baki ta lumshe idonta tana taunawa suka sata a gaba suna dariya saukowa tayi tasa hannu sukaci sukayi hani'an.

Bayan sun nutsa ne Ya'isha tace “nayiwa Saleem alqawarin gobe zan taho dake yace dubu dari zaibani tukuici idan Kuma kin amince yazo gda" dagowa tayi tace “aa nidai kar yazo banason zuwansa wancan zuwan da yayi Ya Kareem kamar zai cinyeni saboda masifa har cewa yayi zai fadawa Baffa'am"
Tsaki sukaja a tare Amrah tace “ke muguwar bahuwa ce waike meye yasa bazaki waye ba koda yake dama ance sai mutum ya shekara arba'in yake wayewa badon hakaba kawai kita nuqu$^2$ da kayan dadi a jikinki saidai ki wanke kisa masa pant yayi gashi ki aske babu me mora" watsa mata harara tayi tace “ai cikar mutuncina kenan" wata dariya suka kwashe da ita sukace “sakarya ita ajiya yanzu haka mijin da kike adanawa ma yana kwance da wata zaa daura masa aure dake Kinga ta banza kikayi, tabe baki tayi tace “eh shida ubangijinsa nidai nafiso na hadu da nawa salin alin murmushi sukayi sukace ai saikitayi aikine be isheki ba duk gindin da baayi masa susa ya zama sorry rayuwar ga ta hutawa daga duniya sai Habuja aljanna tamai rabo"

Da wannan tasa rigar baccinta ta juyansu baya tayi kwanciyarta tanajin kowacce na waya da saurayinta itakam ko a jikinta washegari da wuri ta tashi tayi wanka tayi sallah ta fito ilai kuwa ta iske malamin nata a falo yana duba wani littafin addini ta isa gabansa ta zauna suka gaisa cikin larabci kamar yanda ya sabar mata ya zuba idanunsa akanta yanajin saqon daya dade yanayi masa yawo a zucci na tasowa hadda take kawo masa shikuma hankalinsa nakanta Saida ta gama ta dago taga yanda ya kafeta da ido taja numfashi tare dakai hannunta idonsa ya qifta da sakin wata babbar ajiyar zuciya ya fara Bismillah sannan ya fara yimata qari bayan ya gama biya mata suka koma Hadith suka sake gangarawa tajweed haka ya rinqa karbar haddarta mataki mataki yana sake ware injin idonsa akanta gabadaya yau kallon da yakeyi mata yasa ta kasa sakewa dashi suna gamawa ta miqe ya riqo hannunta yace “na takura miki ko?"
Qasa tayi da kanta tana wasa da yatsunta yaja numfashi ya qara rage sautin muryarsa yace “wasu fararen kyawawan furanni ne suke sauka saman shararriyar hanyar da babu komai a samanta sai wasu korayen bishiyu da suka kewayeta gefenta Kuma ruwa ne yake kwaranya ta saman wani farin dutse a gefen dutsen wata yar bukka ce irin taku ta fulanin asali tsuntsaye nata shawagi dangin su Kanari Dawisu Jimina Alhuda'huda dadai sauransu"
Gabadaya ya dauke mata hankali da Ibrn nasa jin yayi shiru ne yasata dagowa ilai kuwa idanunta ya fada cikin nasa kwarjini yayi mata irin zaman da yayi saman kilishin dole ne ka kiyayeshi yayi murmushi yace “ina tafe cikin nutsuwa Amma zuciyata matse take data isa inda wannan bukkar take wacce ta gefenta ruwa yake gudana take, Ina isa naja na tsaya saboda wata busar sarewa me kashe jijiyoyin jiki dake tashi ta cikin wannan bukka tare da wata zazzaqar murya tana rera waqe cikin harshen fullanci" sake tsagaitawa yayi ya hadiyi yawu can yaci gaba da cewa “bansan wace a ciki ba Amma zuciyata ta kwadaitu dason ganin mamallakiyar wannan murya me saukar da kasala Kuma me irin suffar matan aljanna, Aminah ba fadamin akayi ba a Raina naji koma wacece zata kasance haskenta kamar na hurul'ayn, Ina shiga kinsan wa idona ya ganemin?" Girgiza kai tayi cikin matsuwa dajin qarshen labarin ya daga hannunsa ya nunata da yatsa yace “kece Aminatuh...." Zaro ido tayi ta dafe qirji tace “ni Kuma Ya Kareem?" Matsowa yayi numfashinsu na gwamuwa yace “na'am Juhud kene na gani a dakin Kuma aka mallakamin ke matsayin matata ta sunnah tunda nake bantaba mafarkin da naji dama ban farka ba kamar wannan naso naga irin rayuwar da zamuyi da rayuwata a wannan kyakkyawan muhalli Aminatuh Wlh tallahi billahil lazi la'ilaha illahuwa Inasonki sonda bantaba yiwa kaina ba soyayya ta aure"...............

*Oum Hairan*
[7/19, 9:16 AM] Oum Hairan: *JH012 littafina na kudine idan kinsan baki siya ba don Allah kada ki karanta, bansanki ba bare na yafe miki haqqina dake kanki*

*Regular group 300  VIP 600 via bank Account  0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank  or card for This number  09013718241 only WhatsApp or vtu only for dis 09031307566*

Wata irin zabura tayi ta miqe a hargitse tana waige² kamar ance ta daga kanta sama ta hango Baffa'am dinta tseye shima ya zubanta ido fuskarsa babu alamun haske ko annuri mamaki ya cikata a tace “yaushe ya dawo?" Baita samu amsar abinda take nema ba Kareem yasha gabanta ya tsugunna yace “malaminki yana neman taimakonki Aminatu don Allah kada ki wofintar dani nasan har yanzu babu kowa cikin zuciyarki shiyasa nayi gaggawa wajen furta miki abinda Raina ya qunsa"
Sake kallon inda Rasheed yake tsaye tayi har yanzu ita yake kallo ta janye hannunta daga riqon da Kareem yayi mata ta nufi step din upstairs din da sauri zuciyarta na bugawa da qarfi kafin ta qarasa taga ya juya ya shige dakinsa ya danno qofar da qarfi daidai Ikcn ta qarasa ta shiga qwanqwasa qofar tana cewa “yau nafi kowacce ya saa Baffa'am ashe idan mutum Yana mafarki gani yakayi wayyoh dadi baffana ya dawo gareni, please budemin na kwashi tabarraki kasamin albarka My lovely Dad......"
Yana tsaye jikin qofar yanajinta qirjinsa na harbawa da qarfin dashi kansa baisan dalilinsa ba so yake ya bude mata ya kasa saboda wani tuquqi da zuciyarsa takeyi masa yayi danasanin fitowa a daidai wannan Ikcn duk da baisan meye Kareem ya fada mata ba Amma yanayinsu ya nuna wani sashine me muhimmaci sukeson wanzarwa.

Zama yayi saman gadonsa jikinsa Yana wata irin rawa a hankali ya furzar da iska me zafi yace “meye yake fada miki Meenah?" Miqewa yayi zunbur ya bude qofar har ta hqr ta juya jikinta a sanyaye abinka da me qoramar hawaye ta fara fitar da qwallah taji ya bude qofar ta juya da sauri ta nufesa a guje ya bude mata hannu me Kuma ta tuna saitayi turus a gabansa idanunsu na sarqe cikin na juna hakanan taji sautin bugun zuciyarta yana nunkuwa ta kama hannunsa ta tsugunna saita rushe da kuka abinda ya qara tashin hankalinsa yasa hannu biyu ya dagota yasa yatsansa Yana share mata hawayen har zuwa Ikcn zuciyarsa tafasa takeyi burinsa kawai yaji meye Kareem yake fada mata harta bashi attention haka data kasa jin kiransa ta kasa ganinsa?
A kasalce ya hadata da jikinsa qirjinta ya tokare nasa yaja wata ajiyar zuciya me qarfi yanajin wata nutsuwa na saukar masa yace “miss ur My Meenah" dagowa tayi hawaye nabin kuncinta tayi murmushi ta sake saqale bayansa tace “shine Saida ks batamin farin cikina Baffa'am kasan irin wahalar da nasha kafin na saba da rashinka kuwa meye yasa ka ja zuciyata a qasa harna fara tunanin ko na bataran haskena?"
Inda kalamanta suka nufa daban inda yakaisu daban janyeta yayi ya zauna a qasa itama ta zauna yace “meye Kareem yake fada miki me dadi haka da har ya dauke miki hankali kusan 30 minutes Ina tsaye akanku Amma baku sani ba?" Rufe fuskarta tayi tana dariya sokuwar tace “nifa Baffa'am bansan meye yake nufi ba wai Yana sona kuma son aure hakams Saleem yace da Ya'isha nikam bana kulasu ma cewa nakeyi suje su sami Baffa'am dina namasan bazakayimin aure ba ko........."

Wani ihu yayi daya ja hankalin mutanen dake falon qasan gabadaya ya miqe ya shaqeta jikinsa na tsuma ya kasa mgn sai wani turiri da bakinsa yakeyi haqoransa suna haduwa da gudu Mom ta nufo saman ta riqeshi tana cewa “na shiga uku ni Aishatu Abdulrasheed meye Kuma yarinyar nan tayi maka daga dawowarka ko hutawa bakayi ba...." Da ihu yace “So Momy sonta fah yace yanayi Kuma har take iya fadamin wai yanasonta Nawa take Mom irin riqon amanar taku kenan har damar soyayya kuka bata injiwa? Waye yabaku wannan damar?" Daqyar suka bambare Juhud daga hannunsa yayi watsi da ita baijira cewar kowa ba ya fada dakinsa ya doko qofar da qarfi hada kansa da bango duk wata qofa ta gashi a jikinsa ta miqe idanunsa ya kada yayi jawur zuciyarsa kuwa kamar ta faso qirjinsa haka yakeji.

Mom ce ta dagota idanunta gabadaya sunyo waje saboda ba shaqar cigaba da rayuwa yayi mata ba so yayi ya aikata lahira sauka sukayi Addah Abulle ta karbeta hannun Mom tajata dakinta ta zaunar da ita Ya'isha ta matso tace “kay yau Ina ganin masifa towaishi Big Cele meye yake nufi dan ance anasonki ya nemi aikaki barzahu?" Iska Addah Abulle ta furzar tace “Lamarin Rasheed wuyar sha'ani garesa ni yaran nan sun fara gwaramin kai wlh yanzun Kareem ya fita harda hawayensa wai in taimakeshi ta yarda tanasonsa kafin ya tafi karatu ayi komai a gama a hada aurensu da Rasheed sai tayi karatunta acan shine nace yaje ya samu Mai Martaba ya fada masa shikuma wannan kurman yazo Yana neman kasheta kawai don ance anasonta ko ubanme yake nufi oho"
Shiruce ta ratsa na dan lkc Amrah ta miqe tace “Allah ya kyauta saiki tashi kisa uniform dinki mu fita ai" tunda suka shigo tana kwance jikin Addah tana aikin kuka daqyar Addah ta rarrasheta ta miqe tasa uniform din suka fita driver yajasu suka tafi mkrnta duk abinda akeyi akan idon Muntaz yayi qwafa ya fito ya shiga cikin gidan sukayi clear da Kareem suka harari juna kowa ya wucce.

Tunda suka fito har sukaje mkrntar kuka takeyi har suka isa kai tsaye office din principal suka nufa suka gaisheta tare da gabatar mata da Aminah Haroona Moddibo a matsayin sabuwar dalibar da aka dade dayi mata bayaninta, tambayoyi tayi mata ta bata Amsa duk da batada nutsuwa Madam Khairat ta Yaba da qwazon yarinyar a mstsayinta na wacce batayi karatu ba. Bayan ta gama mata Interview din tabasu izinin su tafi domin Mai Martaba yace kada a raba masa yaya abarsu tare, hakance ta faru har aka tashi batada walwala, Muntaz ne yazo daukarsu baiga fuska a gurinta ba dole yasha jinin jikinsa maimakon ya tafi dasu gda wani park yakaisu waisu huta tukunna kafin lkcn islamiyya, Ya'isha da Amrah suka tafi harkokinsu itakuma ta nemi guri ta zauna har yanzu idan ta tuna ta batawa Baffa'am dinta rai sai taji hawaye ya zubo mata.
Ji tayi an kama hannunta ta dago tana sauke ajiyar zuciya ganin Muntaz da wani fure a

hannunsa yasata zubansa ido ya miqo mata yace “yau ranar masoya ce ta duniya shiyasa na zabeta matsayin ranar da zan fara fayyace miki sirrin zuciyata, kafin hakan ki karbi wannan furen ki shaqi qamshinsa nasan zaiyi miki dadi" hannu tasa ta karbi furen tayi jifa dashi tace “na shiga ukuna ni Aminatuh don Allah Ya Muntaz kar kace kanasona wlh Baffa'am kasheni zaiyi dazun saboda Ya Kareem yace yanasona daqyar aka kwaceni a hannunsa...." Batayi aune ba taji ya banqarata baya ya hade bakinsa da nata numfashinta ya dauke ta rintse idanunta ta hada qarfinta ta tureshi daqyar  ta miqe tana rarraba idanu yayi murmushi Yana shafa sumarsa yace “nop Ni ba irin baqauyiyar soyayyar nan zamuyi ba sai kinso kosu Ya'isha zasusan halin da muke ciki kawai zan baki damane mu rinqa ware guri muna haduwa har zuwa lkcn da Mai Martaba zaibamu damar yin aure Kinga saimu bayyana kanmu matsayin masoya lkcn babu abinda Big Cele ya isa yayi, to waima da kike wani tsoronsa shidin ubanki ne naga shima aure yake Shirin yi kekuma saiya hanaki jin dadinki akan me?"

Da sauri ya fice fit daga falon yabarsu zaune da sanyin jiki itakam Meenah gabadaya kalamansa tsinka mata jijiyoyin jikinta sukayi ta kasa koda miqa wuyanta miqewa Amrah tayi tana taunar dabino tace “aikin banza Harbin daurarre dama tunda an cinye maka zuciya Ina zakaga laifinta baqar munafuka wlh bantaba tsanarta irin wannan lkcn ba" daquwa Mai Martaba ya watsa mata yace “dake da tsanar na hada na dakaku a turmi naci kan uwarku ja'ira me qirar yar tsana" sumsum tabar gurin tana haarar Meenah Mom ce tace da ita Aminatuh tashi ki shiga ciki ki kwanta naga kamar sanyi kikeji ko?" Miqewa tayi ta nufi sashin Mom ta bude ta shiga ta ishe Ya'isha na guga ta karba tana tayata suna hirarsu itadai qarfin hali kawai takeyi da taji ma bazata iyaba sake mata gugarta tayi ta koma ta kwanta nandanan zazzabi ya rufeta wasa kamar wasa Abu ya rinqa qarfi hardai a qarshe Saida aka Kira likita ya daura mata ruwa da magunguna.

Kwananta biyu tanajin jiki sannan taji dama sabon laulayi yasata a gaba batada aiki sai cin gurji shi dayane abincinta aikuwa nandanan ta zuqe kowa yazo ya dubata a gidan Amma Banda Aliya da Nana matan yayyen mijinta itakam Addah cewa tayi haqqin dantane da tun ranar daya zabgawa Amrah Mari yake kwance ciwon zuciyarsa ya tashi yanata Aman jini duk ya fice daga hayyaci sunan matar yayan nasa kawai yake kira a qarshe dai dole Mai Martaba ya daukeshi yabar qasar dashi.
Itakam tama manta da babinsa ta kanta takeyi da lfyrta gabadaya ta zuqe ta rame saboda tsangwamar da take fuskanta a gidan batada wani sauqi a gidan saina bangaren surukarta da

kullum take rarrashinta da bata baki shikam Rasheed baisan meye akeyi ba kasancewar daga Dalta Enugu aka turasa wayarsa ma ba samuwa takeyi sosai ba a haka dai har bikinsu Ya'isha ya qaraso aka shiga hidimar biki ka'in da na'in dake bikin yazo mata a wani yanayi batama fiye shiga mutane ba warin jikinsu amai yake sanyata.

Ana jibi daurin auren yan uwan Mom sukazo daga Mali ranar Juhud yini tayi a daka Babu lau tana kwance taji an shigo part din batada qarfin miqewa ma shiyasa ta sake bin katifa ta lafe ya bude dakin ya shigo cikin dokin ganinta da shauqi ya tsaya jikin qofar dakin yace “Uhmmm qaddarar so! Kenake so!! So habo ya zabaran yayi naso!!! Yadda nakeyin nazarin so habone!! Ni inajinsa arai tuntubene!!! Dan Adam shikuwa Mai kuskurene!!! Afuwa ki agaran nayi zaune!!! Ban iyawa da rabon qaddarar so!!!!!
Wani tsalle tayi ta saki ihun murna ta rungumeshi tana kissing dinsa ta ko Ina shima kissing dinta yakeyi suka zube a gurin ta hade bakinsu cike da shauqin qaunarsa sun jima a haka ta janye ta shafa kansa zuwa qirjinsa tace “miss ur My life...." Miqewa tayi da sauri hawaye suka zubo mata ya miqe ya riqota yasa harshensa ya lashe hawayen yace “ina tsananin buqatar matata wlh nasha wahala a wata ukun bantaba gwadawa ba......" Hannun takai ta shafo mararsa zuwa qasa ta dago tayi masa murmushi tace “burina kenan Abba Aanam ya kasance me kiyaye kansa hakan shine farin cikina" harararta yayi ya riqe kunnenta yace “bakijin tausayin babynki?" Tasan meye yake nufi ta riqe hannunsa tace “asalin tausayi ma kuwa duk da ajiyarta ya hanani sakat Amma zan bata kulawa bakin gwargwado da haka ta samu ya tashi ta hadamai ruwan wanka yaqi Wai saidai tayi masa batason qamshin sabulum hakanan ta daure ta tayashi suna gamawa ya kulle dakin ya janyota jikinsa ya fara lalubeta ta sakensa jiki sosai sukayi qara'in watanni sun gurji juna kuwa son ransu ita kanta ta yarda sunyi missing junansu bayan komai ya nutsa ne ya dubeta itama shi take kallo ya lumshe ido yace “da kewarki da qaunarki zan mutu Meenah kowanne motsina kene na yarda so Yana canza mutum wlh tunda na tafi naji bana sha'awar kowacce mace bayan ke ko nayi qoqarin nema idan na tuna dake sai naji na qoshi nake nakeson ci.........

*JH013 littafina na kudine idan kinsan baki siya ba don Allah kada ki karanta, bansanki ba bare na yafe miki haqqina dake kanki*

*Regular group 300 VIP 600 via bank Account 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank or card for This number 09013718241 only WhatsApp or vtu only for dis 09031307566*
*Ga yan Niger da suke son wannan littafi basusan ya zasuyi ba ga number da zasu tuntuba 94775574 zasu tura katinsu daidai da kudin littafin sai suyimin mgn na gde*

*Oum Hairan*
[8/1, 8:43 PM] Oum Hairan: *0025* Sake shigewa tayi jikinsa tana sunsunar qamshin turarensa cikin wata murya me kashe jiki tace “inasonka My world" matseta yayi Yana shafa cikinta na watanni hudu yace “inasonki fiye da yanda nakeson komai a duniyata ki zama amanata tawa Ni kadai kinji" murmushi tayi masa ya sake mirginawa kanta ta lumshe ido ya dora bakinsa saman idanun nata Yana lasar eyeslashers dinta tare da matse nononta a qirjinsa yana matsata yanda yaga dama wannan Rana an kurbi zumar qauna yanda ya kamata.
Sunaji ana buga musu qofar sukayi likimo abinsu fir ya hanata fita wai yau Ikcnsa ne bazaa yimasa ojoro ba hatta abinci Saida dare ya fita yaje ya siyo musu ya dawo suka qara bajewa suna tsinkar furensu da dare aka kwanta akaci gaba da bawa qauna haqqinta tun Juhud na jurewa har ta fara gajiyawa abinka dame yaron ciki shikuma dadinta ya hanashi qyaleta, da safe Mom da kanta tayo tattaki tazo barayin nasu domin babu wanda yasan ya dawo sai Muntaz daya daukoshi a airport.
Ta jima tana bugu daqyar ya saki Juhud daya maqale ya fito parlourn yana tambayar waye? Jin muryarsa yasa Mom cewa ”haba nidai naji shirun tayi yawa Rasheedu ashe ka dawo?" Bude mata qofar yayi ya kwantar da kansa a kafadarta wannan tsohuwar al'adarsu ce yace “wlh tun jiya da yamma na dawo" murmushi tayi tace “babu Kuma ko nemanmu saima hanamin yata fitowa anata hada² a cikin gida tun jiya wayarta a kashe" sosa qeyarsa yayi ya zauna Ikcn da Juhud din take fitowa ganin mom yasa taji kamar ta nutse ta rusuna a kunyace ta gaisheta tayi dariya tace “yar jaka ba ko sisi waike dadi miji mijinki ya dawo kin manta dani ko zai tafi yabarni dake ai muga qaryar rashin kunya"

Dariya sukayi dukkansu Ya'isha da Amrah suka shigo da Khadija da Zahrah matar da zaa aurawa Kareem Ya'isha ce kawai ta kalli Juhud tace “ai dama Saida na kawo haka a Raina nace duk yanda akayi Babban ogane ya dawo kika manta damu" murmushi tayi tace “yo mi zanyi muku duniyata ta dawo gareni" dukkansu kallonta sukayi ta matsa jikinsa Ikcn da Mom take fita tana cewa “aifa baki ya bude da alamun shima unborn din babansa yake buqata naga yau jiki ya wartsake  ya samu abinda yakeso"
Gaisheshi sukayi ya Amsa hankalinsa nakan Meenah ya miqa mata hannu ta kama ya dagota jikinsa ya zaunar da ita suka kalli juna Ya'isha tace “baba Aminu ne yace mu kawo maka Aunty Khadija ku gaisa Wai kun dade baku hadu ba" shafa qirjinsa yayi yace “wlh fah tun rasuwar mijinki halan kin gama idda ne?" Wani farr tayi da idanu tace “kayyy soja ai tun Ikcn mutuwar Aunty Zulaihat ma nayi iddah" tabe baki yayi yace “ok to ai saiki fidda miji kiyi aure kada kice zakici gaba da shashancin da kika rinqayi a baya yaja miki aure da qananun shekaru" murmushi

tayi tace “ai nama fitar Yaya Soja" bai bawa hirar muhimmaci ba ya kalli Zahrah yace “wannan itace dayar amaryan ance amaren ukune halan ya jikin Kareem din hope Yana samun sauqi?" Tabe baki Amrah tayi tana wani yatsina tace “to bama dolenshi ya warke ba wannan auren gayya da zaayi masa da yar asali me cikakkiyar nasaba" kallonta yayi batare daya fahimci meye takeso tace ba ya miqe yace “Life help me breakfast kin yasheni jiya fah" Saida taso ta nutse dan kunyar qannen mijin nata hakana ta miqe Khadija na harararta ta nufi kitchen cikin yan mintuna ta sama masa abinda zaici ta dauka ta nufi dakinsa ta aje masa zata fita ya riqota yace saurin na meyene?"

Zama tayi tana hada masa tea din tana cewa “mom tace idan na gama naje mu gaisa da baqin Mali sunzo tun jiya sunata buga sashin nan ka Hana a budensu" yasan da hakan shiyasa baice komai ba ya rinqa janta da hira Saida ya gama yayi wanka sannan suka fito tare sunsha kyau na ban mamaki suna fitowa da ango Kareem suka fara kicibis sukayi musabaha ya tambayesa aiki shikuma ya tambayesa jiki itadai gaba tayi saboda zuwa lkcn wani haushin Kareem din takeji yanda yake nacin kallonta.
Ta rigashi shiga tana shiga parlourn Hajiya Bilki da su Nana da sauran mutanen suka fara watsewa ta tsaya sake da baki kawai sai tajiyo a bayanta wata mata na cewa “ai wannan kina ganinta kyaun dan maciji baqar annoba kenan yanzu kina cika wargi zaki tsinci kanki a Ramin kabari ta tsotse bargo ta lashe kurwa"
Juyawa tayi ta zubawa me mgnr ido hawaye wani nabin wani shiyasa jiya taqi fitowa saboda gudun abinda zatayi gamo dashi a wannan taron bikin, ji tayi an saqalo qugunta taja ajiyar zuciya tare da share hawayenta da gefen  mayafinta ya zagayo gabanta yace “dame Kuma kika gamu daga fitowarki" murmushi tayi tayi gaba ya riqo hannunta yace “wlh bazaki shigaba saikin fadamin uban waye ya tabaki?" Tana Shirin mgn Ya'isha tace “wato Ya Rasheed yau zaayi kutmar uba a gidannan....." Fuuuuuu tayi gaba tana zuwa ta dauke Hajiya Bilki da Mari ta kama qunduma mata ashar abinka da bakatsina yau jini ya motsa bala'i takeyi tana dara nandanan gurin ya kacame taron biki ya koma taron fada shidai Rasheed baisan meye yake faruwa ba Saida yaji tana cewa “aikin banza aikin wofi har wasu kune zaku dubi Meenah ku rinqa jifanta da miyagun kalamai dama ai na dade Ina jiran damar cin bura uban kowannen shege a gdannan idan kuna taqamar ance muku itan mayya ce to ai gara ita ansan wacece ita ku waye yasan asalinku yayan bayi kawai Wanda tsiya da munafurci ta Haifa ta goya ta shayar Bilki kibi a sannu halwa ce dake gaba da baya Kuma mata ba maza ba aure Big Cele yace bayaso bazai auro irin masifa irin jaraba ba wlh dadai auren halwarki gara auren mayyah so million indai msita irinta Meenah ce Kuma Meenah ta zame muku ciwon ido a gdannan kowanne dan iska saidai yaganta yabarta idan da meja Kuma yaja shima ya wullah barzahu kamar yanda Zulaihat data dage saita shiga tsakanin rabo ta fece, yan iskan banza munafukan wofi"

Tunda yaji dalilin rikicin jikinsa ke tsuma ran maza ya baci idanunsa suka kada sukayi jawur ya dubi Juhud data durqushe a qasa taketa aikin kuka me cin zuciya ya juya ya dubi mutanen kowa jikinsa ya hau karkari baice komai ba baiwa kowa mgn ba ya figi hannunta da qarfi suka fice daga falon gurin Mom din da baajeba kenan ya mayar da ita sashinsu ya kulle ya zauna yanata huci ya miqe ya zauna yafi sau ashirin sannan Kiran Mai Martaba ya shigo yayi jifa da wayar ta tarwatse ya tashi ya shiga dakinsa batasan me yayi ba ya fito dauke da jakankuna manya guda biyu ya fice ya jefa a mota daidai Ikcn da yake Sanya kayan a mota Mai Martaba ya iso gurin yace “ya subhanallah meye Kuma hakan Ina zaka?" Juyowa yayi idanunsa sun kada sunyi jawur ya dubeshi ya kawar dakai Alh Aminu ne ya matso shima Ikcn Rasheed din ya koma cikin gdan ya figo hannun Meenah ko dankwali Babu akanta Mai Martaba daya fahimci barin gidan yake niyyar yi yace “wai ba mgn nakeyi maka bane" a fusace ya juyo yace “banaji Mai Martaba banji abinda kaceba ka kauce kabani guri yau kam ko baku koreni ba na gama zaman gdan sarautar nan akan matata zan iya hqr da komai....."
Muryarsa ce ta sarqe ya jefata a mota ya kulle har yanzu kuka takeyi yama kasa rarrashinta ya sake kallon Alh Aminu ya nunasa da yatsa yace “ka sanar da munafukar matarka ni Abdulrasheed nafi qarfin yayanta a aure  kun bani Zulaihat banaso na karba Allah ya dubeni ya kasheta kun bani Hidaya na sakar muku kayarku shine yanzu zaku liqamin bazawara kwancen wasu saboda kun Mai dani jani talau waima ni kadaine da namiji ne a gidannan Ina Salman Ina Arman Ina Kareem Ina Muntaz hatta Urwat kukayiwa aure zama zaiyi da matarsa saini akanme zaku sanyawa rayuwata idanu ne banaso na fada muku banaso wlh tallahi zanci mutumcin duk ubanda ya qara tunkarata da mgnr aure auren banza auren wofi da har zaku sanyawa matata tsura akansa aiba ita ta hanani ba nine naga batada tamka bare mahadi, Abu na qarshe ka fadawa Bilki ta kiyayi dawowata gdannan Kuma ta shirya Amsa Kira kotu saita fadamin uban wa matata ta kashe da take fadawa duniya cewa in mutum ya cika rabar Meenah saidai yajishi a Ramin kabari?....."

Sosai Mai Martaba ya girgiza da yanayin Rasheed din yasan tabbas yau yakai qarshe akwai gagarumar matsala idan yabarshi yabar gidan dama Meenah ce zatake kawoshi tunda shi dama asalinsa bayada ra'ayin zaman gdan sarautar to ya dauke abarsa meye Kuma zaisa suganshi? Mai martaba na Shirin mgn Mom ta iso gurin ita da wasu mata su uku dole tasashi yin shiru ta kama hannun Rasheed tajashi gefe sun jima suna bugawa kafin ta shawo kan kayanta Yana kuka kamar wani yaron goye daqyar ta lallabashi ya yarda zaibar Meenah a gidan sarautar Amma da angama biki da ita zai tafi.
Zuwa tayi ta fito da ita a mota ta janye mata sumar data rufe mata fuska tana ganin Mom din ta fada jikinta ta sake rushewa da kuka itama hawaye ta share tana tausayawa rayuwar Meenah Babu uwa Babu uba babu shaqiqin dan'uwan da zata zanta dashi taji dadi ga rayuwar taqi mata dadi wata murya taji ta bayansu tace “kiyi hqr Aminatuh komai yayi tsanani sauqi na zuwa hakanan Allah yake jarabta bayinsa zababbu domin ya gwada imaninsu ba sonki ne bayayi ba qaunace ta kawo miki hakan bantaba ganin Wanda akayiwa irin wannan qazafin ya qare rayuwa

a wulaqance ba ko baizama wani ba zai samu yardar Allah"
Juyawa tayi ta zubawa matar idanu gabanta ya yanke yabada wani rass ta janye jikin Mom da sauri tana qara kallon matar tare da langwabar dakai a rayuwarta nata taba ganin kamar tsagin Kara irin wannan ba kama haske da jiki inda kasan innatun ta a hankali ta sauke ajiyar zuciya tace “mom wannan fah?"

Dadine ya cika mom ganin ta fara warewa tace “Wannan Kharimatu kenan qanwata ce babanmu daya daga Mali suke ita da Mamanta Hamida kinganta can" juyawa tayi ta kalli dattijuwar matar da tayi tsufan jin dadi fatar nan kamar a matsa a tatsi jini tana sanye ds farin tabarau tayi mata murmushi ta bude mata hannu ta fada jikin matar hakanan takejin wata nutsuwa na ratsata da kwanciya a jikin Kumbo Hami Kumbo Hami ta shafa kanta tace “kiyi hqr jikata zakiga ribatai a gaba munci wannan baqin cikin nida babbar yata Aysho tana jaririya a tsumman goyo aka koremu daga gdan babansu Aishatu surukarki......" Kuka ne ya qwacewa Kumbo Hami ta share qwallarta tace “saboda qin jini da yanayin qabila wannan abu yake bibiyarmu kamar garin Bodde wani babban garine da yake cikin Qasar Mali So garin yazamo kamar Biddah a Nigeria sunyi qaurin sunan asiri da maita Wanda ba dukkan garinne suke da wannan hali ba su masu yinma sune kaso mafi qanqanta.
Baffana attajiri ne a garinmu a zahiri bama maita bama tsafi Amma saboda dukiyarsa yasa ake cewa shine shugaban mayun garinmu  Baffa Garbu wato babansu Aishatu surukarki yaron babana ne hakan yasa yabashi aurena tunda nazo garin Ikcn baa auro uwayen su Aishatu ba matan gidan suka tsangwamin Kuma Allah dabawa mugu dama haka akayita rashe rashe a gabar tun baa yarda har suka amince da gaske ni mayyace hakanan na haifi Aysho ranar dana haifeta Garbu bayanan uwarsa tasa aka daukemu akaje bayan gari aka yasar damu daqyar na iya komawa Mali daga Senegal naci gaba da rainon Aysho Garbu nasona Amma bashida ikon dawo dani domin babana ya fusata hakan yasa Aysho nada shekara goma ya karbeta a gurina sai labari naji ya auradda ita ga dan qanwarsa ya taho da ita Nigeria tun daga wannan Rana nakebi akaini inganta nakasa samun dama dakaina nazo Nigeria neman Ayshatu na ban dace ba a qarshe dai nama hqr domin jikina na bani Ayshatu bata raye don da tana raye inni ban nemeta ba ita zata nemeni, bayan na rasa Ayshatu ne qulafucina da son naganta yasa na komawa Alh Garbu shine har na sake haihuwar Kharimatu, Aminatuh yanzun komai ya wucce bayan ansha wuya kema idan kikayi hqr watarana zai wucce"...........

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane kada ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/2, 6:36 PM] Oum Hairan: *0026* Jinjina kai Juhud  takeyi da jin wannan rikitaccen al'amari tabbas duniya ta cika da mutane marasa tsoron Allah saidai kayi fatan Allah ya dada maka Imani kawai, dubanta Mom tayi tace “Kumbo Hami itace ta riqeni tun bayan rasuwar mahaifiyata banida uwar data fita a duniya Meenah" sosai Meenah taji dadi da ganin dangin surukar tata hakanan taji tanayi musu wata qauna me game jini suma sosai suke nuna mata qauna da kulawa sun jima sosai a sashin nata sunata hirarsu gabadaya su anan suka qarashe bikinsu basajin Hausa sosai hatta Rasheed fullanci yakeyi musu wannan tasa Juhud sajewa dasu. Kwana uku aka dauka ana bikin qofar falo Rasheed hana Juhud zuwa yayi da sunan biki to itama bata matsa ba ganin Mom ta goya masa baya a gdanta tayi nata bikin saidai tasa ta cire kawai idan yaga garara mutane sunwa bangaren sauqi yasata a corner yayita hadanta aiki ta rasa a wanne bigire zata aje Rasheed irin mazan nan ne masu jarabar nacin masifa shi indai zaki dagansa qafa to bakida matsala dashi idan har kaga Yana ciccin mazu to ya nema anyi masa rowa ne.
Tunda ta fahimci haka itakuma taci alwashin kozata wahala indai ya nemi haqqinsa zata bashi domin shima Babu ta inda ya tauyeta ya tsarenta mutumcinta fiye da yanda ma ya tsare nasa, ranar da biki ya watse aka kai amare gdajensu washegari su Kumbo Hami suka shirya tafiya Juhud har tafi Mom shiga damuwa da tafiyar tasu da anyi mata mgn sai hawaye Ikcn da taga sun kusan gama shiryawa sulalewa tayi tabar gidan ta koma sashinta tasa Rasheed a gaba da kuka wai ita bataso su tafi.

Murmushi yayi ya shafa kanta yace “ke har yanzu yarinya ce Meenah to yanzu Kuma kawai saboda bakison su tafi sai su zauna? Kiyi hqr idan kika haihu zan dauki dogon hutu zan kaiki garinsu nima rabona da Mali nafi shekara ashirin" da haka ya samu ta sake har sun shiga mota Kumbo Hami ta fito ta kama hannunta hakanan takejin yarinyar a jininta tace “kici gaba da hqr mijinki Yana sonki Ni shaida ce Meenah idan Allah yasa watan hsihuwarki ya kama da rai da rayuwa zan dawo ni zanyi miki biqi kinji jikata" dariya tayi itama tayi dariya suka tafi suna dagawa juna hannu tana kwance bisa kafadar mijinta.
Taso rakasu airport fir yaqi saboda yasan idan taga tashinsu tsaf zata rikice masa, suna komawa kuwa ya fara hadansu kaya ta dubesa tace “yada hada kaya?" Dubanta yayi yaja numfashi yace “tafiya muma zamuyi" komawa tayi ta kwanta yaci gaba da aikinsa bayan ya

gama yazo shima ya kwanta sukaci gaba da soyayyarsu sai biyar na yamma sannan sukabar gidan Muntaz ne yakaisu airport suka daga zuwa Enugu.
Sun sauka da dare suka samu motar taxi takaisu masauki suna zuwa ta kwanta zazzabi ya rufeta Saida ta kwana uku tana kwance yana jinyarta har ta samu ta samu sauqi sukaci gaba da rayuwarsu gwanin dadi.

Aikam tana ganin qauna da soyayya ririta cikin nan yakeyi kamar me, Ikc ya rinqa turawa cikin nata Yana qara girma komai yanayi mata wuya shine yake yi mata komai kafin ya fita hatta abinci daya barta ta girka gara yaje ya siyo musu, October watan haihuwarta ya kama tsakiyarsa suka dungumo suka dawo Daura kwanansu uku kuwa da dawowa Kumbo Hami ta dira a Daura sunyi murna sosai sunata farin ciki kwanansu uku ya tafi ranar daya tafi kuwa cikin dare ciwon naqudar na gaske ya tashi.
Wayyoh anci wuya matuqa kwana tayi ta wuni tana naquda har Saida suka yanke shawarar ayi mata aiki sun gama komai sun shiga da ita ubangiji ya kawo mata sauqi cikin taimakon Allah ta sunkuto qaton danta namiji wayyoh farin ciki gurin Mom da Mai Martaba da Ya'isha hatta Muntaz yayi murna da wannan haihuwa kwananta daya a asibitin aka sallameta suka dawo gda Kumbo Hami na kulawa da ita shikam gogan saboda farin ciki har kuka yayi gashi bayada damar dawowa bama ya qasar Yana sauka aka turashi Africa ta kudu.

Ba Shiba ita kanta taso ace yana kusa yaga dansa yasa masa albarka hakanan dai akaci gaba da hidindumun haihuwar wani abin mamaki babu wani daga bangaren Addah Abulle daya leqo barkar wannan haihuwa lamarin ya bawa kowa mamaki itako Meenah batasa a ranta ba balle abin ya dameta domin ba iyakar su kadai bane duk Wanda ke gdan sarautar Babu Wanda ya leqo musu barka tasan saboda itane Kuma tariga tayi forget na komai dazai sanyata damuwa dane dai ta haifi abinta Kuma ubansa da shaqiqan danginsa suna murna da zuwansa duniya.
Duk wani gata da maijego yar gata take samu Meenah ta samu samansa Babu abinda zatacewa surukarta da Mai Martaba sai gdy domin shima ya taka rawar gani gaya a wannan haihuwa, duk abinda uba yakeyi shine ya dauki nauyi donma komai na buqata Rasheed ya tanadi abinsa sai dan abinda baa rasa ba Kuma ya zuba mata kudi masu kauri a account dinta ko zata buqaci wani abu.
Ranar kwanaki uku ne suna zaune da Mom da Ya'isha da Aunty Hamida a falo Juhud na feeding din babynta ya kafeta da ido qurr yana qare mata kallo suna dariya Kumbo Hami tana cewa “wannan ja'irin yaron quiya zaiyi tun yanzun Yana qarewa uwarshi kallo da shegen wayonsa aka haifesa" itadai saidai tayi dariya kawai.
Sallama akayi a bakin qofar suka daga kai suka kalli me shigowar Hajiya Bilki ce ta shigo ita da Dada Hanne babbar yayarsu Mai Martaba Mom ta taresu fuska a washe tana musu sannu da zuwa ta basu gurin zama Dada Hanne ta tabe baki tace “ashe an haihu?" Da yanayin rashin jin

dadin tambayar  Mom tace “eh wlh yau kwana uku" tabe baki sukayi Dada Hanne tace “eh tun ranar aka fadamin shine dai yau na daure nace Bari nazo Ke Bilki bani ruwan qanzon nan" dukkansu kallonta sukayi ta miqa hannu ta dauki yaron a cinyar Juhud tana harararta kawai ta bude bakin yaron ta dauki ruwan zata dura masa Meenah ta miqe da sauri tayi kukan kura ta warce danta Dada Hanne ta kuwa dauketa da mari tace “kutmar ubancen ke dan uwarki ni zaki qwacewa yaro a hannu koda yake ba banza ba dama anfada ance indai da abar a jikinki bazaki Bari a karyawa danki ba gashi kuwa munga alama to wlh baki Isa ki bata Mana zuri'a ba dolene abawa yaron nan ruwan qanzon nan Kuma daga yau an daina bashi wannan baqin nonon na tsiya a nema masa Madara ko abawa Fadila ta shayar dashi shidai Rasheedun da kwadayin farar fata da kyauwun banza yakaishi ya dauko to ta qare masa akansa...."

Tana qoqarin fusgar jaririn Juhud ta qara qanqame abinta ta saki wani kuka me sauti tace “wlh bazaku kashemin daba duk abinda zakuyi saidai kuyi....." Mom ce ta karbe da cewa “Dada Ina ganin mutumcinki ki fita daga lamarin halwata kafin na hada dake na tsince muku zarafi yaran nan daga ita har mijinta basu damu da lamarin kowa ba ku kun damu dasu to waima Ina ruwanku da abinda ta Haifa ne ince dai nasu ne su suka Samar da abinsu ke yanzu bakiji kunya ba gotai gotai dake kizo kina yada girma gaban jikarki"
Hayayyaqo mata Dada Hanne tayi tana cewa eh dama Mana dole kice haka Aisha ai kinci kin qoshi mun kaiki matsayin da baki takaba a baya to dake da Mahfuz da Rasheedu da duk wani Wanda yake yaruwa a gidannan a qarqashin darajata yake balle wannan yar galaulawar da kuka kwaso kuka manna Mana saboda haka wlh muddin Ina raye Kuma Rasheedu daga tsatson sarki Waziri ya fito to dole ne a bani dannan mu karya masa maita takanas nayi tattaki har Kankia na karbo wannan maganin don tseratar da ahllinmu daga gurbacewa irin maita ai bala'i ne bazamu sake a lalata Mana halwa da son zuciya ba" Hajiya Bilki ce ta cafe da cewa “yo Dada Hanne da kike wannan mgnr jinki zasuyi ne ko zaa barsu su gane me kike nufi da gatan da kikeson yi musu ne ai anriga an lashe kurwas basuda katabus hatta Mai Martaban bashi da fuss indai akan wannan tsintacciyar magen ala qaqai dince kina gani fah saboda a samu a ceto yaron nan nabawa Alh Aminu shawarar yafadawa Mai Martaba tunda yaqi Hidaya ga Dijenan babu makusa in batafi ba bazaa fita ba ya aurawa Rasheed Amma yaron nan ya debemin albarka ta sama data qasa har Yana cewa indai halwata ce to har abada bayaso......"

Fashewa tayi da kukan munafurci nandanan Mom ta zuciya Mom akwai hqr da kawaici Amma tanada mugun zafi idan aka kaita qarshe ta miqe tace “Hanne ku fice daga bangaren nan tunda baa ginashi da sunan dayanku ba da sunan Dana Abdulrasheed aka ginashi Kuma iyalinsa ne a ciki munji ko Meenah zata rinqa sakatarmu da daidai munasonta a haka tunda danmu yanaso munafiki ya ciji yatsa maqi gani ya rintse ido insha Allahu Meenah saita haifi sarkin gobe a gdannan muga shegen daya Isa ya Hana Allah ikonsa magani ne bamaso mun gode bazaa

bawa yaron nan ba indai ta jikin dana ya fita muga Wanda ya isa ya gwada ikonsa a gidannan" Tana fadin haka ta karbe yaron a hannun Meenah data hada kanta da center table taketa kuka wannan cin mutumci da take jawa uwar mijinta yayi yawa itakam da tana da dama data fita daga cikinsu ko da samu salama to tunanin halin da Rasheed zai shiga shine yake takanta burki ya dauki amanar kansa da komansa yabata sun jibanci lamarinta sun yarda da kowanne irin cin mutumci indai akanta ne idan tace zata gudu tabbas batayi musu adalci ba domin ta kwaranye musu baya magautansu zasu samu damar yi musu dariya.

Kumbo Hami ce ta matsa jikinta ta riqe kafadunta tana jinjina girman halin da yarinyar take a ciki bata taba tunanin abun yayi qamarin haka ba dole yarinyar ta kasa sukuni cikin wannan ahli lamarin rashin kararsu azumin ne basa da mutumci ko kadan sosai kalamin Dada Hanne sun girgiza Kumbo Hami ta dago Juhud jikinta ta shige jikinta cikin kuka tace “don....don Allah Kumbo ki taimakeni kice da Rasheed ya hqr da zama dani tunda danginsa basa qaunata wlh zuciyata zata buga idan naci gaba da zama a cikinsu ya sukeso nayi ne da wanne zanji? Yaushe zanyi farin cikine yaushe zan samu salamar rayuwa nima kamar kowa, Allah inason mijina Amma lkc yayi da zan barsa na nemawa kaina yanci ina zangansu??"
Bubbuga bayanta Kumbo Hami takeyi cikin jimami tace “ki daina tuhumar ubangiji akan abinda bai kawo qarshensa ba Meenah meye laifin mijinki ne da zaki zabi jefashi cikin garari yanasonki baitaba kallonki da abinda wadannan debabbun ke kallonki dashi ba surukarki ta karbeki ta yarda da komai daya jibanceki kada ki bata rawarki da tsalle koda bazakiyi hqr domin Allah ba kiyi don wadannan ahlin mijinki mahaifiyarsa yan'uwansa da suka fito daki daya nasan Allah zai baki ladan saka Alkhairi da Alkhairi kada ki zama butulu rayuwar butulu bata qarshe me kyau kinji?"
Kwantar dakai tayi cikin yanayi na nadamar kalami tace “yanzu shikenan ni tawa qaddarar kenan Kumbo haka zanta rayuwa cikin tsangwama a cikin ahlin da ba nawa ba haka zan qare rayuwata ni a qunci halwata a qunci?" Murmushi tayi tace “kada ki cire tsammani daga rahamar ubangiji insha Allahu komai zaizo qarshe" da hikima irin tasu ta dattijan da sukaga jiya sukaga yau suke sa ran ganin gobe ta kwantar mata da hankali ta kwanta kanta na ciwo Aunty Hamida ta dauko Sarki junior ta kawo musu Kumbo Hami ta karbeshi ta zubawa yaron ido dan kyakkyawa dashi kamanninsa na ubansa hasken fatarsa na uwarsa.

Miqa mata shi tayi tasa masa nono ya kama Yana zuqa tana cije lebe zafi takeji sosai idan yanashan nonon hakanan take daurewa take shayar dashi bata jima da kwanciya ba bacci barawo ya dauketa cikin baccin taji ana shafa fuskarta tayi miqa tare da tallafe kan yaron ta zare masa nonon a bakinsa ta daga kai ta sauke idanunta da suka kumbura sukayi luhu² a kansa shima ita yake kallo yakai hannu ya dauki Mahfuz ya zubawa yaron ido yanajin qaunarsa data mahaifiyarsa na nunkuwa a ransa ya sake shafa fuskarta yace.
Kin biya Aminatuh Allah yayi miki albarka ya rayani tare dake" ajiyar zuciya taja me qarfi ya

sake zubanta ido yace “naji labarin komai daya faru don Allah ki taimakeni kiyi hqr ki dainasa damuwar wadannan mutanen a ranki kinji" lumshe idonta tayi tare da lasar lips dinta daya bushe yace “talk me Mana" kallonsa tayi idanunta na tsiyayar hawaye tace “idan ya kasance nice matsalarka a duniyar nan Abdulrasheed meye yasa bazaka datseni cikin tarihinka ba ko ka samu record me kyau?" Sakin baki yayi yana kallonta ta zame daga gadon tace “don girman Allah mu hqr da zaman nan tunda mun kasa samun farin ciki a cikinsa Abdulrasheed bantaba zama silar farin cikinka ba saidai na akasinsa tunda ka janyoni ka hadani da rayuwarka taka ta gurbata ta ahlinka ta gurbace inda kai kadai ne da sauqi tunda kaine kaji ka gani Amma meye yasa saboda son ranmu da son zuciyarmu mu zamo silar yankewar farin cikin wasu Baffa'am Munjefa Mom cikin tsaka me wuya mun jefa Mai Martaba mun jefa kanmu mun jefa duk wasu masoyanmu. Please don Allah don girman Allah mu hqr kabarni na rayu da yanci kaima ka rayu da salama kaji"......

Juhud is not free read... regular 300 VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane kada ki biya 300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/3, 9:13 PM] Oum Hairan: *0027* Tunda Juhud ta durqushe gabansa ta riqe qafafunsa tana kuka tanayi masa magiyar jikinsa ke rawa ya kafeta da manyan lumsassun idanunsa ya kasa furta mata ko kalma daya da zata zama salama ga ruhinta saboda gani yake duk furucin da zauyi yayi kadan wajen goge mata radadin ciwon dake cin zuciyarta wanda harya sanyata zabar rabuwa dashi fiye da rayuwa dashi. Kwantar da kanta tayi a cinyarsa ta dora hannunta a fuskar Sarki junior ta sake rushewa da kuka tace “idan ya kasance kalaminka sun qare ni Kuma Ina kakeso nawa suje Baffa'am kaine duniyata kaima kana neman zamewa daga gareni tabbas rayuwata babu kai akwai rudani a cikinta Amma zan zabi na rayu da quncin rashinka fiye da rayuwa da haqqin wasu nikam banajin dadin yanda zamana dakai ya zamo silar rarrabuwar kawunan ahlinka Baffa'am meyesa Allah bai qadarta zamowata Alkhairi gareku ba?"
Lumshe idonsa yayi ya bude ya saukesu akanta ya miqe hannunsa dauke da dannasu yana sake shigar dashi jikinsa yace “abune da bazai taba yuwuwa ba kike furtawa Meenah shiyasa

nake ganin asarar bata Ikcna wajen baki amsa" yana fadin haka ya fice daga dakin ya nufi nasa ya zauna a gefen gado ya yaye fuskar Mahfuz yayi masa addu'ar da baisamu yayi masa ba ya kwantar dashi tare da miqewa yasawa dakin key ya cire kayansa ya shiga bathroom ya watsa ruwa ya dawo yana shiryawa yana kallon yanda yaron keta wutsil$^{2}$n dinsa na jarirai yayi murmushi a fili yace “girman rabo Ina Mai Martaba da yakeson yakaimin wannan Soldier da zai fita daga jikina ya shiga na Meenah ta qinqishemin shi? Da a Ina yakeso na saka wannan kyakkyawan qwan da bai cancanci qinqisar kowa ba saita rayuwata?" Bayan ya gama shiryawa yayi sallar Isha da baisamu yayi ba yayi shafa'i da wuturi ya haye gadon ya kwanta tare da daukan yaron ya dora a qirjinsa yanajin qaunar gudar tsokar tasa har cikin bargonsa, zubawa p.o.p idanu yayi yana nazarin kalaman Meenah tabbas lamarin yau me girma ne Meenah da bakinta ta furta masa gara rabuwa dashi akan rayuwa dashi wannan abu yanayi masa ciwo duk wata matsala ta gidansa bata zuwan musu a kankin kansu saida wasu su qirqireta idan yace zai dauki mataki a hanasa wannan wacce irin rayuwa ce ne?"

Miqewa yayi ya dauki Mahfuz daya farka a bacci yake neman uwarsa ya fita ya nufi dakinta ya bude ya shiga ga mamakinsa ya isketa zaune can qarshen gadon ta zuba uban tagumi ya zubanta ido tausayinta da qaunarsa na qara nunkuwa a zuciyarsa ya haura gadon ya kwantar da Mahfuz ya sanya hannunsa ya janye mata tagumin  ya janyota jikinsa ya rungumeta yana sunsunar sumarta yanajin wata natsuwa na kwararo masa yace “idan na rasa gatan kowa a duniya baikamata na rasa naki ba Meenah bai kamata na zamo mara galihun nunawa duniya a gurinki ba bayan kin kasance mace daya tal dake mulkin zuciyata please na roqeki ki daina jin a ranki akwai abinda zai rabamu qaddarar mutum Babu me tayashi dakonta ni kece qaddarata nima nine qaddararki bazan hanaki kuka ba akan abubuwan da suke faruwa Amma dai ki rinqaji a ranki iyakar rintsin rayuwar duniya ni nakine ke kadai Babu wani tsanani da zaisa na rabu dake saidai qaddarar mutuwa idan ta gifta saboda haka banson sakejin wadannan kalaman naki don Allah kinji?" Zamewa tayi a jikinsa ta miqa hannu ta dauki Mahfuz tayi Bismillah ta Sanya masa nonon ya kama yanasha shikuma yana aikin kallonsu.

Kwanciya tayi badon tayi bacci ba saidon tabawa zuciyarta hutu shima kwanciya yayi a bayanta ya maqaleta da haka sukayi bacci washegari da wuri ya fice daga gdan duk cika ta gidan sarautar idan ka shiga barayin Rasheed bazaka taba cewa sabuwar haihuwa akayi ba saboda yanda gdan yake a yashe  daga ita sai Kumbo Hami suketa harkokinsu Rasheed bai dawo ba sai bayan Isha lkcn har sun kwanta ya shigo  ya kirata ta miqe ta nufi dakin nasa yana safa da marwa ta samu guri ta zauna shima ya zauna a gabanta ya dubeta sosai yace “nasa anzo an kama Hajiya Bilki da Dada Hanne....." Dafe qirji tayi da sauri tace “na shiga uku Baffa'am me sukayi maka?" Share zufa yayi ya miqe yace “saboda a koya musu hankali su fita daga harkata da iyalina" yana mgnr yana hada kayansa ta miqe ta Isa gabansa jikinta na rawa ta durqushe

tace “wlh wannan abin baikai ka dauki wannan matakin ba Abban Sarki ana barin halal ko don kunya please kada kayimin haka wani bala'in zaka qara jefani a ciki kasa a sakosu wlh ni na yafe musu...."
Rufe mata baki yayi yace “ke zaki iya yafewa saboda bakisan ciwon kanki ba nikam ban yafe ba Yana fadin haka ya shige bathroom yabarta sake da baki wannan mutumin kwai dan neman jarfa anason kashe wata yana neman zunguro sama da kara

Tananan zaune ya fito daga wankan Yana tsane ruwa ta sake dubansa zatayi mgn ya nuna mata hanya yace “jeki ma hadu da safe inason zanyi yan nazarce nazarce" miqewa tayi jikinta a mace ta koma dakinta ta ishe Kumbo Hami tana sallar Isha ta zauna bayan ta idar ne take tambayarta meye yake faruwa ta kuwa zayyane mata komai tayi shiru na dan Ikc sanna ta dago tace “banji dadin kaisu qara da yayi ba shima hakan qarin wata fitinar ce daya qyalesu watarana sai Ibr"
Miqewa tayi ta Sanya Sarki junior a gadonsa tana cewa “nima abinda naso ya fahimta kenan yaqi bani hadin kai koroni ma yayi Kuma tunda yayi niyya Babu me hanashi" da wannan tayi addu'a ta kwanta sukayi baccinsu itadai da zullimi ta kwana aikam abinda take gudun ne ya faru da safe Yana fita Hidaya da Khadija sukayiwa gdan tsinke suka rinqa zaginta sunacin mutumcinta Meenah babu baki sai hawaye kawai da takeyi suna tsaka da wannan tujarar ne Kareem yazo musu barka don shi sai ranar ma yakejin Ibrn haihuwar gurin Fadila aikuwa ranar Khadija da Hidaya sunji a jikinsu domin dukan mutuwa yayi musu kamar shine sojan daqyar Mai Martaba ya qwacesu barkar da baiyi ba kenan ya fice daga gdan rashin mutuncin gdan ya fara girmewa tunaninsa ace Babu Wanda ya isa ya fada aji anbi an tsangwami yarinya akan abinda bashida tushe balle makama aikam ranar hatta Addah Abulle Saida taji kunyar irin rashin albarkar da Kareem yazo ya zazzage mata a gdan akan rashin zuwa taga Dan da aka haifawa Rasheed yan uwansa kuwa gda gda ya rinqa binsu yana ci musu mutumci Yana fada musu ai ba Meenah suke qi ba Rasheed suke qi tunda shine ya dauko Meenah Kuma yakeson kayarsa sannan ba Meenah kadai ta haifi Mahfuz ba Rasheed shine silar zuwansa duniya saboda haka shine basaso"

Basu wani dauki mgnr da muhimmaci ba ba Kuma su risuna ba sukaci gaba da dabdalarsu rikici yaqi qarewa cikin wannan family har ranar suna akayi sunan babu wani armashi kamar abin arziqi dangi suka hadu ranar Meenah Saida ta gwammace ita dama mutuwa tayi da wannan baqin cikin data riska wannan Rana a qarshe baa gama sunan da ita Ify ba sai a gadon asibiti ta qarashe sunan jininta yayi mugun hawa hawan da Rasheed bai taba tsammani ba ya shiga tashin hankali matuqa da yanayin da yaga matar tasa a ciki, da dare aka sallamesu suka dawo gda kanta na ciwo sosai da Rasheed da Mom da Kumbo Hami sunata rarrashinta da kalami na kwantar da hankali bacci ya dauketa washegari badon yaso ba ya shirya yabar garin ya koma

wajen aiki yabarsu cike da kewar juna................

_Kuyi hqr da wannan_

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏽 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane kada ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/4, 8:56 PM] Oum Hairan: *0028* Kwananta sittin da haihuwa Kumbo Hami ta koma Mali inda ita Kuma taci gaba da rainon danta cikin kulawa da tattali a hankali Ikc yaketa tafiya qaunarta da Rasheed tanata qara gaba inda aiki ya riqeshi kusan watanni biyar sannan ya waiwayosu ranar anyi qara'in rayuwa kamar bazaakai gobe ba yayi musu sati biyu ya shirya domin tafiya wani aikin hadin gwiwar qasa da qasa zuwa Togo yaso tafiya da ita Mom tace gara yaje yaga yanayin gurin tukunna inyaso sai yazo ko ya aiko tabisa.
Hakanan suka rabu bason ransu ba wani abin almara tunda ya tafi wayarsa bata shiga da farko sun dauka yanayin aiki ne tafi tafi da tafiyarsa ya dauki wata biyu babu waya babu aike, sosai hankalin Juhud yaqi kwanciya hakanan wata faduwar gaba ta aureta Mom ma tana cikin damuwar rashin jin labarin dannata  hakanan take daurewa tana kwantarwa da Meenah hankali, tafiya na qara tsayi har aka tafi wata shidda Babu waya Babu amo Babu labari. Qa'idar aikin nasu yace watanni shiddan ne gashi sun wucce nan fa Mai Martaba ya tashi takanas yaje barikinsu inda ya dawo cikin matsanancin tashin hankali suna ganinshi Meenah dake zaune ta dora kanta saman cinyar Mom tana aikin kuka ta miqe tana cewa “Mai Martaba kaganoshi Yana cikin qoshin lfy?"

Sunkuyar dakai Mai Martaba yayi yana kwance rawaninsa yace “lamarin akwai daure kai fah naje barikinsu duk sojojin da aka tura Togo sun dawo tsiraru ne suka mutu Amma shi bai dawo ba dana matsa da bincike ma a data na aikinsa tun sunada wata biyu da tafiya wani mugun ciwon kai ya sarqeshi shine dalilin da yasa aka bashi hutu da zummar zai dawo gda tsayin watannin nan bai dawo ba....."  Yanke jiki Meenah tayi ta fadi qasa sumammiya gabadaya sukayi kanta Mom ta dauko ruwa ta fara yayyafa mata daqyar ta dawo hayyacinta ta miqe zaune ta dubi Mai Martaba cikin gushewar hayyaci tace.
“Me kakeso kacemin Mai Martaba mijina ya taho gda daga filin daga Kuma baizo gidaba to Ina ya tsaya Kuma wayoyinsa basa shiga tun satin daya tafi?" Gumi Mai Martaba ya sharce yace “shine abinda nima nake tambaya kada ki tashi hankalinki na sanar da duk Wanda ya kamata na sanarwa wannan isue din Kuma sun fara bincike daga yau insha Allahu komai zaizo da sauqi...." Cikin kuka tace “ta yaya zan kwantar da hankalina bayan rayuwata tana cikin garari nikam don Allah ku fitomin da mijina wlh inason kayana"  daqyar suka samu suka lallasheta shima ba shiru tayi da kukan ba kawai surutan ta daina hakanan aka duqufa babu ji Babu gani nemansa ta kafofin sadarwa na Internet da duk wasu hanyoyi da zaa samu bayaninsa Amma shiru Babu amo Babu labarinsa.

Gabadaya hankalin gdan sarautar Babu na kwance wannan baqon alkaba'i daya fado musu Babu zato ya girgiza zuciyar kowa a gdan daga yara har manya hatta wadanda ke nuna adawarsu irinsu Hajiya Bilki a zahiri suna nuna alhininsu tare da jefar da maganganu na zargi a fakaice suna alaqanta batan nasa da Juhud da take kwance cikin halin jinya bata kwana uku da Ify saboda tashin hankalin da take ciki duk ta qare sai qasusuwa gashi kullum lkc qara tafiya yake babu wani amon labari tun daga sama ga manyan sojojin da suka baza idanunsu a kowanne lungu na Africa domin ganoshi zuwa gwamnati da itama take hobbasa wajen ganin an samo bakin zaren saidai kullum labarin daya ne baya canzawa daga inda yake.
Malamai kuwa da suke aiki da addu'ar Allah ya fito dashi sunfi dari suma kullum amsar daya ce a qara hqr lamarin daya Sanya Juhud a wani hali ga shayarwa gashi ko abincin bata iyaci dole tasa sarki yanada shekara daya da wata hudu Mom tayi masa yayen dole aka dorashi akan abinci aka qyaleta da damuwa daya gabadaya ta quntata kanta kullum bata da aiki daga sallah karatun qur'ani sai kuka

Mai Martaba da yayansa maza musamman Kareem daya dawo daga Saudia ya gama karatunsa kullum basa Kano basa Abuja basa Lagos Basu kotono Basu Togo Basu Burkinafaso tafiya kullum qara miqawa takeyi Abu ya tafi shekara guda, watarana suna falo suna zaune Meenah na rungume da Sarki junior Amrah da Fadila suka shigo suka zauna aka gaisa suka

jajantawa juna Dada Hanne dake zaune ta rafsa tagumi ta dago tana kallon Juhud tace “lamarin nan da ban mamaki Mahfuz batan Abdulrasheed kamar batan toka a ruwa gsky abinnan da lauje cikin nadi Anya ba mutuwa yaronnan yayi ba"
Duk Wanda ke falon Saida ya dago karma Juhud taji labari da kaduwa tasata zamewa daga kujerar ta sauko qasa tayi dabar tana kallon Dada Hanne.  Harara ta watsa mata tace “eh Mana biri yayi kama da mutum to nidai tunda abinnan ya faru nake biyar malamai da yan bori idan suka hau bori suka jirge sai suce ai saqale kurwarsa akayi akayi bandarsa" gabadaya hankalin kowa sai ya dawo kan Juhud da itama take jujjuya mgnr a kwakwalwarta Dada Hanne tace “kuma fah cewa sukeyi makusancinsa ne yayi masa wannan abin kawai saboda yanason cin gado to nidai naga kaidai Mahfuz bazakayi wannan abu ba itama Mom din yara bazatayi ba saura da me dama Kuma ku hudune magadan nasa....."

Miqewa Kareem yayi yace “don Allah dakata Dada kada kizo Mana da surkullen hauka cikin wannan lamari ke Ina kika taba ganin anyi bandar mutum banda sakarcinku na mata? Kuma ma meye Rasheed ya Tara da har zaayi tunanin kasheshi don gadonsa haba dallah ku rinqa auna mgn kafin kuyita Mana" Yana fadin haka ya miqe zumbur ya dubi Addansa daketa harararsa ya dubi Mai Martaba da Mom yace “wlh daukan alhakin Meenah zakuyi indai kuka zargeta yarinyar nan batada wani abu da ta sani game da batan mijinta haba ai abinda zai yuwu ma dagaji ansanshi" ficewa yayi daga gdan idanunsa nakan Meenah da keta jan zuciya tunda mijin nata ya bata take cikin masifa  komai Yana neman koma mata baya gdan an qara tsangwamarta da Mom kawai takejin dadi sai Kareem daya mayewa Sarki junior madadin bsbansa komai ya tarkato Sarki.
Ana haka Mai Martaba yaga zaman ya fara tsayi Abu ya tafi shekara biyu ya Sanya Kareem ya nema mata admission bayan sun biya mata an zana mats jamb  lkcn da sukayi mata mgnr karatun fir qi tayi tace ita bataso daqyar Mom da Kareem sukasha kanta ta yarda ta fara zuwa Alqalam University Katsina bata jima da fara zuwa ba abubuwa suka fara canzawa Dada Hanne da Alh Aminu suna zuga Mai Martaba baiyi furuci ba Amma gabadaya ya janyewa Meenah tallafi babu Wanda yasan dalili Mom ce taci gaba da dawainiya da karatun nata ita da Kareem.

A hakadai da dadi babu dadi take gurgura karatun cike da samatsi da qalubalen rayuwa kullum addu'a takeyi Allah ya bayyana mijinta itama ko ta samu hasken zuciya. Yau da gobe ce tasa Kareem bawa Mom shawarar kama mata hostel saboda karatun nata na Law yanajan kudi sosai hakan kuwa akayi suka kama mata hostel ta koma can da zama Sarki junior na gurin Mom yanata girmansa inda a lkcn Ya'isha ta ta haihu Zahran Kareem ma ta haihu  taso zuwa daidai lkcn suna exam hakanan ta hqr sai bayan Exam akayi hutu ta shirya domin zuwa tayi barkar ta nufi Daura cike da kewar gudan jininta da sallamarta ta shiga falon  Sarki ya taso da gudu ya rungumeta ta dagashi tana juyashi suna dariya tayi kissing nasa tace “miss you love

inata kewarku"
Lakace mata hanci yaran me shekaru hudu yayi yace “yaushe zaki dawo?" Narkar dakei tayi tace “saura semester guda Son ka matsu na dawo ne?" Turo baki yayi yace “Addah Fadila ce tacemin na daina zuwar mata gidanta kada na cinye mata su Jabir Momy wai tace kece kika cinye Dad Ina ya bata....." Gwabe bakinsa Mom tayi tace “ba nace maka idan na qarajin mgnr nan a bakinka saina yankaka ba" riqe bakinsa yayi alamun yayi shiru ta daukeshi jikinta a mace ta nemi guri ta zauna suka gaisa da Mom ta miqe tace “zanje nagano babyn Ya'isha" miqewa itama tayi tace “nima abinda ya kawoni kenan hutunmu na sati daya ne Kuma tun shekaran jiya akayi" dungumawa sukayi suka fita suna fitowa Muntaz na shigowa Mom tace “yawwa zo ka kaimu gdan Ya'isha"

Babu musu yaja suka tafi suna taba yar hirarsu tace “Jiya Hafeez abokin aikin Baffa'am yakaimin ziyara" murmushi Mom tayi tace “nan ms yazo gurin Mai Martaba yazo ne da wani shirme wai qa'ida shekara hudu ne idan mijin mace ya bata alqali zai bata damar tayi aure ke anbaki dama ne? Tsaki taja me zafi tace “shege sai naci kutumar ubansa ni ce masa akayi mijina bazai dawo bane nifa Mom bantabaji a Raina Baffa'am ya mutu ba Yana raye kawai dai Allah ne be gama ganawa ba" numfashi Mom taja tace “nima haka nakeji so naga Mai Martaba ya saduda shiyasa nima na fidda rai da tsammani" shiru ce ta dan gifta suka Isa gdan Kareem ta jinjina haduwar gdan karo ns farko data sanya qafarta a gdan tun aurensa da Zahrah kasancewar Zahra mugum baqin kishi takeyi da ita to itama shiyasa taja jikinta.
Da sallama suka shiga aka Amsa musu Dada Hanne na dagowa taga Juhud tayi maza ta dauke jaririn tasa a bayanta suka gaisa tayima Zahrah barka tana amsawa a yatsine ta aje kayan data siyowa bebin tana satar kallonsa a bayan Dada tanason jariri a rayuwarta bata samu arziqin daukan jaririn ba Kareem ya sauko tunda ya fito idonsa na kan Juhud dake wasa da yatsunta yace “aa Meenah Ina cewa zanzo na daukoki ashe kina hanya" murmushi tayi masa tace “wlh na matsu nazo naga baby's din da muka samu shiyasa na biyo motan haya" shafa kansa yayi yace “insha Allahu cikin satinnan motarki zatazo haihuwar nan cema ta dan takemin birki" gdy tayi ta miqe saboda bata cikason zaqewa a lamarinsa ba ganin haksn yasa Mom miqewa sukayi sallama ya biyosu har jikin motarsu yanajan Sarki da wasa suks shiga suka tafi shikuma ya juya suka nufi gdan Ya'isha.........

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏽 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane ki biya 300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/6, 10:48 AM] Oum Hairan: *0029* A gdan Ya'isha suka shantake sunata fira Basu suka baro gdanba sai gefin magrib suna shiga gdan gaban Juhud ya fadi batare da tasan dalili ba suka nufi parlourn da sallamarsu a tsaitsaye suka tarar da Addah Abulle da Fadila Juhud na Shirin mgn taji an shaqeta ta baya batare da sanin waye ba suka rinqa kokawa daqyar Mom da Muntaz suka rabasu Fadila na huci ta nuna Juhud da ta zubanta ido tace “muguwa azzaluma Ni dama tunda akace kinje barka nasan ba Alkhairi ne yakaiki ba ace daga zuwanki jaririya ta kama cuta kwana uku da haihuwarta batayi ba sai yanzu da kikaje to wlh ki sakar Mana kurwar yarinya ko mu aikaki lahira shegiya baqar kadara"
Cafewa Addah Abulle tayi da cewa “to waima meye yakaita barkar waye yace Yana buqatar barkarta gsky nikam wannan lamarin na gdannan ya isheni Abu ya wucce kan wadanda suka jajuboki ya dawo kanmu shekara uku dayin auren nan baa haihu ba shine daga kinji an haihu zaki lashe musu ya tab wlh bazai yuwu ba dole ma Mai Martaba ya zaba a gdannan ko mu da muke dolensa ko Kuma ita da suka liqawa mutane" tunda suka fara mgn ta fahimci inda suka dosa jikinta yake rawa hawaye ya kasa tsayawa a idanunta mgn takeson yi Amma bakinta ya sarqe zuciyarta wani zafi takeyi hakanan takejin a ranta yau ko zata fita a kasheta sai tabar gidan lamarin ya fara wucce yanda zuciyarta zata dauka. Juyawa tayi ta shiga dakin da take taja akwatu ta fara hade takardunta tana wani irin kuka me ciwo itakam tagaji da wannan quntattaciyar rayuwar shekaru ashirin da biyar na rayuwarta ta qaresu a qunci shekaru tara Mom na hadiyar baqin ciki akanta meye yasa bazata gushe ba kota samu salama da sanyin ruhi suma masoyanta su samu?
Tanayi tana jan zuciya tana tunano yanzu hakanan zata fice tabar gudan jininta daya tal a duniya meye makomar rayuwar Sarki idan ta tafi ta barsa? Dagowa tayi bayan ta gama hada kayan ta zuge ZIP din trolley din ta miqe ta dauki hijjab dinta ta zura taja akwatin takai hannunta zata bude qofar Mom ta bude ta shigo idanunta na tsiyayar da hawaye tace “duk wani abu daya kamata nayi miki Meenah nayi miki domin Allah meye yasa qaramin Abu yakesaki jin tafiya kibarni shine mafita? Me kikeso nacewa Rasheed idan Allah ya bayyanashi yaji abinda kika aikata? Haba Meenah nidai Ina ganin indai kika yanke barina to tabbas baki biyani haqqina ba Kuma kin basu damar yimin dariya ne......."

Wani kuka ta saki me ciwo tare da durqushewa ta kifa kanta jikin akwatin tanayinsa babu furuci

kalma batada ita a bakinta da zata iya furtawa zama Mom tayi tana bata baki tana rarrashinta Amma kamar tana zugata, aka bude qofar aka shigo Mai Martaba ne ya shigo fuskarsa Babu alamun wasa yace “ke Aisha tashi ki bani guri inason mgn da ita" miqewa Mom tayi ta fita tana kallon Meenah data dunqule tanata aikin kuka ta girgiza kai ta fice daga dakin ya nemi guri ya zauna Yana nazarin yarinyar da yanda duk jikinta ke rawa jikinsa yayi sanyi shi kansa yanajin kunyar kansa irin biyayyar da yarinyar takeyi masa bata cancanci haka daga gareshi ba ta daukeshi kamar mahaifi tanayi masa biyayya fiye da yanda yayan daya Haifa sukeyi masa to waima meye yasa yake yarda da jita jita akanta ne?"
Gyaran murya yayi yace “ina kike Shirin tafiya yanzu?" Cikin kuka tace “inda ubangiji ya kaini don girman Allah karka hanani Mai Martaba na gaji wlh na gaji da qaddarorin nan masu wahalar dauka inaji a jikina banida wani rabo na farin ciki a rayuwata Mai Martaba idan ka hanani zan rasa kaina zuciyata zata buga....." Jinjina kai yayi cike da tausayawa yace “meye yasa kika yanke wannan hukuncin?" Dagowa tayi idanunta akansa bakinta ba rawa tace “Baffa'am shine mutum na farko dayayimin gata ya zabi farin cikina akan komansa Mom ta dora sunci baqin ciki akaina sunama kan ci wlh koda bana tare da mijina inaji a jikina duk inda yake hankalinsa yana gareni Mai Martaba bazan zama silar bacewar da na zama silar macewar uwa ba idan naci gaba da zama da Mom baqin cikin abinda ke faruwa Dani zai iya taba tata rayuwar nikam na riga na zaba na yankewa kauna da samun wani jin dadin rayuwa kubarni naje na rayuwa ni kadai abinda kukayi a baya na gde....."

Daganta hannu yayi yaja zuciya yace “naji Meenah  ki cire wannan tunanin a ranki Babu inda zakije kinanan" miqewa yayi ya fita daga dakin yana fita ta koma ta kwantar da kanta jikin gado tana wani kuka me ciwo, tana jiyo hayaniya da fadan Mai Martaba a falo saidai bata fahimtar meye yake cewa sama sama taji yana cewa “ni na haifi Rasheed na haifi Kareem dukkansu ikona ne duk da qaddara tasa Meenah bata zama mallakin Kareem a farko ba hakan bazai zama hujja ta cin mutumcinta ba wlh tallahi Zainab duk ranar da wani abu makamancin wannan ya Kuma faruwa zakisha mamaki na Kuma babu wanda ya isa hanani zartar da abinda nayi niyyah a gobe juma'a zan yanke abinda nayi niyyah kai nama fasa yau dinnan idan da Wanda ya isa ya Hana"
Bata fahimci komai ba Amma sosai taji wata faduwar gaba ta darsar mata ta miqe ta shiga bathroom ta watsa ruwa ta dawo ta kwanta damuwa tasa zazzabinta na qa'ida ya dirar mata wanda likitoci sukayi ittifaqin zai iya haifar mata da ciwon zuciya saboda Yana yawan kumbura zuciyar tata.
Bacci ne ya dan dauketa sama sama kasantuwar ba sallah zatayi ba tanaji ana Kiran sallar Isha a masallacin Fada ta sake gyara kwanciyarta bacci me nauyi ya dauketa batasan meye yake faruwa ba sai ji tayi ana yiwa qofar bugu na hauka ta miqe zunbur tana son tantance dalilin bugun taji muryar Addah Abulle tana cewa “billahil lazi la'ilaha illahuwa indai nice na haifi Kareem bazai taba zama da wannan tsinanniyar yarinyar ba matsayin mata wlh Allah saidai idan na kasheta nima a kasheni"

Muryar Mai Martaba taji Yana cewa “bazama takai ga kisan ba kizo ke ki fita a gdannan ki tafi gdan naki uban aure ne na daurashi Babu dalilin fasashi" bude qofar taji anyi ta sake zabura ta zubawa me shigowar ido Kareem ne ya shigo idanunsa akanta itanma shi take kallo ido cikin ido ya mayar da qofar ya rufe ya nufota taja baya da sauri yaja ya tsaya Yana kallonta ya dan saki fuskarsa batare data tsammata ba taga wasu hawaye sun kwaranyo daga idanunsa ya daga hannu sama yace “Alhmdllh Meenah duk da banyi tsammanin zuwan wannan lkc da wuri ba Ina tayamu murnar samun kanmu a sabuwar rayuwa matsayin da naso samunsa a farko ubangiji bai amince ba wato ma'aurata.........."
Ai bai rufe bakinsa ba ya tsinceta a qasa warwas yayi kukan kura ya isa gareta Yana jijjigata Addah Abulle ta danno qofar tayo kansu da wuqa tsirara a hannunta ya miqe da sauri ya tareta Mai Martaba da Muntaz suka tayashi riqeta ya damqe kaifin wuqar da hannunsa tana wani kuka me cin zuciya tana cewa “wlh saina kasheta mayya cikin zuri'a ta bazan taba lamunta ba......"

Abinda Mai Martaba baitaba yiba yau shine yayi mata allurar yan maza ta motsa abinka da tsohon soja baisan sanda ya saketa ba yayi bal da ita taje ta daki gini ta dawo qasa tana qoqarin tashi ya sake nufarta Kareem da hannunsa keta zubar jini saboda riqon da yayima wuqar ya nufeshi da sauri shida Muntaz suka riqeshi daidai lkcn da Arman ya shigo shima yayi kan Mai Martaba Mom ce da Salman sukayi ta Juhud suka kimkimeta Kareem ya saki Mai Martaba har yanzu kuka yakeyi yace “don Allah Mai Martaba kada kayi abinda kayi niyya ka qyaleta tayi duk abinda da tayi niyya aurena da Meenah ne Allah ya riga ya daurashi babu abinda zai kwanceshi saidai mutuwa ko qaddarar data raba auren Rasheed da ita"
Fita yayi da sauri ya shiga motarsa yabi bayan tasu Mom suka nufi asibiti sukayi emergency da ita likitoci suka rufu akanta numfashinta suketa qoqarin saqalowa abin ya gagara faduwar da tayi taja mata shiga doguwar suma, ranar daga Kareem harsu mom Babu Wanda ya koma gda anan suka kwana gurinta gabadaya ya rude hankalinsa yaqi kwanciya Yama manta da lissafin yar jaririyar yarsa da take asibitin itama ta Juhud din kawai yakeyi Muntaz ya tafi gda suka dawo da Hamida da Mai Martaba Addah Abulle bata gdan hankali ma baya kanta balle asan Ina ta nufa.

Mom da Hamida ke jinyarta tsayin kwanakin biyar batasan waye akanta ba Kareem ya canza mata asibiti yakai uku qarshe Asibitin Mal Aminu Kano ya mayar da ita acanne suka samu ta fara motsa gabbanta sai lkcn ya samu nutsuwar tunawa da iyalinsa har zuciyarsa nutsuwarsa ta rabasa da tunanin komai sai lfyr Meenah babban tashin hankalinsa da likita yace masa

zuciyarta ce take barazanar daina aiki saboda ta cunkusa mata damuwar da tafi qarfinta tunaninsa ta yanda zai fara nasa aikin ya goge mata duk wata damuwa dake buwayar rayuwarta ya sanyata farin ciki kamar yanda ya shirya yi a farko Allah bai amince masa ba burinsa bai wucce Meenah ba cikin duniyarsa gata ya sameta Amma Kuma wasu abubuwan sun danni soyayyarta gareshi tsabar qin da takeyi masa ne yasata shiga wannan yanayin dajin cewa shine matsayin mijinta ko meye dalili?
Wadannan tunane$^{2}$n sune suka sanyashi ramewa cikin kwanaki biyar din.

Ranar kwana biyar din ranar ta kama sunan Matarsa hakanan ya nufi Katsinan bashi da wani kuzari dake yasan dama ba taron sunan akeyi ba har zuwa lkcn Zainab sunan yarinyar kenan sunan mahaifiyarsa yasa mata tana asibiti ciwon gendis yayi mata kamun gaske anyi mata juyen jini Amma duk da haka taqi Ify inda likitoci suka tabbatar da a cikin mahaifiyarta ta samu matsala Amma su sun dauki alhakin ciwon kacokan sun dorawa Meenah musamman su Dada Hanne da dangin Zahrah da sukayi tsalle suka dire suka dauke yarsu cewa bazata zauna da Meenah ba shidai daya yakabo yaje ta qare masa,
Bai damu ba koda yaje gdan nasa ya tarar dashi a kulle domin ya riga ya shiryawa zuwan wannan Rana a baqin kishi irin na Zahrah ba Meenah data tsans fiye da kowa a duniya ba ko wacce mace ya auro sai anyi wannan rikicin shiyasa baisa abin a ransa ba taje tayita zamanta a gdannasu idan ta gaji ta dawo. Kwanan Meenah bakwai a Kano ta bude idanunta tana kallon kowa daidai a lkcn tunaninta bai dawo ba bama kowa take ganewa ba hakanan ta rinqa rarraba ido kan mutane.

Mom sai sannu take jera mata tana binta da kallo da la'asar Kareem ya iso asibitin shida Ya'isha tun daga harabar asibitin ya hadu da Lado drivern Mai Martaba yayi masa albishir din Juhud wani farin ciki da murna daya dade baiyi irinsu ba suka cika zuciyarsa har gudun motarsa ya qara don ya isa gareta yayi parking baikai ga rufe motar ba ya nufi ciki sai Ya'isha ce ta rufe masa motar cikin tausayinsa ko lkcn da Meenah take matsayin matar Rasheed Kareem baya zama cikin nutsuwa muddin tana guri Allah ya jarabceshi da qaunarta gashi Kuma yanzu tasan ba qaramin rikici ya saukowa kansa ba don tabbas Meenan da ba itace yanzu ba batajin zai samu kanta da sauqi duk wannan rawar qafar da yakeyi akanta ba gani zatayi ba tunda bashine a zuciyarta ba hasali ma ita a lissafinta ma Babu aure.
Yana shiga bai saurari kowa ba ya nufi gadon da take kwance idanunta a lumshe yaja wata

ajiyar zuciya tare da binta da kallo me nuna tsantsar qauna da kulawa yace “Aminatuh" jin saukar muryarsa tayi kamar muryar Rasheed ta kuwa juyo da sauri tare da bude idanunta ta saukesu akansa yanayi mata gizo cancanzawa yakeyi daga Kareem ya koma Rasheed ta kasa gane taqamaiman waye a gabanta.

Tun farkawarta bata iyayin furuci ba sai yanzu da bakinta ya bude da furta “Abdulrasheed....." Daga haka ta sake lumshe idanunta ta kwantar da kanta a pillow kuka me ciwo ya qwace mata daya Sanya Mom dake shigowa nufota da sauri tace “Subhanallahi waike yanzu Aminatuh bazaki daina Sanya damuwar nan a ranki ba kenan kullum ke kenan cikin jinya" wata ajiyar zuciya me qarfi Kareem ya sauke ya nemi guri ya zauna gumi na karyo masa Yana sharcewa Ya'isha dake shigowa tace “ya Kareem motar taka baka rufeta ba ka barota" shafa sumarsa yayi yace “wlh hankali nane baa jikina ba ince kin rufe" dagansa kai tayi ta nufi gadon da Meenah ke kwance ta riqo hannunta tace “amaryar Ya Kareem sunqi Allah yaso meye yayi zafi da doguwar jinya haka?" Zame hannunta tayi a na Ya'isha ta sake gyara kwanciyarta taci gaba da jan zuciya abubuwan da suka sabbaba mata ciwon suna dawo mata a fili tace “Aure, Ni Mai Martaba Ya Kareem Innanillahi wa Inna ilaihir raji'un Allahumma ajirni fih musibati wlh banaso don Allah ku taimakeni ku rabani dash.........

_Nasani wannan page din ba kowa zatayima dadi ba so Amma a babin qaddara wannan daidai ne shi ubangiji Yana zartar da hukuncin da yake daidai batare da la'akari da abinda Wanda ya zartar da hukuncin akansa zai nazartawa zuciyarsa ba kada ku manta matar mutum kabarinsa Kuma shi rabo ajali ne yakanyi kisa ma idan qarfinsa yakai._
_So kada kuga laifin alqalamina haka abin yake kamar yanda kuka ganshi a rubuce kada ki manta 50% is true life story._

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏽 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account

din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/6, 9:00 PM] Oum Hairan: *0030* Miqewa Kareem yayi ya fice daga dakin ya koma waje ya rafsa tagumi jikinsa sai tsuma yakeyi Yana tausayin kansa Amma yafi tausayin Meenah saboda tafisa shiga damuwa ya jima zaune a gurin kafin likitan ya iso suka shiga tare likitan ya dubata ya sake bata kulawa ya fice daga dakin ya dubi Juhud datake zaune take shan tea yace mata “sannu" bata ko dubesa ba ya nemi guri ya zauna Suna taba hira lkc zuwa lkc suna taba hira da Ya'isha Mom tana Sanya musu baki itako ko kallo bai isheta ba hasali ma tunda ya zauna takejin wani qunci aranta ji takeyi kamar ta fice daga dakin bata son ganinsa.
Kwanciya tayi taci gaba da saqa da warwara a ranta sai yamma Ya'isha tace zata tafi mijinta yazo daukanta sukayi sallama suka tafi Mom ta tafi rakasu ya taso ya matso jikin gadon yace “duk da nasan ni mai laifine a gurinki Meenah Allah ya sani inasonki tun kafin yanzu Amma bantaba yimiki fatan ki dawo gareni ba Allah shine ya tsara hakan saboda haka na karba Kuma nayi masa gdy kema inaso ki karba kiyi masa gdy......" Miqewa tayi zaune zuciyarta na tafasa tace “akanme zanyi gdy akan abinda ba zabina ba bankuma nema ba? Why da zakace dole saina karbeka? Kareem da zaka manta dani ka fice cikin rayuwata da mun taimaki kanmu wlh banyi farin ciki da samunka matsayin miji ba kada kaji a ranka na karbeka bazan taba karbarka ba Rasheed shine zabina shine rayuwata......"

Hannunsa ya dora bakinta yace “stop Meenah ya isheki don Allah kada ki fasamin zuciya da kalamanki kiji a ranki wannan bayin kaina bane yin Allah ne..... Wayarsa ce tayi ring ya zaro a aljihunsa number Zahrah ce yayi kamar ya kashe saidai zuciyarsa ta raya masa ya daga qila wani abune Important yasata kiransa  danna wayar yayi ya Kara a kunnensa ta cikin wayar Meenah take jiyo gunjin kukanta tana cewa “Allah ya isa tsakanina dakai Kareem ka cutar dani kaine wlh kaine sila tunda kaine ka rakitomin ita cikin rayuwata harta cutar dani, na dauki ciki watanni tara na Haifa matarka ta kashemin yata wlh bazan yarda ba kaji na rantse maka wayyoh Allah na Zainab ta mutu Aminah ta lashemin yata......"
Qit ya kashe wayar idanunsa ya ciko da hawaye ya dubi Juhud data zubawa TV idanu a zahirinta ba TV take kallo ba kalaman na Zahrah ne sukeyi mata yawo a kwanya yace “kinji sauqi likita yace zaki iya komawa gida zanyiwa Mom mgn ta shirya mu tafi Zainab ce ta rasu...."

Bata ko kallesa ba taci gaba da wasa da yatsunta yaja numfashi ya fice a dakin suka hade da Mom a reception ya tsaya Yana dubanta da jajayen idanunsa da damuwa biyu tasa suka kada

tace “yanzu ake fadamin Zainab ta rasu ya kamata kazo ka tafi kaima tunda jikin nata da sauqi" girgiza kai yayi yace “ban yarda da hankalin Meenah ba Mom zata iyayin komai Ina tsoron kada na tafi tayi tunanin guduwa tabarni wlh mutuwa zanyi a wannan karon Mom ke shaida ce na wahala a karon farko dana rasata don Allah ki tausheta ta soni koda kwatan Wanda nakeyi matane ni basai yakai rabi ba inasonta a haka"

Murmushi Mom tayi me dauke da hawaye ta dafa kansa tace “Abdulkareem to Banda abinka Meenah yanzu ai taka ce kasan dai ba cikakkiyar Ify gareka ba don Allah ka rage damuwa da duk abinda zatayi zai hucce kasan kaima dole zaa fuskanci wannan qalubalen tunda ba ita taga damar auren nan ba Ni kaina Meenah fushi takeyi dani ban damuwa domin nasan gata Mai Martaba yayi mata kaidin dama kaine ka dace da ita Hukuncin Allah ne yabawa Rasheed da Kuma rabon Sarki junior Kuma ma ai tanasonka tun a baya kawai yanayin da take cikine yasa zakaga kamar batasonka"
Murmushi yayi yace “hakane Mom na gde am Dr yace zamu iya tafiya gda nikam zanfi samun nutsuwa tana tare dani" batason jayayya dashi shiyasa ta aminta su tafi din ta shiga dakin ta fara hada musu kayansu Meenah na kallonta harta gama ta dubeta tace “mu tafi mijinki ya matsa saidai mu tafi gabadaya" daqyar Mom tasha kanta ta miqe suka tafi baya ta shiga yana kallonta yayi murmushi sai Mom ce ta shiga gaba suka nufi Katsina da suka isa Daura ta samu ta fita a mota tayi wuf ta shige dakin da take ta fada gado ta rushe da sabon kuka tana tuna wai yau ita ce matar Kareem bata Rasheed ba meyesa qaddararta kullum ita baibai ce a fili tace “Ikc yayi da zan nemawa kaina gata dole na nemi su Baffa Ribado ko zasu kasheni su fitomin da dangin mahaifiyata"

Qwanqwasa qofar taji anayi ta miqe ta bude qofar ganin Kareem ne tayi saurin mayarwa ta datse yaja baya da sauri tare da cije lebe ya juya a kasalce ya fice daga gdan ya nufi gdansa babu kowa kamar yanda ya tsammata yayi murmushi ya nufi gdansu Zahrah acan ya tarar da yan karbar gaisuwar bai wani zauna ya dade ba ya nufi gidansa ya kwanta a gado Yana saqawa da warwarewa akwai aiki a gabansa.
Meenah batashi takeyi ba baya a lissafinta ga Addah Abulle ta takura masa da Kira har takai baya daga wayarta saboda yariga yasan mgnrta bata wucce akan qiyayyar aurensa da Meenah tana qara tuna masa tun tana budurwa an hanashi sai yanzu data zama saura ragowa sannan ga rashin asali kalma daya yake fada mata Babu komai Addah inasonta a haka ba meenah ce ta qini ba a farko fin qarfinta akayi saboda hska nima bazan qita ba" idan ya Fadi haka Adda ji takeyi kamar ta kasheshi shima gashi Mai Martaba yaqi sauraronta balle yaji kokenta hasali ma fushi yakeyi da ita wannan tasa ta zare hannunta daga lamarin Kareem din ta zubansa ido tare da cin alwashin indai itace ta haifeshi to Meenah ta gama kwanciyar hankali a duniyarta saisun takurata sun azabtar da ita ita da yan'uwanta babban abinda yake daganta hankali Zahrah yar

wanta ce ta nemawa Kareem aurenta don huce haushi yanzun Kuma ya samu abinda ransa yakeso bayama ta ita tunkan tafiyar tayi nisa.

Wadannan dalilan suka hadu sukayiwa zuciyar Kareem yawa abinka da mara isasshiyar Ify nandanan zazzabi ya rufeshi shi kadai a gda yayita murqususun ciwo yana dafe qirjinsa wayarsa ma ya kasa dauka ya kira wani, baa Ankara ba Saida ya kwana shidda yana fama da ciwo shi kadai a gda sannan ubangiji ya kawo masa sassauci a galabaice ya lalubi wayarsa ya Kira layin Zahrah bugu yafi biyar tana gani taqi dagawa ya hqr ya Kira na Meenah itanma yayi mata misscall yafi goma tana kallon wayar taqi ta daga qarshe ma ta kasheta gabadaya ya jinjina kai cikin azabar ciwo ya Kira layin Mom dan yasan idan ya Kira na Addah ma itanma kamar yanda matansa Basu saurareshi ba itama ba saurararsa zatayi ba.
Bugu daya Mom ta daga tace “dan halak kaqi ambato Ina ka shigene inata nemanka bana samunka....." Nishin da taji yanayi ya fadar mata da gaba tace “ya salam kardai bakada Ify ciwon ne ya tashi Kareem....." Cikin rawar murya yace “Mom....ki....ki taimaka ki kawomin Aminatuh don Allah kada ta zamo silar ajalina sonta zai kasheni...."
A gigice tace “o.... Ok ganinan don Allah kada ka mutu Kareem mukam mun shiga uku da wannan masifa" kashe wayar tayi ta zari mayafinta ta fice a kidime ta nufi dakin Meenah tana zaune tana koyawa Sarki Homework ta dago ta dubi Mom tace “Lfy Mom?" Sharce gumi tayi tace ”taso ki rakani unguwa"

Babu musu ta miqe ta dauki mayafin doguwar rigarta ta sanya ta kama hannun Sarki suka fito ita kejan motar Mom na fada mata inda zasu tana fahimtar gidan Kareem suka nufa hasken fuskarta ya dauke ta hade rai donma Mom tafi qarfin musu ne a gurinta shiyasa tayi shiru har suka isa gdan suka Mai gadi ya bude musu sukayi parking Mom ta fito itakam gyara zamanta tayi Mom ta dakanta tsawa tace “bafa nason sakarci Meenah ki fito mu shiga nace"
Tana qunquni ta fito suka shiga cikin tun daga falon taji gabanta na faduwa komai a hargitse tabi falon da kallo taja tsaki Mom ta haura saman tabi bayanta tana kallon tsarin gdan bude wata qofa Mom ta Kuma yi qofofi ne guda biyu suna kallon juna ga mamakinta nan dinma falo ne sai wasu qofofin biyu tsayawa Mom tayi tana tunanin wacce zata bude Sarki yace “Mom ga dakin Uncle nan" Yana mgnr Yana murda qofar suka shiga a tare itakam guri ta samu ta zauna a falon tana hura hanci.
Yanayin da Mom ta isheshi yayi mugun tada mata da hankali ta saki wani kuka tace “innanillahi wa Inna ilaihir raji'un Abdulkareem meye hakan kashe kanka zakayi a gda kai kadai" gaban Meenah ya sake faduwa lkcn da Mom ta qwala mata Kira ta miqe a razane ta shiga dakin tare da zaro  ido Yana kwance a qasa magashiyan cikin wani mawuyacin yanayi ya bude idonsa ya saukesu akan Juhud tare da sauke ajiyar zuciya ya fara yunqurin miqewa Yana cewa “Am.... Ami...na...tuh zo... matso gareni please...." Janyewa tayi tayi baya idanunta na kansa Mom ta

tura ta fada jikinsa ya lumshe idonsa tare da sanya hannunsa ya zagayeta yaja wata ajiyar zuciya me qarfi tana qoqarin qwacewa ya bude bakinsa yace “na...na gode Mom ke kadai kike tausayina a duniya Mom Meenah bata sona...." Juyawa Mom tayi ta fice saboda yanda taga Yana qara matse matarsa a jikinsa abin yabata tausayi da kunya ta lura da Rasheed da Kareem tafiyarsu daya Basu da kunya akan abinda sukeso.......

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏽 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane kada ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*

[8/7, 7:18 PM] Oum Hairan: *0031* Da qyar ta samu ta janye daga jikinsa idanunsa suna lumshe hawaye yake zubarwa ya riqe hannunta yace “Nayi tunanin kedin me yarda da qaddara ce da hukuncin ubangiji Meenah ashe ba haka bane Meenah ko bazakiji tausayina ki daina azabtar da ruhina don na cancanta ba ya kamata kiji qaina don qaunar da nakeyi miki inasonki ne Meenah da jinina da rayuwata" Yana mgnr numfashinsa ba kakkatsewa hakanan taji bazata iya jure cigaba da kallonsa a wannan yanayin ba ta miqe zata fice ya Kira sunanta ta tsaya ya dauki wayarsa ya miqa mata yace “idan tafiya zakiyi ki kiramin Amrah ko Urwat ko Muntaz wani cikinsu yazo ya zauna dani Ina cikin yanayin da komai zai iya faruwa dani"
Harararsa tayi ta fice a ranta tana cewa “badai ni ka zaba ba wlh saidai ka mutu yanda uwarka da yan'uwanka ke qina haka nima nakeji game daku ban shirya zama da wannan ahlin ba abarni na rayu da zabina koda baya tare dani nasan Ina kwance a zuciyarsa" sauka tayi qasan ta tarar da Mom da Dr Razaq suka dubeta tare sukace “ya me jikin" a gajarce tace “yana ciki" ta juya ta fice ta shige mota shiru dogon lkc ya wucce basu fito ba can taga mota ta shigo Mai Martaba ne da Arman suka shiga suka daukoshi suka fito dashi. A mota suka sanyashi suka fice Mom ta shiga mota Juhud taja suka fita sosai ta qular da Mom da halin ko in kula din data nuna akan mijin nata bata taba tunanin zuciyarta tayi soyewar haka ba.

Saida sukaje gda ta juya zata shiga dakinta Momy tace “bantaba tunanin hakan daga gareki ba Meenah mijinki zabinki a baya banga zafin da rayuwa tayi tsakaninki dashi ba da zaki zabi azabtar dashi Meenah koda a yanzu baki zabeshi ba cancanta aka duba aka zabanki shi kada kiyi wasa da damarki inaji a jikina Kareem zai sharenki hawaye don Allah Meenah indai da gaske kin daukeni matsayin uwa a gareki kiyima mijinki biyayya ki rintse idonki ki ninka hqrnki akan wanda kikayi a baya. Tabbas akwai qalubale cikin zamanku to Amma qaddara ta riga fata haka Allah ya shirya mana addu'a Rasheed yake buqata kawai daga gareki"
Sunkuyar da kanta tayi tana sauraron Mom harta gama fadar abinda zata fada
Ta juya ta fita ta kwanta rigingine zuciyarta na hasaso mata abubuwa da dama da suka faru a baya Ikc zuwa Ikc tana dauke hawaye a fuskarta itadai batasan sanda bacci ya dauketa ba wajen biyun dare ta farka tayi alwala ta tayar da nafila tana roqon Allah ya shiga lamuran Rasheed a duk inda yake ya tsareshi da tsarewarsa ya bayyana shi cikin aminci da salama bayan ta idar ta zauna tana lazumi taji wayarta tana ring takai hannu ta dauka lambar Kareem ce taja tsaki ta katse wayar ya Kuma Kira ta dauka zata kashe maganganun Mom suka rinqa dawo mata tayi qarfin halin dorawa a kunnenta

Ajiyar zuciya ya sauke Ikcn da tayi masa sallama ya Amsa cikin wata irin murya me tsananin sanyi shiru taci gaba da wanzuwa wadda harta sabbaba mata tunanin kashe wayar can taji ya sake jan zuciya yace “nayiwa Mai Martaba mgn game da tariyarki yace nayi miki mgn shiyasa na kiraki a wannan Ikcn me kike shiryawa meye plan dinki?" Shiru tayi kamar bazata ce komi ba shikuma yayi kasaqe Yana jiran jin cewarta alamar da yaga na ba mgnr zatayi ba yasashi cewa “ok bakida wani tsari ga dukkan alamu ni inadashi yau Litinin na baki zuwa juma'a ki gama komanki zaki tare a gdanki kici gaba da ibada kamar kowacce mace, ki duba account dinki na tura miki wasu yan canjika Basu da yawa kiyi hqr dasu idan basu isheki shirye$^{2}$nki ba zanyi qoqarin qara miki insha Allahu"
Katse wayar yayi daga haka tabi wayar da kallo cikin mamaki lallai ma Kareem dinnan yana fama da kansa yana fama da bala'i shikam dama ya hqr ya barta anan inda take da yafi musu kwanciyar hankali dukkansu. Qwafa taja ta duba alerting din da akayi mata dazun ta zare ido tare da cewa “wht? Me zanyi da kudaden nan ni Aminatuh 2 millions ta meye ce?" Komawa tayi ta kwanta baccin da bata koma ba kenan washegare wayewar Litinin ta fara shiri don komawa makarata Mom na kallonta batace mata komai ba harta gama shiryawa ta dauki jakarta ta saba tace “mom zan koma school" murmushi tayi tace “da izinin wa?" Kallon Mom tayi da sauri tace “izini Kuma?" Daganta kai tayi tace “mijinki ya kirani da asuba yace kada ki koma makaranta kiyi shirye$^{2}$nki juma'a zaki tare a gdanki Litinin me zuwa zaku tafi Saudi zai koma can da zama abinda yayi saura na karatunki yayiwa H.O.D na department dinku mgn zaayi bakin qoqari" zama tayi dabar a gurin gumi na karyo mata tace “ni Kuma Mom in bisa Saudi haba Mom don Allah kice masa aa inada abubuwan da sukafi binnasa muhimmaci anan Mom inason in nemi dangina su hadani da dangin mahaifiyata idan naci gaba da zama a haka akwai matsala please

Mom kisa baki don girman Allah"

Murmushi Mom tayi tace “wannan duk me sauqi ne ni na daukar miki alqawarin bibiyarsu har zuwa lkcn da zaa dace kibani address nasu" sunkuyar da kanta tayi hawaye wani nabin wani itadai bataso ba taso tayi komanta da kanta miqewa tayi ta koma dakinta ta kishingida zuciyarta na zafi haka yinin ya kusan qarewa kiran duniya da yakeyi mata taqi dagawa itafa bayan zafin tsanarsa saboda mahaifiyarsa da tayi harma da ganin rashin dacewar wannan auren nasu duk da tasan ba haramci a ciki Amma wata halal din ta cancanci bari don kunya.
Da la'asar tana kwance Mom ta turo qofar ta shigo da sallamarta ita da wata mata Meenah dake kwance ta miqe suka gaisa da matar Mom tace “wannan itace nakeyi miki mgn aurenta na farko yazo a wani yanayi baayi mata komai ba so data haihu an gyarata Amma anja shekaru kusan shekara antafi biyar shine yanzun nake buqatar ki qure fasaharki wajen gyarata ko nawa ne mijinta yace zai biya" suna hirarsu wannan Hajiyan na fito da saiwoyi da magunguna tana yima mom bayani tare da turaruka itadai tabe baki kawai takeyi bata yarda abin gaske ne ba Saida taga an dauki wani qoqo an zuba wani ruwan tsumi an dauko wasu barbade barbade anyi an gwamutsa da danyan madarar shanu wai sun miqo mata tasha.
Ta dubi Mom da idanunta daya kawo ruwa zatayi mgn ta kuwa daure fuska tace “aini dama nasan ban isa dakeba Aminatuh nunamin bani na haifeki b...."  Da sauri ta karbi qoqon maganin jikinta na rawa ta kafa bakinta ta shanye daqyar tana kakarin amai matar tayi murmushi tace “wannan shi kadai ma idan Tasha na kwana biyar ya wadatar bare zaa hada da wasu tun daga wannan rana Juhud ta bani ta lalace da magunguna wasu tsarki wasu Sha wasu dafawa itadai bakinta har daina tantance dandano yayi cikin kwanakin batada aikin daya wucce kuka.

Wayar ma da Kareem ke kiranta ta jefashi a blacklist ko ya Kira baya samunta hakan tasa dole ya qyaleta yasan duk inda yau takai da jimawa gobe tana tafe yanaji a jikinsa wataran wannan qiyayyar zata shude tunda da babu ita daga baya ta wanzu to watarana itanma zaa nemeta a rasa, da wannan tunanin ya tattarata ya zubanta ido akayita shirye$^{2}$n tariyar tata shine da Mom da Ya'isha da Aunty Hamida suketa digiminsu dakin uwar ango da yan'uwansa Babu me ko lale da bikin hasali ma ko bangaren da ake shagalin basuyi itama amaryar haka saidai idan Mom tayi mata dole sannan take dan motsawa hakana aketa kaiwa da komowa su Ya'isha sune yan jeran amarya har zuwa lkcn Zahrah bata dawo ba aka gyarawa Juhud dayan bangaren kamar yasan zaiyi mata biyu dama tsarin mace biyu yayiwa gidansa bayan sun gama gyarawa sun zubanta duk wasu kayan alatun rayuwa suka kullo suka taho gda sunata yabawa da kudin da Kareem ya narkar a furniture dinta lallai ba qaramin so yakeyiwa Meenah ba.
Ta dauki gyaran jiki na ban mamaki abinka da farar fata har wani yellow takeyi yanda Mom ke rawar jiki a wannan bikin ko Rasheed ne ya dawo ba lallai tayi ba ko lalle da akayi mata dishi$^{2}$

ya kama jikinta saboda tsabar gyara hatta gyaran gashi a gda akayishi yin duniya suje gurin gyaran taqi tana maqale a daki kamar wata mara gsky ko yaushe cikin kukan rashin mijinta take da anbarta da wannan damuwar ma da tafi mata fiye da wannan da aka qara mata

Ranar juma'ar Mom taga ikon Allah yini Meenah tayi tana kuka tana kiran Rasheed duk dauriyar da Mom takeyi a wannan karon Saida ta kebe itama taci kuka ta gode Allah Mom bata qara tsinkewa da lamarin Aminah ba Saida magrib da Kareem ya turo da motocin daukar masa amarya tunda ta fice a sashin su Mom din aka nemeta aka rasa babu wanda hankalinsa bai tashi ba amarya ta bace da aka fadawa Kareem neman zaucewa yayi ya nufo gdan afujajan suka shiga nemanta lungu da saqo domin sun tabbatar da cewa tana cikin gdan kasancewar masu tsaron qofofin gdan sunce Babu wacce ta fita gabadaya sun gama karade gdan babu dalilinta sai a qarshe Mom tace aje bangaren Rasheed ko can tayi haka Kareem da Mai Martaba suka nufi part din ga mamakinsu suka tarar dashi a bude suka kalli juna babu furuci suka kutsa ciki yayi qura sosai part din haka suka rinqa dubawa can cikin wani daki suka rinqa jiyo shassheqarta har rige² sukeyi wajen shiga dakin sukaja sukayi turus dukkansu ganinta zaune gefen gado rungume da wani hoto a qirjinta sai kuka takeyi me ban tausayi.
Wani abu me nauyi ne yazo ya tokarewa Kareem maqoshi ya furzar da iska me zafi ya juya ya fice daga dakin sai Mai Martaba ne ya qarasa shiga ya kamo hannunta Babu musu ta miqe tanaci gaba da kukanta idonta lullube da  alqyabba ya fito da ita harabar gdan Ya'isha ta nufosu da sauri suka sanyata a mota tana qarawa kukanta sauti tana Kiran sunan Baffa'am Sarki junior dukkan wanda yake a gurin hatta Mai Martaba Saida tasashi sharar hawaye.

Hakanan suka nufi unguwar da gidan nasa yake Mai gadi ya bude musu suka shiga sukayi parking Aunty Hamida ce take riqe da hannunta har cikin gdan suka haura da ita saman itama kamar dayan sashin dakuna biyu ne sai wani qarami da alamun local kitchen ne wanda koda zaka buqaci wani abu da dare basai ka sauka ba, daya cikin dakunan suka bude suka shigar da ita sosai Hajiya Kulsum aminiyar Mom ta qara yimata nasiha akan biyayya ga mijinta itadai Babu abinda da takeyi sai kuka da rawar sanyi zazzabi ne yake neman rufeta Ya'isha ta matso jikinta ta sunkuya tace “ke banza ce wlh Ni banga abin kuka ba to kukan mafita ya zame miki kome?" Dagowa tayi ta sauke idanunta sa suka jima da komawa jajaye saboda kuka tace “shi....shikenan da gaske na rasa Baffa'am dina Ya'isha Kuma akeso nayi rayuwar farin ciki....." Muryarta ne ya kama rawa Ya'isha tace “mun shigai Aunty Hamida ku Kira mijinta zata tayar mana da aljanu" yanda jikinta ke tsuma ne yasa Hamida yarda ta Kira wayar Rasheed ya daga muryarsa can qasa shima rawar tasa muryar takeyi yace “ya aunty Hamida ya akayi?" Cikin zaquwa tace “Meenah ke neman rikice Mana mun kasa gane kanta don Allah kazo idan kana kusa" kashe wayar yayi dake dama Yana gdan duk  motsinsu yanaji ya dauki doguwar riga ya saka ya bude qofar ya fito idanunsa kamar garwashi saboda ja dake duk yafisu Rasheed haske

shi fari ne sosai daka kalleshi zaka gane kukan shima yakeyi.
Kuka Fadila ta saka da ganin yanda yayan nata ya zama wani kalar tausayi tace “tunda yarinyar nan ta shigo zuri'armu muka daina cikakken farin ciki Ya Kareem kaima duk ta susutaka yanzu kukannan don ita kakeyinsa....."
Hanya ya saita mata cikin zafin zuciya yace “kowa yaje na gde" binsa sukayi da kallo ya dubi Hajiya Kulsum yace “Mama wlh idan akaci gaba da hayaniya a gdannan tsaf zan haukace brain dina tana neman daina aiki" sumsum suka rinqa ficewa daga gdan saida suka fice gabadaya ya tsaya yana jin tashin motocinsu gabansa faduwa yake daqyar ya tura qofar da sallama ya shiga dakin ya tsaya tsakiyarsa Yana qarenta kallo tana zaune ta dora kanta jikin gado sai tsumar jiki takeyi a sanyaye ya isa gareta ya tsugunna gabanta yakai hannunsa zai dago kanta gabansa ya fadi ya janye ya sake saita idanunsa akanta yace “meye yake damunki?" Kamar me jiran yayi mgn ta dago kumburarrun idanunta suka shiga cikin nasa ya kawar da kansa ya dake zuciyarsa yakai hannunsa jikinta yajishi zafi zau yaja numfashi ya miqe ya dauki wayarsa Yana zagaya dakin can yace “Inada petiant a gdana kazo da wuri don Allah" da haka ya kashe wayar yaci gaba da zagaya dakin can yaji ana qwanqwasa qofar ya sauka ya bude suka shigo tare Dr Razaq ya fara tambayarta yanayin da takeji tayi masa shiru shikam Kareem ido ya kafeta dashi can da tambayar ta isheta tace “Kaje Dr Razaq bakada maganin matsalata Allah ne kawai zaimin magani" wata iska Kareem ya furzar ya juya ya fice Dr Razaq ya biyosa yaganshi tsaye ya hade kai da garu ya dafashi yace “ka daina Sanya wannan damuwar a ranka Ranka shi dade kanada heart problem idan komai zaike damunka to rayuwarka tana cikin kwale$^{2}$"
Juyowa yayi ya dubi Dr Razaq yace “kana nufin Meenah zata soni nima?" Dariya tambayar tabawa Razaq yace “kama qaddara a ranka tasoka fiye da kowa ta gama karfa ka manta kaine ta fara so a rayuwarta ko ka manta Karin mgnr hausawa da suke cewa so baya tsufa saidai masoyan su tsufa bature kuma yace true love never end" wani murmushi yayi yace “na gde Dr Razaq zan jira Ikcn da zan gasqata hakan".............

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane kada ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/8, 9:07 PM] Oum Hairan: *0032* Sallama sukayi ya rakashi ya hau motarsa tare da karbar magunguna bai koma gdan ba shima ya shiga tasa motar Yana duba agogo 8:30pm ya jinjina kai ya fice a gdan kai tsaye wani restaurant ya nufa yayi musu siyayyar abinda zasuci ya juya ya koma gdan ya kulle ko Ina ya nufi saman Saida ya shiga dakinsa yayi wanka ya sanya kayan baccinsa ya fito ya bude nata dakin tana zaune inda ya barta har yanzu kukan takeyi gabadaya lamarinta ya tsinka masa lakar jiki da gaske take jin damuwar a cikin ruhinta.
Aje ledar dake hannunsa yayi ya tsugunna a gabanta ya kamo hannunta ta fuzge ya zauna sosai a gabanta ya dafe kuncinsa da hannayensa biyu ya zuba mata manyan idanunsa da a baya suke firgitata da sanyata shiga taitayinta baiji a ransa ko yace ta tashi suyi nafila zatayi ba shiyasa ya janyo ledar yace “Ya'isha tace tun shekaran jiya bakici abinci ba ko meye dalili?"
Shiru tayi masa yaja fasali ya furzar da iska ya bude ledar ya fara yaga mata Naman yanda zataji dadin ci ya dauko yakai mata bakinta ta kawar dakai yayi murmushi yace.
“Lamarinki abun mamaki ne Meenah sai naga kamar kina jayayya da hukuncin ubangiji ne ya kamata ace rayuwarki kadai ta ishenki darasin da duk wani abu da Allah yayi zaki tarbeshi hannu biyu wlh duk da nakasance me qulafuci da addu'ar idan kedin Alkhairi ce gareni ki zama gatana ki zama mallakina bantaba furtawa wani burina a kanki ba na fawwalawa ubangiji na yarda duk abinda yayi daidai ne so Kuma sama taka cikin lkcn da ban tsammata ba kiran Mai Martaba ya shigomin yana fadamin na tanadi sadaki a hannuna daga dubu hamsin zuwa abinda Allah ya horemin nazo masallacin Fada yana nemana bansan meye zai faru ba hakanan na tafi Ina zuwa naga dogare sun budamin na shiga kamar yanda baa nemi izininki ba nima baa nemi nawa ba wlh kudin aljihuna kawai Mai Martaba ya karba dubu tamanin yabada umarnin a daura nidai na nemi guri na zauna Ina jiran naji auren waye zaa daura kawai naji ance yace shi a matsayin waliyinki ya bada aurenki gareni akan sadaki naira dubu tamanin bisa sharadin zanyi miki lefe kamar yanda al'ada ta tsara"

Shiru yayi yana mayar da numfashi sannan yaci gaba da cewa to meye laifina cikin lamarin nan Meenah?" A qufule ta dago tace “meyesa bakace bakaso ba?" Murmushi yayi yace “ko bake bace zan karba balle Kuma ya kasance dadaddiyar addu'ata ce ubangiji ya amsamin tare da tabbatarmin da ita kamar mafarki so ni a tsarina bana jayayya da duk abinda nasan ba ikona bane, Meenah a baya kema haka kike saboda kedin dalubata ce bansan meye ya sauyaki ba kinga inada maganganu da yawa da nakeso mu tattauna da zasu zame mana mafita Amma farko don girman Allah badon halin Abdulkareem kici abinci muyi sallah wlh ko Isha banyi ba saimu zauna"
Yanayin magiyar tasa tasata dole ta dauki Naman takai bakinta yaji dadin hakan sosai ya miqe ya shiga bathroom ya dauro alwala lkcn daya fito ta gama ya tattare ya fita da kayan ya dawo ya isheta a bayi tana brush da alwala, abin sallar ya shimfida yajasu sukayi Isha sukayi nafila raka'a biyu ya sanya hannunsa ya dafa kanta ta zame zata miqe ya miqe ya riqeta tare da matseta a jikin bango ya fara karanto addu'o'insa cikin larabcinsa me Sanyaya jiki sunkai 10 minutes a haka sannan ya saketa yana binta da kallo har zuwa lkcn bata daina dauke hawaye a idonta ba miqewa yayi ya dagata ya zare mata alqyabbar jikinta ya sake ware lafayar jikinta

tana tureshi tana komai ta durqushe da sauri yayi dariya wai kunyarsa takeji Meenah da Ikcn data fara period shine mutum na farko daya fara sani shima a lambu ya isheta tanata kuka wai taji ciwo daqyar ta fada masa yayi mata bayani.
Sautin dariyarsa ce tasata dagowa ya zauna tare da daganta gira yace “ashe kinajin kunyata Meenah yaushe kika farajin kunyana?" Harara ta galla masa yace “ko a jikina ki kwana kinayi yanzun dai Bari na barki ki kwanta ki huta abinki Saida safe" ficewa yayi yaja mata qofa tabisa da kallo tare da miqewa tayiwa dakin key ta haye gadon tayi kwanciyarta badon tayi bacci ba saidon tabawa zuciyarta damar tunanin abinda yake damunta.

Batasan Ikcn da bacci ya dauketa ba a sama ta rinqajin ana taba qofar ta miqe tana miqa tare da yin salati tace “wayene?" Cikin sanyin yanayinsa na dabi'a yace “kinyi sallah ne?" Bata bashi Amsa ba ta nufi bathroom ta watsa ruwa ta dauro alwala ta fito ta sanya doguwar riga ta tayar da sallar bayan ta idar tayi azkhar ta sake zubewa a gurin duk da ba wata hidima tayi a bikin ba tanajin gajiya a jikinta sosai, bacci ne ya sake dauketa bata farka ba sai 10:30pm shima din wayarta ce taji tana ring baqon layine ta Kara a kunnenta yace “barka da safiya ki fito kinyi baqi" Miqewa tayi tasa rigarta ta bude qofar ta fito Sarki ya rugo da mugun gudu ya rungumeta ta dagashi daqyar tana dariya yaron yace “Mom jiya nayita kuka daban ganki ba ashe gdan Uncle kika dawo nima na dawo nan" murmushi tayi tace “surutu dai kazo ka dameni ko" tsuke fuska yayi zaiyi kuka Kareem ya matso ya karbeshi yace “ba tun jiyan nace kazo mu taho ba kace kai bazaka tafi kabar Mom dinka ba to yanzun fah zaka taho ko shima aa?"  Da sauri ya daga kai yace “eh" Mom dake tsaye tayi dariya tace “aikam baka isaba yaro muna tare aurena dakai mutu ka raba" kuka ya saka Yana cewa “nin...Ni Mom banasonki kinmin tsufa ni gurin Mom dina da uncle zan dawo"

Dariya sukayi dukkansu ta nemi guri ta zauna Hamida tace “jikin yayi sauqi kenan tunda na tafi nakasa sukuni dake na kwana a raina" sunkuyar dakai tayi ya miqe yace Mom me zaa kawo muku gdan namu bai gama tsaruwa ba Hajiyan sai yanzu ta fito" kiransa Mom tayi tace “kazo kayi zamanka bama buqatar komai tun jiya da sukaje suka sanar dani halin da ake ciki na kasa sukuni shiyasa nazo naganku yanayin Alhmdllh komai zai wucce insha Allahu Meenah hqr zakiyi da abinda Allah ya hukunta, Aminatuh nice na haifi Rasheed Amma bazanyi shaidarsa kamar yanda zanbada shaida akan Kareem ba kin samu miji na nunawa saa daya tamkar da dubu idan kin kwantar da hankalinki insha Allahu komai zaizo qarshe ita rayuwa kowa da irin tasa jarrabawar Babu me taya wani dakon kayan da ubangiji ya qulla masa dole shine zaiyi dakon kayansa rabon dake tsakaninku me qarfine Allah ne kawai yasan adadinsa saboda haka kuyi hqr da jarrabawarku"
Kallon kallo sukeyi kowa da abinda keyi masa yawo a ransa Mom ta miqe tace “Inason mgn dake Meenah miqewa tayi tabita suka haura saman dakin baccinta suka shiga Mom ta zauna a

gefen gadon ta kama kunnenta tace “ki kiyayi shiga haqqin Kareem kawaicinsa da kararsa ta game kowa zai iya zubanki ido akan duk abinda yaga baki da raayi koda kuwa shi zai cutu hqrnsa abin jinjinawa ne shiyasa yake wahala idan ciwo ya ganshi don Allah kada ki zama silar wargatsa masa rayuwa kinji"

Kwantar da kanta tayi a cinyar Mom tana shassheqar kuka ta dauko wasu turaruka masu qamshin gaske na humra da na wuta tace muje a jerasu a show glass din fita sukayi suka jera ta fito da wani garin magani ta dauko danyen nonon raqumi ta barbada a ciki ta miqa mata tace “shine yayi saura da jiya kikaqi sha duk yanda kike tunanin fitinar Rasheed Kareem yafisa saboda akan hakan har so akayi a raba aurensa da Zahrah kwanakinsa bai qare ba yanzu Kuma gashi zaki zauna ke daya da sunyi hqr ma sun barta ta dawo da kin samu sauqin wani abun don Allah banda rowa Meenah shidai abinnan in kin hanashi ma ba ado zakiyi dashi ba Kuma ba kwanaki zaa qara masa ba idan wa'adinki yayi shima nasa yayi please a kula don Allah" sosai Mom ta rinqa bata shawari a fakaice saida taga ta dan sake sannan sukayi musu sallama suka tafi shima ya fice a gdan ta shiga bathroom tana wanka ta jiyo wayarta tana ring batabi takanta ba Saida ta gama shirinta tsaf sannan ta dauka number Ya'isha ce tabi suka gaisa tace “ya amarci jiya tsohuwar zuma ta motsa Ya Kareem an kwana ana zikiri" dariya mgnr tabata tace “waiku don Allah meye yasa kuka bawa abinnan muhimmaci ne haka"
Dariya Ya'isha tayi tace “mahadin rayuwa kenan gulma nazo yi miki" gyara zama tayi tace “aike dama indai anga kiranki to gulma ke cinki meye zaki fadamin" gwauron numfashi ta sauke tace “wato bantaba sanin Addah Abulle jahila bace sai jiya iliminta baya mata jagora kamar yanda yakeyiwa danta jiya Mai Martaba Yana zagaye bayan an taho kawoki ya nufi bayan gda ya isheta ita da Dada Hanne suna qusqus Dada Hanne nabata shawarar kawai tunda duk bugunsu yaqi tasiri akanki to su dora miki jinya yanda shi Kareem din zai gaji ya koreki sannan su sanyawa kowa qiyayyar ki a zuciyarsa ta yanda ko kin dawo gdannan Babu me karbarki Ina kaiki sun gama tattaunawar nan suna daga ido sukaga Mai Martaba da Ya Muntaz shine Mai Martaba yayi musu wani warning mai kama da daukar rai har yana fada musu daganan zuwa shekara goma idan kikayi ciwon kai saiya hanasu kwanciyar hankali ke sosai fah akayi rikici qarshe dai Addah Abulle tace da Mai Martaba tunda har ya nuna mata ita ba kowa bace akan danta to saidai ya zaba ko ita ko ke shikuma yace ya zabi zabin dansa aikuwa tace saiya saketa anso hanashi yaqi ji qarshe yayi mata daya me kyau sannan yace da Kareem yabashi damar rabuwa da Zahrah tunda abin nasu iskanci ne aikuwa tuni ya yankawa Zahrah ticket itama Kinga sai tafi samun sukunin zaman gida"

Zuciyar Imani ta Meenah duk sai jikinta yayi sanyi tace “Innanillahi wa Inna ilaihir raji'un Ya'isha wannan ba labarin badawa bane Allah fa shine ya halatta saki Amma bayasonsa nikam banji dadi ba idan Addah bataci arziqin komai ba yakamata taci na yayanta wlh wannan sakin bala'i

Mai Martaba ya qara jefani sannan ita Zahrah meye laifinta a ciki najifa ance iyayenta ne suka dauketa bataso tanason mijinta Kuma ko jiya da yazo dakina naga ta kikkirashi bai dagaba haba don girman Allah wannan ba adalci bane bai kamata ba"
Tabe baki Ya'isha tayi tace “saiki fada mawa Mai Martaban tunda kinfishi hangen nesa nikam naji dadin hakan ko banza sayi hankali susan ba ko Ina ake shimfida a zauna ba" kashe wayar tayi ta zabga tagumi wannan wacce irin masifa ce daga wannan sai wannan?
Bataji tsayuwar motarsa ba saiji tayi ya zare hannunta a kuncinta ya tsugunna a gabanta ya shafa habarta ya dago kanta taja numfashi tace “Hasbunallahu wa ni'imal wakil" Babu alamun bacin rai a tattare dashi yace “meye kuma?" Kafin ya rufe bakinsa yaga ta balle da kuka tayo qasa ta dora hannunta a cinyarsa gwiwarta na gugar nasa tace “kayimin wannan alfarmar ko ita daya ce a rayuwa don Allah Ya Kareem" da rashin fahimta ya dubeta tayi qasa da kanta tace “ka dawo da matarka dakinta domin Allah.

Miqewa yayi yace “ok kinyi sallar Isha?" Girgiza masa kai tayi yace “ki dafamin coffee ki kawomin dakina" ficewa yayi daga dakin ta bishi da kallo wani takaici ya tokareta waishi miji gashi babu damar yin musu yau izzar yakeji sosai batada zabi sai nufar kitchen din da tayi ta fara hada masa coffee din ta gama ta nufi dakinta tayi wanka ta Sanya kayan baccinta ta zura hijjab ta nufi dakin nasa ta qwanqwasa yabata izinin shiga ta bude ta shiga gabanta na faduwa ta kawar dakai tunda take bata taba ganinsa a tube ba sai yau cikar zatinsa kawai abin ka tsaya ka nazarta ne qirarsa ta hutun gaske fatarsa lufluf su ta lura kamar sign na Fam dinsu ne gargasar jiki daga mazansu har matansu.
Sunkuyawa tayi ta aje masa ta miqe zata fice ya Kira sunanta ya nuna mata guri ta zauna Saida ya gama abinda yakeyi sannan ya miqe ya nufi wardrobe ya dauki riga yasa yajasu sukayi sallar ya dauki coffee din yanasha Yana kallonta ita Kuma na kallon qasa ganin yanda duk ta takura yasashi cewa “jeki Saida safe" kamar me jiran umarni ta miqe tayi zuruf ta fice ya girgiza kai yana murmushi yace “Meenah kenan"

Ya jima zaune Yana tunanin hanyar da zaibi ya samo kanta bai kwanta ba sai 12:00am koda ya kwanta din baiyi bacci ba yanason kasancewa da matarsa Yana tsoron takurawa rayuwarta ko kadan baison shiga rayuwar dan' Adam balle Meenah da take da muhimmaci cikin rayuwarsa hakanan ya kwana Yana juyi shikam bacci me sunan bacci baiyishi ba da safe ta rigasa fitowa ta gyara part din nata ta sauka qasa ta gyara ta koma ciki tayi kwanciyarta fitowa yayi cikin shirinsa na fita yaga ta gyara ko Ina ya girgiza kai ya bude dakin nata tana kwance tana chat ta kallesa ta kawar dakai yace mata “barka da safiya" aje wayar tayi ta miqe tace “ina kwana" shafa sumarsa yayi yace “na tashi Ify Visa dinmu zan karbo gobe da safe zamu tafi nayima Sarki passport Mai Martaba ya hanani shi bansan meye yasa ba" itadai batace masa komai ba ya miqe yace “kina burgeni salonki yana sanyani nishadi nabarki kiyi iyakar abinda zaki iya kafin

ki shigo hannuna"
Ficewa yayi ta tabe baki ta koma tayi kwance abinta bata tashi ba sai azahar da yunwa ta fafaketa ta shiga kitchen ta samawa kanta abinci ta dawo ta zauna a falon qasa tana zaune taji an bude qofar an shigo ta daga kanta suka hada idanu da Amrah da Zahrah ta miqe tana cewa dasu “Lahh Amrah sannunku da zuwa ku iso mana" wani mugun kallo suka watsa mata Zahrah tace “tun Ranar dana fara ganinki matsayin tsohuwar budurwar mijina naji zuciyata bata karbeki ba ashe kedin masifa ce Kuma bala'i cikin rayuwata Aminah kin kashemin Zainab nikuma nayi alqawarin kashe taki rayuwar sai kinyi nadamar shigo da kanki cikin rayuwar gidana"..........…..

Juhud is not free read... regular 300 VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane kada ki biya 300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/9, 7:14 PM] Oum Hairan: Sun jima suna zazzaga mata rashin mutumci banda kallonsu da hawaye Babu abinda takeyi ita qwarin gwiwar ayi mata ta rama ma ba ko yaushe takedashi ba tana tsaye suka juya suka fice Amrah tana cewa banza liqaqqiya ai baki fara kuka ba tunda kika nace Saida kika auri yayanmu muna murna Allah yarabamu da qaya ashe kina manne zaki gane bakida wayo shashasha dake kawai" suna fita ta koma ta zauna ta zuba uban tagumi tana kukanta me cin rai bata ganin laifinsu kanta take dorawa laifi data maqale musu da tayi wani yunquri na samawa kanta yanci da yanzu ba wannan zancen akeyi ba itadai batasan tsayin lkcn data bata ba kawai dai taji tsayuwar motarsa ne ta miqe ta dauke abincin data faraci dazun ta nufi kitchen din ya shigo yabi bayanta da kallo bata juyo ba hakanan yaji ransa bai kwanta da shirun nata a kitchen ba yabi bayanta.
Tsaye ya tarar da ita ta kifa kanta a cabinet tanata kukanta me karya zuciya gabansa ya fadi ya fita yabarta qlau ya dawo ya tarar da ita cikin damuwa, matsawa yayi bayanta ya hade tazarar dake tsakaninsu qamshin turarensa ya daki hancinta taja ajiyar zuciya ya sanya hannunsa biyu ya dagota ya juyota ta sunkuyar da kanta ya matsa sosai kanta ya hade da qirjinsa yaja numfashi ya dafa kanta yace “meye ya faru bayan fitata naji a jikina wani yazo gdannan"

dagowa tayi ta dubeshi ko fushi Kareem yake fuskarsa a washe take yace “fadamin waye don Allah" kawar dakai tayi ta tureshi ta juya zata fita ya riqo hannunta ya janyota ta shige qirjinsa ya Sanya hannunsa ya matseta Yana sauke ajiyar zuciya me sanyi yace “kiyi hqr don Allah duk da kinqi fadamin meye ya kawo kukan"

Sake janyewa tayi zata bar gurin ya riqota ya dagata cak bai direta ko inaba sai dakinsa ya sauketa a gadon ya kulle qofar ya shige bathroom ya jima ya fito daure da towel yana tsane jikinsa har zuwa lkcn kanta na qasa tana wasa da yatsunta bayan ya gama shiryawa ya zauna a gefenta ya riqo hannunta Yana qarewa lallen hannunta kallo yace “yayimin kyau sosai am su Amrah da sukazo Basu bar miki saqo kibani ba?" Girgiza kai tayi yaja numfashi yace “ita dawa sukazo?" Cikin rawar murya tace “da Zahrah" nandanan annurin fuskarsa ya dauke yace “ok sai sukace miki me da har yasaki kuka?" Kallonsa tayi da idanunta da suka kada sukayi jawur yace “uhum inajinki" kawar dakai tayi yasan bazatace komai ba ya dauki wayarsa ya fice batasan me yayi ba ya dawo tana zaune inda yabarta yace “kiyi hqr komai zai wucce insha Allahu"
Ganin taqi daina tsiyayar hawayen yasashi kashe wutar dakin ya nufota gabanta ya yanke ya Fadi ta miqe da sauri taja baya ya tsaya tare dayin murmushi yace “kina tsoron mijinki akan me?" Bata ganinsa sosai hakan yabashi damar cafkarta ya cillata gadon ta miqe yabita da sauri ya danneta ya dora harshensa a kuncinta yana tsotse hawayen nata sanyi da qamshin iskar bakinsa na saukar mata da wata kasala me qarfi shikuma yaci gaba da yawo ds harshensa tsakanin kuncinta da wuyanta gabadaya ya saukar mata da wani yanayin wanda bata tanajin irinsa ba ta lumshe idonta tana sauke numfashi a jere hakan yasashi fahimtar rauninta ashema sauqin kamuwa gareta ya tsaya Yana wahalar da kansa.

Saida ya sake kashenta jiki sannan ya kamo bakinta ya hade da nasa yana tsotsar lips dinta da salo me kwantar da hankali a wannan yanayin ya mantar da ita komai daki daki ya rinqa binta harya isar da hannunsa ga qirjinta tayi saurin riqe hannunsa ya dago kansa dake tsakanin qirjinnata cikin muryarsa me sanyi data hade da kasala yace “na daina bakyaso?" Da sauri ta daga masa hannu yayi ajiyar zuciya tare da janyewa ya koma gefe ya kwanta yana matse cinyoyinsa tare da lumshe idonsa yayi alqawarin iya wahalar da zaisha bazai takurata ba yafiso ta kawo masa kanta ta yanda bazataji ya wahal da ita ba tunda yasan kansa yana jinjina haduwarsu, ji yayi ta shige jikinsa ta Kira sunansa da wata murya data sanya tsigar jikinsa miqewa gabadaya ta rikice jikinta sai rawa yakeyi ita kanta yanayin yabata tsoro bata taba rinskar kanta a mugun feeling irin na yau ba ji takeyi kamar bazata iya kaiwa gobe ba indai baa sosata ba bai zataba bai tsammata ba yaji harshenta a saman nipples dinsa yaja wata wawuyar ajiyar zuciya ya dafe kanta yace “ahhhhh Meenah!!!"
Harshenta ta rinqa karkadawa a saman nipples dinsa Yana sauke numfashi tare da sakin ajiyar

zuciya Yana matseta ta sake shigewa jikinsa a hankali ta janye tare da dora kanta a qirjinsa tana shafa gashin dake kwance tace “bamuyi sallar Isha ba....." kulle mata baki yayi da nasa yana Shan yawunta yana sakin nishi jikinsa na rawa yace “kin riga kin canzamin move bazan iya komi ba yanzu Meenah ki barni nasha daga gareki zanji dadi zanyi alfahari da hakan kinji don Allah kice kin amince bana burin yimiki dole" kawar da kanta tayi  ya janye jikinsa ya miqe yana layi ya nufi bayi baikai ga qarasawa ba ya zauna saman bedside drower yana mayar da numfashi daqyar shi kadai yasan yanayin da yakeji mararsa ds twins dinsa ciwo sukeyi masa sosai yanason ya fitar da ruwan daya taru masa Meenah taqi bashi dama bangaren zuciyarsa daya na bashi shawarar ya karbi haqqinsa kota wanne hali wani sashin na cewa dashi aa yabita a hankali.

Miqewa yayi Yana Shirin shiga bathroom din yaji ta riqeshi ta baya yaja numfashi ya juyo ya dago kanta idanunta suka kawo ruwa tace “ni....sai nakega kamar bai dace....." Hannunsa ya dora saman bakinta yace “meye bai dace ba Meenah kina nufin kinfi ubangiji sanin abinda ya dace?" Saurin girgiza masa kai tayi yace “to shine ya halattamin ke Kuma yabani damar nayi komi dake batare da komai ba Meenah shi lamarin aure da gadon mamaci Allah ne ya tsara abinsa dakansa koda Rasheed yana tsakankaninmu yana rayuwa idan Allah ya qarar da rabonsa a jikinki hakanan ko yanaso ko baiso zaiji baya buqatar zama dake koda laifi ko babu ya rabu dake ni Kuma na dauka saboda Allah ya hukunta Mana kedin ba matar mutum daya bace a cikinmu so banso don Allah ki daina qoqarin haramtamin abinda Allah ya halattamin ko zamanin samartaka bantabaci daga haramtacciyar itaciya ba"
Yana fadin haka ya juya ya shige bathroom din a bakin qofar ya tsaya yace “bazan hanaki abinda kikayi niyya ba bakuma zanyi miki dole ba Amma kisani duk da cewa tun aihuwata an haifeni da sign na ciwon zuciya bata taba qarfin da take neman kaini Ramin kabari ba saita dalilinki Aminah idan kika wayi gari babuni kada ki zargi kowa kece abar zargi" turo qofar yayi ta tura da qarfi tana wani irin kuka me kashe jiki ta durqushe a gabansa tace “kayi amfani da qarfinka ka qwaci haqqinka yafimin sauqi dakace kabarni da Allah Ya Kareem da wanne zanji da ciwon rashin galihu koda na sharrin Maitar da aka liqamin ko Kuma da batan mij......"

Rufe mata baki yayi jikinsa na rawa yace “karki qara Aminah karki qara hada kanki dashi keba matarsa bace yanzun kada ki Kuma danganta kanki da wani namiji madamar bani bane" yanda ya harqitse mata lkc guda abin ya bata tsoro bata taba ganinsa cikin wannan yanayin ba ashe akwai abinda yake sosa zuciyarsa haka lallai kishinsa babba ne, kama hannunta yayi ya fitar da ita daga bayin ya koma ya watsa ruwan daqyar ya gama saboda zafin da zuciyarsa takeyi masa ya fito har lkcn tana tsaye a inda ya barta ya kalleta yace kije kiyi wanka zakiji dadi sosai" batayi masa musu ba ta nufi qofar fita daga dakin yabita da kallo harta fice tana fita tayi wankan tayi sallar Isha tayi shafa'i da wuturi ta zauna tana lazumi sai 11:00pm ta miqe tasa kayan baccinta

ta shafe jikinta da turaruka masu qamshin gaske ta kwanta.

Hakanan takejin zuciyarta bata aminta da rashin jin motsinsa ba ta miqe ta fito daga dakin nata taja baya da sauri ganinsa tsaye a falon yana kaiwa da komowa cikin yanayi na mutuwar jiki ta matsa bayansa batare da yasan ta fito ba tace “Ya Kareem" tsayawa yayi batare daya juyo ba ta zagaya gabansa yayi saurin sanya hannunsa ya goge hawayen daya tsiyayo masa ta zaro ido waje tace “mene yayi zafi?" Murmushi ya qaqalo yayi mata ya lakace mata kunci yace “meye ya hanaki bacci?" Rausayar dakai tayi tace “kai meye ya hanaka?" Iska ya furzar yace “Feeling Meenah" kallonsa tayi da sauri ya lumshe idonsa tare da budewa a kanta yace “kwanaki 34 ga lafiyayyen namiji kamata babu mace ba kwanakine masu sauqi ba ko a baya lkcn da baki gama sanin wayece kedin ba kinsha tambayata meyesa nake yawan azumi nasha fada miki zaki fahimci hakan daga ranar da liman ya saqala igiyar aure tsakanina dake Aminah Ina wahaltuwa haqiqa cikin kwanakin nan kinqi tausayamin"

Daga hannunta tayi sama idanunta a lumshe tace “nabaka dama Ya Kareem kayi duk abinda kakeso dani......" Wata runguma yayi mata data sanya numfashinta daukewa yana kissing dinta ta ko Ina yace “na gde My Soul Allah yayi miki albarka" bai barta ta gama jin yanayin ba taji ya sanya hannunsa ya zare mata rigar jikinta gabansu ya fadi lkc daya yakai hannu ya kama breast dinta yaja zuciya yana shafasu da yanayi na shauqi itadai bata bude idanunta ba Saida tajita a gado ashe dauketa yayi ya nufi bedroom dinsa da ita ya tsugunna a gabanta tana zaune yasake riqe qasan boobs dinta yana shafa nipples dinta da yatsunsa ta sauke ajiyar zuciya ta bude idanunta suka shiga cikin manyan idanunsa da suke koyaushe a lumshe kamar na mashayi idanunsa na cikin nata ya dora harshensa a boobs dinta yana lasar nipples dinta taja ajiyar zuciya yaci gaba da lasar nipples din tanajin yanayin na musamman musamman dake ba qaramin hadi akayi mata ba iyakar tsotsar da yakeyiwa boobs dinta ta rikitata jinta takeyi a wani baqon yanayi inda shikuma yabada qarfinsa wajen lasar breast dinta zuwa dokin wuyanta aikam tana karbar yanayi  matuqa tanajinsa ya kwantar da ita ya hauro samanta ya hade bakinsu Yana tura yatsansa cikin pant dinta daya jima da jiqewa jagab daga haka ya kai hannunsa ya kashe glub din dakin duhu yasani yowa baya sama$^2$ najishi Yana karanto addu'ar kusantar iyali can naji Meenah ta saki wata qara tana Kiran “wayyoh Ya Kareem kabi a hankali zakajimin ciwo wayyoh Allah na don Allah ka bari ni na gaji...." Bankumajin muryarta ba sai gurnaninsa da nishinsa dake tasowa sama$^2$

Wannan dare Meenah ta gane kurenta ta fahimci maza suna suka tara duk Wanda Allah ya hadaka dashi shine gwarzonka iyakar mitarta saida ta sallamawa Kareem don ta fahimci shima baji yakeba ba gani yakeba akan wannan harka duk abinda takeji ana fada akansa qin aminta takeyi ganinsa bashida zafin yanayi yasa ta rainashi ashe ba anan takeba sai takega Rasheed ma baya mata komai, daya qyaleta bacci ya fada daukarta zataji ya qara shigewa jikinta tana

bude baki zatayi mgn zai hade bakinsu ya kama cewa “double sorry My Soul" itadai a wannan dare har suma tayi saboda wahala Allah da yayita bata jurar nacin sex itakuma qaddararta kenan dukkansu kamar anyi musu tsarki da garera basa gajiya da sex kamar wadanda aka dafawa Naman Ayu sukaci.
Bayan ya gama bidirinsa ya tashi ya shiga bathroom ya hada mata ruwa me dumi yazo ya sunkuceta kamar wata jaririya yasata a ruwan ta kuwa saka masa kuka tace “wayyoh Allah wayyoh wayyoh Ya Kareem gurin ya kumbura zafi yakemin don Allah kabarni tausaya mata yakeyi sosai da alama bata saba da wannan yanayin ba koda yake ita mace roba ce a hankali zata saba tunda Allah ya hadata da maza. Daqyar ta Bari ya gasata ta miqe tana tattale qafa ta fita dakin ta dauki rigarta tasa tana duban agogo 6:15am gabanta ya fadi wato kwana ma yayi Yana qwaqularta wannan kwai jarababbe tab aikuwa indai haka yake to itama zatabi sahun Zahrah don wlh tsaf zata gudu kwana till down Babu bacci, fitowa yayi yajasu sallah daqyar take motsa qafafunta sukayi sallar ta gaisheshi a daqile yayi murmushi tare da shafa kansa ya sanya hannunsa ya dago fuskata yace “ayyah sannu fah amarya ta to ya kikaji mijin naki baikai ba ko yafi yanda kike tunani?" Ture hannunsa tayi tace “banaso ka riqe kayanka bazan qara yarda ba kai mugune Allah......"

Dariya ta bashi sosai yace “ke Kuma matar mugu ko raguwa kawai a haka kamar zakiyi juriya ashe bilhu ce" shiru tayi masa ya miqe yace “ki kwanta ki huta zanje na dawo 11:30am zamu tashi naso muje muyiwa su Mom sallama so na fahimci har yanzu gdan a hargitse yake shiyasa bance ki shirya ba nidai zan shiga kekuwa sai wataran idan munada yawan kwana" kallonsa tayi tanabin gado ya cire doguwar rigar ya fita ashe kitchen ya shiga ya hado mata shayi me kauri da cake ya dawo yace “kafin bacci ki fara Shan wannan zakifi jin dadinsa"
Karba tayi tanasha yana bata cake din Saida yaga ta shanye yayi hamdala ya dafa cikinsa yace “har naji na qoshi" yanda yayi mgnr dole yasata murmushi yace “wow mamaki ban zataba kinfi kowacce mace a duniya kyau da murmushi My Heart" lumshe idonta tayi yace “ko bacci kikeyi kinafin kowacce mace kyau kinsan meye nakeson fada miki nakejin kunya?" Bude idonta tayi ya matso da fuskarsa daidai nata Yana lasar lips dinsa yace “kinfi kowacce mace a duniya dadi ni'imarki sadidan ce wani malami yana cewa wai duk namijin yace yaci mata qarya yake  a fada masa baici mataba mata suna aljanna hurul'aynee so nikam na fada tabbas nima naci mace fiye da kowacce mace....."
Sosai kalamansa suka sanyata a kunya ta kasa bude ido ya hura mata iskar bakinsa yace “kiyi bacci cikin aminci tare da hasaso Mana sabuwar rayuwar da zamu fara Ina fatan nayi ajiyar qannen Sarki a daren jiya My Soul kinsan fah nidin jarumi ne Saida Inna bada aqi karba Amma inabada ruwa iyakar gona......"

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane kada ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/10, 8:10 PM] Oum Hairan: Lumshe ido Juhud tayi kalaman Kareem sun girmewa tunaninta Allah Allah takeyi ya fita ta samu damar tunani saboda tafi jin dadin yinsa fiye da komai, so shima ganin bazata bashi amsaba yasashi miqewa yace “ok na fita" a ciki tace "a dawo Ify" ya Amsa da Amin ya fice ta sake gyara kwanciyarta Babu wani bata lkc bacci ya dauketa bataji dawowarsa ba saiji tayi Yana shafa mararta taja numfashi tare dayin miqa ta bude idanunta akansa yayi mata murmushi yace “kinaso ki makarar damu shikuma jirgi baya jiran kowa" Miqewa tayi tana gyara hijjab dinta ta shiga bathroom ta sakarma kanta ruwa ta fito ya gama hade musu kayansu ya fice da akwatunan guda biyu daya Mom ce tabashi tace yatafi mata dashi daya Kuma kayanta ne da yasan zata buqata shikam banda qaramar jaka ta hannu Babu abinda ya dauka suka fito Lado drivern Mai martaba shine ya daukesu zuwa Kano daga Kano 2:00pm suka daga zuwa Saudi Arabia bacci ne ya sake dauketa batasan tsayin tafiyar da sukayi ba Saida suka sauka a Madina tajishi Yana yawo da hannunsa cikin rigarta ta bude idanunta ya shafa fuskarta yace “Allah ya saukemu Ify sauranmu masauki" janyewa tayi a jikinsa ya tashi itama ta tashi yana riqe da hannunta suka fito har motar University of Madina tajasu suka tafi tanabin garin da kallo tanajin wani nishadi a zuciyarta hawaye ya zubo mata yau gata a garin masoyinta dan gatan Allah zababbensa Muhammadur Rasulillah (S.A.W) cikin zuciyarta ta qudurce zata yawaita yima Allah tasbihi da yimasa magiya ya bayyana mata Baffa'am dinta a raye ko a mace ko zuciyarta ta samu sanyi da salama duk da yake cewa zuciyarta bata taba aminta Baffa'am dinta ya mutu ba Amma yanayin yanda zamani ya zama batan Dan Adam Yana wahala to meye zai batar dashi tsayin lkc me tsaho haka?

Tuni zuciyarta tayi raunin da batasan sanda kukanta ya qarfafa ba Saida taji yatsan Kareem a kuncinta yana share mata Yana cewa “please stop crying My Heart" qoqarin hadiye kukan takeyi taga sun shiga cikin University din sun dauki tafiya me tsayi sannan suka Isa wasu benaye anan drivern yayi parking sukayi musabaha da Kareem wasu baqaqen fata suka nufosu da sauri suna dariya suna Dr Kareem Mahfuz barka da dawowa" cikin larabci suke maganar

tana tsinta kadan² sune suka debi kayansu suka shigar musu dasu bangarensu bayan ya gama gaisawa da mutane ya gabatar musu da Juhud a matsayin matarsa mafi soyuwa a ransa larabawan da Baqaqenmu sunata yimusu fatan Alkhairi ya kama hannunta suka haura lifter din a hawa na biyar sashinsa yake ya sanya remote control din door din ya bude ya shiga da kayan da dalubansa suka hauro musu dashi ta tsaya tana qarewa falon kallo,
Fasali taja a haka ta waje saita Raina yanayin girman gurin data shigo Kuma saita Raina kanta falone babba da aka kashe manyar Riyaloli wajen shiryasa ta ko'inansa babu qarya an shiryawa rayuwar duniya a cikinsa. Wani daki ya bude shi kansa dakin girmansa abin a jinjina ne Babu komi a cikinsa daga gado sai wardrobe sai madubi bango guda kusan kowacce kusurwa ka nufa a dakin kana kallon kanka a madubin wannan abu yabata mamaki bata qara tsinkewa da lamarin ba Saida taga ya matsa wani dan madanni a jikin bango Wai kamar rufar ido taga wani labule ya sauko ya rufe wannan bango da madubin yake.
Numfashi ta sauke a ranta tace "tsarki ya tabbata ga ubangijin daya halicci duniya da abubuwan alatunta mabambata Allah kayi dadin tsira ga fiyayyen halittunka zababbenka badadinka Annabi Muhammad (S.A.W)" da wannan tasbihin taji ya saqalota ta baya dumin da taji a jikinta ne yasa gabanta faduwa ta zubawa dantsensa ido dake cike da qasumba yayi qasa da kansa ya sauke mata wani hot kiss a dokin wuyanta tare da zame mayafin dake jikinta Yana tura hancinsa cikin wuyanta, hakan taji wani tsoro ya dirar mata yanda taji jikinsa ya dauki dumi yana sauke numfashi ba daidai dana kowa ba yana yawo da hannunsa a sassa na jikinta sosai taji tana tsoronsa ta janye tare da zama gefen gadon ya shafa mararsa ya zauna kan bed drower ya zubanta ido miqewa tayi ta nufi wata qofa da zuciyarta ta bata bathroom ne ta turo qofar ta cire kayanta ta fara wanka taji an bude an shigo Saida taji wani rass bai damu da yanda yaga ta tsaya dinba ya zare boxes din jikinsa shima ya shiga cikin komin wankan ya hade jikinsa da nata ta aje numfashi daqyar saboda yanda ya sakar mata nauyinsa ya karyar dakai yace "ana bina bashin salloli biyu magrib da Isha Kuma inajin yunwa nasan kema kinaji Amma bazan iya kaisu ba saina fitar da abinda ya hanani sakat tun a Kano My Heart please karkice aa"

Lumshe idonta tayi qirjinta na lugude wannan masifa da yawa take daga dirarsu ko hutawa batayi ba zai raraketa ga baqar yunwa da takeji itakam taga boni cikin rayuwanta, bai bata wani damar zabi ba yafarabin kusurwa ta jikinta yana kissing inda zai tsotsa yana tsotsewa yana fusgo numfashi daqyar itadai duk a firgice take karonsu na Daren jiya ya razanata shidin dabanne bayada sauqi koda take yima Rasheed iskanci tana cewa dashi jarababbe ashe ga inda jarabar takenan.
Rintse idanunta tayi da qarfi lkcn daya dora bakinsa saman boobs dinta suma zafi sukeyi mata saboda matsa da tsotsar da sukasha jiya hakanan yaci gaba da luguiguitasu yana ciza kan a hankali da wannan ya samu ya shigar da ita ya dagata suka koma dakin ya sata a corner ya hadata da aiki dake yasan akwai gajiya a tare da ita ga yunwa yasa baija sun jima ba ya tsiyayar da abinda yakeson fitarwa ya rungumeta yanata tsotse kunnenta tare da sanya mata albarka itadai qasanta sai zafi yakeyi mata ta janye ta koma bayin ta hada ruwan dumi ta shiga

tana lumshe ido hawaye nabinta sosai takejin radadi ita ba budurwa ba Amma gurzar da Kareem yakeyi mata tafi budurwa azabtuwa hakanan ta tsaftace jikinta ta fito daure da towel idanunsa na kanta ya dauki wayarsa ya kira jami'an kula da Da'ami na sashin nasu ya sanar dasu suna buqatar abinci ya zayyana kaloli ya miqe shima ya shiga yayi wanka yazo yajasu sallah sukayi magrib kafin su tada Isha sukaji qararrawar part din na kuwwa ya bude ya karba ya kulle qofar suka Ida sallar sannan suka dirawa abincin sosai takejin yunwa saboda haka taci abincin babu qarya ta Kora da Madara ta miqe a qasa tana miqa Yana kallonta ta gefen ido.

Itadai daga wannan kwanciyar baccin gajiya ya dauketa bata farka ba sai cikin dare da sanyin dare ya busa taji yana lalubarta taso qin sauraronsa Amma bata isaba shi gabadayansa wayo gareshi da hikima yake shigewa jikinta bata Ankara sai taji ya fara lalubar gurare masu muhimmaci a jikinta tanajinsa Yana sucking dinta tare da fingering bata dorar da dadin sai wuya saboda ya gama sissike gurin jinya yake buqata shikam ruwan da take fitarwa yafi masa komai dadi yana lasa Yana tura harshensa har Saida yaji tana neman release sannan ya janye ya maye gurbin harshensa da dick dinsa ta qanqameshi tana ajiyar zuciya shima ajiyar zuciyar yakeyi yaji gaba da motsa kansa a nutse tana nishi da gaske dadinsa takeji sosai yakan ya qara masa qaimi ya rinqa binta duk ta inda yasan zataji dadin aikuwa ta rinqa qanqameshi tana surutai masu nuna rashin hayyaci ita kanta batasan mi take cewa ba Saida taji ya tsaya cak da abinda yakeyi taja wata wawuyar ajiyar zuciya ta shafa kansa cikin mutuwar jiki tace “Baffa'am Inasonka har qarshen numfashina......"
Zare jikinsa yayi a sanyaye ya koma gefe ya kwanta ya juya mata baya jikinsa sai rawa yakeyi, sai yanzu ta fahimci barnar da tayi ta zubawa bayansa idanu gabadaya ilahirin jikinsa jijjiga yakeyi gabanta ya Fadi ta miqe zaune da sauri ta Sanya hannunta da nufin juyoshi ya janye mata hannun cikin rawar murya yace “ki barni don Allah Aminah ki barni ki kwanta Saida saf...."
Kakarin amai ya fara ya miqe da sauri Yana layi ya nufi bathroom ta diro a gadon ta wawuri hijjab dinta tasa tabisa da gudu taja baya tare da dora hannu akanta ta saki wata qara tace “na shiga uku Ya Kareem aman jini meye yayi zafi....."

Kafin ta rufe bakinta ya Fadi kasa sumamme ta nufeshi a guje jikinta na qyarma ta fada kirjinsa ta rushe da kuka tanajin yanda zuciyarsa ke harbawa da mugun qarfi ta Kuma rushewa da kuka tana cewa don Allah kada ka mutu ka taimakeni Ya Kareem meye nayi maka da zafi haka wlh bansan ya akayi ba ba laifina bane laifin zuciyata ne......" Numfashin da taji yajane yasata janyewa da sauri ta miqe jikinta na tsuma ta zuba masa ido tana tsiyayar da qwallah itakam tana ganin bala'i a rayuwarta daga wannan sai wannan shikuma haka yake daga mgn sai Aman jini sai suma?
Wayarsa taji ta fara ruri ta fita da sauri number Saudi tagani taja ajiyar zuciya tana kokawa da

wayar wajen amsa kiran ta Kara a kunnenta hamdala tayi Ikcn da taji ance “bakada kirki mutumin zaka dawo baka fadamin ba ashe da amarya ka ta....." Katseshi tayi da gunjin kukanta tace “ka taimakeni kazo mijina zai mutu...." “wht?" Ya fada da qarfi tare da cewa “ganinan" daga haka ya kashe wayar ta koma ta sake tsugunnawa tana danna qirjinsa tana share masa kumfar dake fita a bakinsa da tissue taji an taba qofar ta miqe har tana fasa yatsa da qofar bayin ta bude qofar Dr Khazeem ya shigo da sauri yana dubanta yana cewa “inane yake" bathroom din ta nuna masa ya nufa da gudu ya cicciboshi daqyar sukayi waje itama ta zura doguwar riga ko bra batasa ba ta rufansa baya.
Suna sauka a lifter ya sashi a mota suka nufi asibiti dake da ID card dinsa na aiki a cikin jami'ar nandanan suka rufar masa suka sassaqala masa na'urori don taimakon numfashinsa tare da wasu manyan Allurai, wannan Rana Juhud bata rintsaba a tsaye ta kwana tare da likitocin suna aikinsu tana binsu duk inda sukayi.

Hakana gari ya waye sunata safa da marwa daqyar da taimakon Allah suka samu ya fara numfasawa daidai ta sauke ajiyar zuciya ta zubansa ido gabadaya sai taji zuciyarta ta karye tausayinsa yana ratsa duk wata kusurwa ta jikinta a fili tace “wanne irin so kakemin Ya Kareem da kake neman rasa rayuwarka saboda ni bayan nidin na kasance ba kowa ba maras galihu? Don Allah ka rage kishina....." Tana mgnr ne hannunta na qirjinsa taji yaja numfashi ya daga hannunsa ya dora saman nata ya matse hannun nata idanunsa a lumshe taga hawaye na fita ta gefensu ta daga dayan hannun nata takai fuskarsa ta share masa hawayen masu zafi tace. “Zai zama azabtarwa a gareni zubar hawayenka Ya Kareem ka daina don Allah banaso" daga mata kai yayi ta sunkuyar da kanta daidai fuskarsa tace “are you sure?" Murmushi yayi mata ta dora dan qaramin bakinta a kuncinsa tace “I like you...." Bude idonsa yayi akan fuskarta ta sakar masa murmushi shima murmushin yayi ko bada gaske takeyi ba yaji dadi sosai aransa Kuma kalmar ta qara masa qarfi yaji ya fara warkewa.

Yunqurawa yayi zai tashi ta taimaka masa ya tashi zaune ta hada masa tea me kauri ta zauna tana bashi yanasha a nutse idanunsa nakanta Saida ya kawar dakai tace “ka qoshi?" Daganta kai yayi ta mirgina kai ta miqa masa cup din ta bude masa baki ya karbi cup din ya fara bata tanasha tana kallonsa duk ta sauke masa gajiya Saida taga hannunsa na rawa ta karba ta taimaka masa ya suka nufi bathroom ta hadansa ruwan wanka zata fita ya riqota duk da kunyarsa da takeji hakanan ta zage ta wankeshi tsaf ta dauki towel ta tsane masa jikinsa ta dauko mai lotion ta shafa masa a jikinsa tana shafa masa yana lumshe yanajin wani mugun feeling na bijiro masa yakai hannu ya saqalota qirjinta ya buga batason saka masa kokwanto akan kalaminta hakan yasa ta narke a jikinsa yana sunsunar jikinta Yana lumshe ido ta sanya harshenta ta kamo fatar kunnenta ta lasa yaji wani irin yanayi mai fitar da hayyaci ya ziyarceshi

ya maqaleta suka miqe suka zube a tsakiyar dakin suna tsotse juna, tunawa yayi ashefa baa gida suke ba ya janye yana gwama numfashi yace “mu koma masaukinmu" kallonsa tayi da idanunta da suke saukensa kasala tace “ai baka gama warwarewa ba" turo baki yayi ya shafa kansa kamar wani dan boy yace “ni nagaji danan mu tafi kawai" batada zabi daya wucce na kiran Dr Khazeem ta fada masa abinda yace, kamar yana kusa kuwa sai gashi suka fita tabisu a baya suna tafe Dr Khazeem Yana masa fadan Sanya damuwa a ransa ya juya ya dubi Juhud yace “tunda kasanni kasanni da ciwon zuciya Dr Khazeem kaga sila nan nasan ba sanadinta na kamu dashi ba tun Ina qarami aka tabbatar da inada sign nasa Amma ko tashi baitabayi ba Saida qaddarar soyayyarta tasakoni a gaba Dr Khazeem inason Aminah sonda bantaba yiwa wani abu ba a duniya idan zan rayu da ita cikin aminci inaji a jikina duniya zata iya mantawa da Dr Kareem Mahfuz yanada matsalar ciwon zuciya domin itace zuciyar tawa"

Jinjina kai Dr Khazeem yayi yace “to ai kanwa dai ta kar tsami Dr Kareem Aminah ta zama taka fah mallakinka ce" murmushi yayi me kama da yaqe yace “zadai ta zama inasonta tanason Yayana Rasheed wlh addu'ar Allah ya bayyana Rasheed kullum da koda yaushe Amma idan na tuna munyi tarayya akan son Abu daya sai naji zuciyata ta karye musamman da yake banine abinda mukeso yakeso ba yafini power a gurin" shiru yayi Yana mayar da numfashi ya dago idanunsa da suka kada sukayi jawur yace “kasan me Dr Khazeem inaji a jikina duk ranar da Rasheed ya bayyana ranar numfashina ya qare a duniya......"
Dukka suka kallesa da sauri musamman Meenah da taji wani dukan zuciya yayi murmushi yace “badaga Ni bane a baya na da bansan wace ke ba nasha wahala har likkafanina an dinka saboda ke Meenah ya kike tsammani idan yanzu ne?" Ta riga kowa bude motar ta kwasa da gudu ya biyota Yana dafe qirjinsa ta rigashi shiga masaukin ta fada saman bed ta rushe da kuka me ban tausayi tabbas tana cikin tsaka me wuya Allah ne kawai yasan meye zai faru gobensu, ji tayi ya kwanto jikinta yana hura mata iska a kunnenta yace “kiyi hqr abinda nasan zai faru ne Meenah na haska miki domin ki shirya inaji a jikina Rasheed zai bayyana bada jimawa ba domin bantabaji araina ya mutu ba nikuma daga ranar da aka daura aurena dake nake qirga sauran kwanakin rayuwata....." Rufensa baki tayi cikin kuka tace “ka daina Ya Kareem Allah bazaka mutu ba saboda ni........"

Juhud is not free read... regular 300 VIP 600 via👉🏽 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane ki biya 300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/11, 4:39 PM] Oum Hairan: Muryar Dr Khazeem ne yasasu miqewa ya fita sukayi sallama ya dawo dakin ya kwanta ta miqe ta nufi kitchen din bata samu komai ba sai ragowar Naman da sukaci jiya shi ta dumama ta sake hado masa tea ta dauko ta nufo dakin ta aje masa ta cire hijjab dinta ta zauna a qasa tace “kaci abinci saika samu qwarin jikinka"
Girgiza mata kai yayi tare da daga rigarsa ya sanya hannunsa cikin wandonsa ya bude bakinsa cikin muryarsa me sanyi yace “bana tare da yunwa kinsan matsala ta Meenah ita kadai nakeson kimin maganinta" sunkuyar da kanta tayi ya sauko ya dago kannata ta lumshe ido yayi kissing na lips dinta yace “kiyi hqr dani nasan na takura miki ko?" Girgiza masa kai tayi ya janyota ta kwanta a jikinsa ya matseta duk da firgicinta tayi masa rawar gani ya samu yanda yakeso. Rayuwa sukeyi me armashi cike da kulawa da tattali wa junansu musamman Kareem da kacokan lissafin rayuwarsa yake akan Juhud itanma fahimtara irin tasa matsalar yasa kan dolen dole ta yakicewa kanta bayyananniyar damuwa, ko tunani ta daina yarda tayi a gabansa yanzun nan saiya rikice mata rayuwarsu a qasa mai tsarki ta zame mata wata rayuwa da take bata nishadi tanajin Kareem a ranta fiye da tunani Amma har gobe takasa canza gurbin Rasheed kullum shine cikin tunaninta mafarkinta da dukkan wani motsinta hatta addu'arta ya kwashe kaso mafi rinjaye shidin bashi da tamka cikin rayuwarta bazatayi masa madadi ba.

Watansu biyar a Saudi aka dauki azumin watan Ramadhan a lkcn Juhud Ify tayi mata qaranci ita ba ma'abociyar bacci bace Amma baccinta yayi yawa Kareem shine ya fara lura da yanayinta suna kwance da dare ya janyota jikinsa Yana shafa mararta ta riqe hannunsa ya daganta gira ta turo baki tace “nikam Allah ya Kareem zaka sani guduwa waikai baka gajiya da abinga ne?"
Murmushi yayi ya zubanta ido Yana lasar lips dinsa yace “kintaba ganin inda mutum ya gaji da dadi ai kullum qari kake nema kinma san me?" Girgiza masa kai tayi ya shafa cikinta yace “baki tunanin komai game da sauyin yanayinki?" Dariya tayi tace “yanzu fah sai kace ciki ne dani ko?" Hade rai yayi kama kunnenta ya murde ta saki qara yayi dariya yace “wato kin mayar dani abin tsokanarki ko naga Sarki junior shekara daya da aurenki kika haifesa nikuma kina neman kaini biyu duk qoqarina" murmushi tayi tace “to abinda bazaka yima kanka ba Ya Kareem meye na damuwa kafa taba aihuwar nan balle kace tsoro kakeji" numfashi ya sauke yace “kawai inason naga yayanmu ne Meenah zanji dadi zanyi farin ciki sosai inasonki shiyasa nakeson zuri'a ta

wanzu tsakaninmu nasan ko bana raye bazan goge a mind dinki ba"
Shiru tayi masa ya kama kunkuminta yayi mata cakuli tayi dariya ta qanqameshi da haka bacci ya daukesu da asuba ya tashi taba jikinta kawai yayi yaji jikinta zafi zau ya tasheta tayi miqa yace “jikinki zafi" numfashi ta sauke tace “na kwana zazzabi Ya Kareem" wanka yayi itama tayi sukayi sallah suka fita asibiti suka shiga aka bata magunguna tare da yimata gwaje² labari me dadi ga Kareem abinda yake zargine itadai jikinta ya mutu batasan meye dalili ba babu farin ciki Babu baqi a ranta saima hawaye da batasan sanda ya zubo mata ba.

Tasbihi da taslimi yayima ubangiji Sarki daya me ikon zartar da komai a Ikcn da yaso ya juya gareta ganin yanda take sharar hawaye duk sai ta Sanyaya masa jiki ya kama hannunta suka tafi suna zuwa gda ya dubeta idanunsa sun kada sunyi jawur yace “bakyaso ko?" Girgiza kai tayi da sauri tace “ba haka ban...." Katseta yayi da cewa to mene?" Kuka ta saka ta fada jikinsa tace “babu fah kawai Ina jinjina girma da buwayar ubangiji Ya Kareem meye kayimin da zanqi jininka" ajiyar zuciya ya sauke yajata suka zube ya share mata hawayen yace “ki daina kina sani a tunani kinji" dagansa kai tayi yace “me zakici?" Kallonsa tayi tace “azumin fah" kallon magungunan yayi yace “ok idan bazaki iyaba ki hqr Allah yayi muku uzuri fah
Dagansa kai tayi yini sukayi yanata tattalinta da riritata wannan ciki Yana ganin boni komai yagani ya rakito mata kayan baby kuwa abin har yazama hauka abinda ya bata mamaki Mom ce kadai tasan da cikin har yakai watanni biyar a Ikcn ne Kuma wani baqon al'amari ya sakosu a gaba hakanan sai taga Kareem yayi tagumi ya tsunduma duniyar tunani idan ta tambayeshi dalili sai yace mata Babu komi Tasha zuwa ta tarar dashi Yana kuka a daki shi daya tambayar duniya sai yace mata Babu komi dole ta zubansa ido a dan ritsin ne Kuma ya kama rashin Ify sosai itadai Saida ta Kira Mai Martaba ta sanar dashi domin an bashi gado baisan waye akansa ba wani abin mamaki daya razana duniyarta ranar da Mai Martaba yazo tana tsaye jikin gadon da Kareem yake riqe da hannunsa tanayi masa addu'a taji sallamar Mai Martaba ta dago da sauri cak ta tsaya komanta ya tsaya hatta da numfashinta Ikcn da tayi arba da wanda yake takewa Mai Martaba baya cikin bugawar zuciya tace “Baffa'am!" Kallonta yakeyi da alamun rashin fahimta ta nufesa da sauri tana cewa “Ya Allah Mai Martaba yaushe akaga Baffa'am dina Amma aka boyemin meye yasa akayimin haka ashe akwai abinda zaa iya boyemin game da Baffana....."

Tana mgnr tana nufarsa shikam ya saki baki ne Yana kallonta zuciyarsa na wani irin bugawa da mugun qarfi qara waro idanunsa yakeyi yanason ya ganeta ya kasa tana Shirin kai hannunta jikinsa taji yace da Mai Martaba “mai Martaba itan wacece?!" Ba itaba shi kansa Mai Martaba Saida tambayar ta dakeshi ya dubeta yaga tayi mutuwar tsaye hawaye nabin kuncinta bakinta yana rawa alama ta magana takeson yi ta kasa kama hannun Meenah Mai Martaba yayi yace “ki nutsu Meenah Rasheed fah ba qalau yakeba duk duniya Babu wanda yake ganewa" zubawa

Mai Martaba ido tayi tace “meyesa aka boyemin bayyanarsa?" Murmushi Mai Martaba yayi yace “akwai hikima cikin hakan yanzun ma banso kikasan da bayyanarsa ba so dandai ya matsa ne saiya biyoni"
Zubewa tayi ta rushe da kuka tace “Allah na gde maka daka bayyanamin shi a raye Mai Martaba Amma ya gane Sarki junior ko?" Murmushi yayi yace “ni kaina da zan fita na dawo saiya tambayeki waye ni" zubawa Rasheed ido tayi da yake bin dakin da kallo yace “Mai Martaba shima wannan dakin bansanshi ba shikuma wannan da bashi da Ify waye?" Yana mgnr yanakai hannunsa ga Kareem dake kwance kamar gawa riqe hannunsa Mai Martaba yayi yace “bakasanshi ba?" Daga kai yayi yayi murmushi yace “wani qaninka ne Kareem ja tunasa?" Dafe kansa yayi kamar zai tuno ya dago yace “ok shine wannan wanda mukayi yaqin tare dashi aka sacemu tare aka kaimu Sudan kace sunan gurin ko?" Murmushi Mai Martaba yayi ya dubi Juhud data kwantar da kanta a jikin gadon tana kallon ikon Allah.

Likitan ne ya shigo suka gaisa da Mai Martaba suka fita suka barta ita da Rasheed abin yana tsuma jikinta da ruhinta wai gata ga Baffa'am dinta Amma baiko kallonta harkar gabansa kawai yakeyi ta miqe tanajan tsohon cikinta me watanni takwas ta matsa bayansa ta sassauta muryarta tace “Abdulrasheed" juyowa yayi ya zubanta ido tare da dibanta ya watsar hawaye ya sake tsiyayo mata tace “wai da gaske baka ganeni ba?" Daina latsa wayar yayi ya sunkuya ya ciro takalminsa duka biyun ya miqa mata yace “nasan sune sukayi miki kyau to gasunan na baki" noqewa tayi taqi karba tace “meyesa zaka mantani tsayin shekara shidda nakasa cireka a Raina na kasa karbar kowa bayan kai Rasheed ni ban cancanci ka mantani ba....."
Saurin ja baya tayi Ikcn daya fara kwance tazugen wandonsa gabanta ya fadi tana kallonsa tanajin ninkin faduwar gaba gani tayi ya zare wandon ya kuma cire rigar ya rage dagashi sai singlet da boxes ya nufeta Yana murmushi yace “nifa kinganni banida rowa idan kinason wadannan dinma zan iya baki wlh Meenah ta tafimin duk abinda na mallaka a duniya Kuma kinsan Meenah ta mutu Ina zuwa kogin maliya zan fada ciki na tsunduma tsundum na mutu nima kowa ya huta yawwa ai kema kinsan zan hadu da Meenah acan ko?"
Tashin hankali Yana matsarta tana matsawa ya damqo hannunta ta rintse idonta ya damqa mata kayan yace “ki riqe nabaki sadaka idan kinason agogon ma da zoben duk na cire miki Ni dama na daina kwalliya takaba nakeyi Kuma bazan qarason wata mace ba a duniya tunda na rasa Meenah"

Girgiza masa kai takeyi tana kuka me gunji ya dora hannunsa a bakinsa yashe “dallah malama kiyi shiru Meenah batason kuka" gumtse bakinta tayi ya juya zai fita Mai Martaba ya budo qofar ya shigo yaja ya tsaya da sauri yace “ya subhanallah Rasheed meye hakan?" Murmushi yayi ya sosa sumarsa yace “ai harkai zan iya kyautarka indai akan Meenah ne" zaro ido Mai Martaba yayi yace “nidin Rasheed" dariya yayi harda riqe ciki yace “kaidin har wata daraja ce dakai ta

musamman da zatasa naqi fansar dakai akan Meenah?"
Girgiza kai Mai Martaba yayi yace “naji banida ita Sanya kayan naka muje masauki" juyawa yayi ya kalli Juhud ya tsugunna yace “don Allah mamana kibani aro Allah niba barawo bane zan dawo miki dasu yau dinnan aidai bake kika sani ba nine nasa kaina nabaki kyautarsu ko?" Miqa masa tayi yace “aafah Hajiya in kinsan ba tsakani da Allah kika baniba bar kayanki"
Dauke qwallah Mai Martaba yayi yace “karbi tsakani da Allah tabaka" yasa hannu ya karba Yana sawa Yana waqarsa “Meenal Aso kin matar da zuciyata ta mace! ki tausaya karki sani bangare na yaudara!! Ina gudun duniya!!!"

Da wannan ya fice Mai Martaba ya dubeta yace “likitana ya tabbatar min da zai samu sauqi fah karki damu" ficewa sukayi suka barta da kallon Kareem dake kwance kamar gawa ta juya itama ta fice kamar mahaukaciya ta nufi block nasu ta fada gado domin tabawa zuciyarta hutu daga sabon tashin hankalin daya tunkarota ga Baffa'am dinta a gabanta Amma yakasa ganeta to waima meye asalin dalilin sukurkucewarsa ne haka Shiba Mai mgn ba Amma surutai rarrara kamar Wanda ya qone a qeya miqewa tayi tare da cewa “tabbas Ikc yayi da zan sakawa Mafi cancanta Alkhairinsa....."
Tunaninta ne ya tsaya cak da tunawa da Kareem shikuma da yake cikin halin ni yasu dora hannu tayi akanta daidai Ikcn da wayarta tayi ring ta wawurota Ya'isha tace “na dade inason tsegumta miki watanni biyu baya anga Big Cele a Tanzania to tsoron jagula wannan dofanannen auren naki da Ya Kareem yasa Mom ta Hanani fada miki wai Kuma yau sainaji me kankat ankawo mikishi har qasarku"
Cikin kuka tace “shine me gata ko rashin galihu yasa kukaki fadamin labari mafi soyuwa a duniyata Ya'isha ko ku fada ko karku fada Rana irin wannan zatazo gashi tazo Baffa'am ya dawo zamana da Kareem ya qare....." Da qaraji Ya'isha ta katseta da cewa bakida hankali ne karki soma wlh Kareem yafi kowa buqatar taimakonki kinaganin fa a halin da yake" jan zuciya tayi tace “meye ribata dama uwarsa ta rantse indai na haihu saiya sakeni to kafin ma na haihu zanbar mata gidan danta nima a dole nake zaune don halacci" magana Ya'isha keson yi mata ta kashe wayarta can Mom ta kirata tace “idan kin kwantar da hankalinki akwai labari me dadin dadi da nakeson baki"

Muryarta harta dashe tace “kun boyemin abinda na cancanci nasani Mom meyesa" murmushi tayi tace “saboda kada muyi mahaukata biyu a dangi shiyasa Meenah kifa nutsu motsi kadan zakiyi ki fada rami mijinki yafi kowa buqatarki to kibi sannu kada santsi ya debeki"haka Mom ta rinqa bata kalamai wai ita a dole saita kwantar mata da hankali batasan qara tashin hankalinta takeyi ba suna kashe wayar Dr Khazeem yazo ta dubeshi yace “ya naki jikin batason hayaniya hakan yasa tace “naji sauqi so ganin yanayinta yasashi ficewa ta koma ta kwanta kamar bazata koma asibitin ba saidai taji zucciyarta taqi natsuwa dole ta shirya ta nufi asibitin ga mamakinta

saita isheshi a zaune shida Mai Martaba ta dubesu suka gaisa da Mai Martaba yace “kema kina buqatar hutu ya kamata ki koma gda ki haihu acan" jinjina kai Kareem yayi yace “dama inada burin hakan sai na kwanta jinyar nan" da wannan sukaci gaba da tattaunawarsu hankalin Kareem na kanta Mai Martaba yace “ki koma masaukinku ki huta zan kwana dashi muga abinda hali zaiyi".......

_Yau fah saidai hqr da qarancin page din_

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏽 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane  ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/12, 8:08 PM] Oum Hairan: Duban juna Juhud da Kareem sukayi yayi mata qaramin murmushi ya shafa sajensa tare da nuna mata hanya yace kije ki huta heart kinyi qoqari fah na gde Allah yabada lada" sunkuyar da kanta tayi tare da daukar wayarta tayi musu Saida safe ta fice ta nufi masaukin nasu zuciyarta na kaikawo tsakanin qirjinta da duniyar Rasheed, tana zuwa wanka kawai tayi tayi sallah ta kwanta itakam wannan dare barawon ma kasa satarta yayi gabadaya ta rasa nutsuwarta batajin daidai saina tunanin Rasheed, da asuba tayi sallah ta zauna tanayima iyayenta da Rasheed addu'a tare da fatan sauqi da sassauci cikin wannan jarabawa da suka tsinci kansu a ciki ciwon tabuwar qwaqwalwa a Rasheed abin Babu kyau.
Data tashi da ciwon mara ta tashi hakan yasa bata koma asibitin da wuri ba Saida Tasha magani ta dan samu relief sannan ta fita ta nufi hospital din a qofar dakin da Kareem yake ta ishe Rasheed Yana tsaye yana danna waya kamar ance ya dago suka hada ido ya lumshe idanunsa qirjinsa Yana bugawa itama haka ta matsa gabansa tace “barka da sfy Baffa'am" ja tayi da baya lkcn daya kece da dariya yace “shegiya ashe kinsan sunana ai Meenah ce take kirana da wannan sunan" lumshe idonta tayi hawaye ya ciko ijiyarta ta bude akansa ta girgiza kai tare da cewa “ka manta kowa da komai ka manta kamannin Meenah a zahiri Amma baka

manta sunanta ba Baffa'am ya akayi hakan?"

Yarfa hannu yayi yace “nima to nasani kawai dai kema kinsan idan na kama Wanda ya kashemin Meenah a gabana saina dirmeshi da alburushi ke barima kiji fah koda yake na daina kulaki Meenah kishine gareta batason a hadata da wata a mafarki Ina ganinta kullum Kuma fah tana dan kama dake kadan Amma bakikai kyaunta ba" Mai Martaba ne yajiyo mgnr ta Rasheed tayi yawa ya leqo yaga ashe shida Meenah ne tasashi a gaba sai hawaye takeyi ya qwala mata Kira tayi saurin goge hawayen tace “ok ganinan" ta juya zata tafi ya riqota yace “shifa Wannan mutumin dan raini ne ya rainani yama zaayi Ina mgn da mutum ka kirashi to kaima ka kiyayeni kafin na qundumeka" zaro ido sukayi dukkansu ya dora hannunsa a bakinsa yace “lalalah ashe fah sabo nakeyi kayyy ke haihuwa zakiyi me zaki Haifa?"
Ganin batada niyyar tahowa ne Mai Martaba ya fito yaja hannunta yace “idan kika biyewa wannan saiku raba Rana da dare yanayi miki soki burutsunsa" sosai sautin kukanta yake fita batare da tasan kalmar ta subuce ba tace “ta Ina zan fara taimakonsa?"
Dubanta Kareem yayi ya kawar dakai yanajin wani abu nayi masa yawo a qirji da sauri ta share zancen da cewa “Mai Martaba ya jikin nasa?" A gajarce yace da sauqi sosai dama Ikcn hutunsa yayi zamu tafi gabadaya daku saboda dukkanku kuna buqatar kulawa" jinjina kai tayi tabbas tana buqatar kulawa sosai Kuma taji dadin hakan domin itace damarta ta fuzgo yancinta zuciyarta na raya mata dolene Kuma wajibi akanta ta qwaci kanta domin Baffa'am dinta.

Kwanaki biyu suka qara a asibitin aka sallamesu cikin kwanakin ta fahimci abubuwa da yawa game da Baffa'am dinta hakanan wani Ikcn sai yayi shiru yaqi yima kowa mgn ya rinqa kallon kowa daidai idan Mai Martaba ya cika damunsa saiya tashi kawai yakoma jikin tagar dakin yana hango waje yana cewa “kawai don anga Aminatuh batada gata sai a takurawa mijinta nifa idan kunsan takurawa na Meenah nazakuyi to kubarni ko da qafa zan koma Tanzania harda Sudan naje naci gaba da gadin kabarin Meenah ta"
Zantukan nasa a sukurkutacce suke ba kowa ke fahimtarsa ba Amma ita tana gane wani abu cikin maganganunsa ta fahimci kamar akwai hoton abinda yake masa yawo a kwanya da yake bashi gizon mutuwarta tunda dukkan wata kalma tasa mutuwa yake cewa Meenansa tayi to ya akayi haka?" Abin da yafi komai bata al'ajabi ita daya yafi yiwa wannan soki burutsun zantukan nasa marasa kan gado inda ta fahimci Kareem ko kadan bayason yaga Rasheed ya fiye mata mgn shi kansa Mai martaba yana nuna alamun hakan wannan take sanyata cikin jimami domin da tazo asibitin kafin sallamarsu zai tareta da cewa yawwa qawata zo na baki Ibrn Meenah a duk sanda ya fadi haka sai takanga fuskar Kareem tayi duhu inda ita Kuma takan shiga tunani da zullumin wannan lamari.
Kwana uku suka qara komansu ya kammala suka dauki hanyar 9ja ko a cikin jirgin da Rasheed

ya fara mata mgn sai Mai Martaba ya katseshi da cewa kai wai meye yake damunka ne Rasheed shikuma gashi ko yayi shiru baa minti biyar zai sake zungurota yace mata “yawwa qawata akai kaza akai kaza" haka Mai martaba zai sake mata tsawa itadai ta kasa jurewa ganinta wannan ai takura dan adam ne Kuma ma meye don ya zabeta matsayin abokiyar hirarsa aikuwa tayi kicin kicin da fuska ta juya gabadaya gareshi ta kamo hannunsa tace “labarin me kakeso ka bani Baffa'am?" Dago kansa yayi da yasa cikin cinyarsa ya dubi Mai Martaba da Kareem yace “ai dama batun yanzu ba na fahimci wadannan Gayun basasona da qawance dake Kuma na daina kulasu"

Murmushi tayi tace “to Kuma meye na kukan aini Inasonka da qawancen...." Ihu yayi yace “don Allah da gaske?" Daga masa kai tayi yace “wayyoh dadi zan baki alawar madarar dana siyawa Meenah zankai mata lahira idan munje gda" murmushi tayi me hade da hawaye tace “Baffa'am ai wanda ya mutu baici baisha baya mgn fah" hannunsa yayi a baki yace “dallah ware sunguma malohuwa ita Meenah an fada miki irin mutuwar kowa tayi ne ai ita kullum tare muke kwana da asuba saita bace bana qara ganinta sai wani daren Kuma in fada miki kullum cemin takeyi Inasonka Baffa'am dina bazan taba rayuwar farin ciki ba tare dakai ba kaji a ranka ko bana duniyarka to Ina fadar zuciyarka daka bani nini kadai....."ba itaba dukkansu Saida suka kalleshi sak muryar Juhud yayi amfani da ita wajen furucin tayi dariya sosai tace “Kana bani nishadi....." Wata tsawa Kareem ya daka mata yace “yaci gaba da baki nishadi zan datse duk wata alaqa dake tsakaninku kuwa muga qaryar baki nishadi" dama a qufule take dashi da Mai Martaba ta kuwa hayayyaqo masa tace “zaka iya Kuma? Kanajin kanada qumaji da qwarin gwiwar raba hanta da jini ne? To karka soma shidin bangare ne na rayuwata da bashida tamka wlh a duniyata yafi iyayena domin na rasasu tun bansan dadinsu ba shine ya mayemin gurbinsu ya zamemin uwa uba Yaya qani aboki qawa sannan ya........" Dauketa da mari taji anyi ta dafe gurin da sauri kafin ta kanta ya gama juyawa taji qarar wani Marin ta bude idanunta da sauri taga Kareem dafe da kunci Mai Martaba a tsakiyarsu Rasheed sai huci yakeyi yana hanqoro so yake ya samu dama ya damqi Kareem Mai Martaba ya hanashi yace “kasheka zanyi in kashe banza wlh don akan qawata Babu ruwana dakai qanina ne inma yayana ne saina aikaka inda na aika Wanda ya kashemin Meenah"

Zama Kareem yayi Yana huci Yana cije lebe shima Rasheed ya zauna yace “saqagon banza dashi dabai iya komai ba sai cin zali" shidai bai kulashi ba don ya fahimci idan yaci gaba da kulashi mahaukata biyu zaayi Amma yaci alwashin ta qarfin tsiya saiya raba Meenah dashi suna sauka a Kano Lado driver yazo ya daukesu suka nufi Katsina Mai Martaba motarsa daban shida Rasheed shikuma shida Meenah ko a tafiyar babu me cewa wani qala har suka isa Katsinan a yanda Mai Martaba ya tsara dole haka sukabi gdan sarautar suka nufa anan yace su zauna harta haihu.

Yana qunci da cin magani suka shiga cikin gdan kai tsaye ya figi hannunta suka shige part din nasa ya kulle qofar ya saki hannunta Yana huci ta juya ta nufi kujera ta zauna ko kallonsa batayi ba ya gama kumburinsa ya nufi dakin baccinsa ta tabe baki a ranta tace “ka kuwa hadu da aiki" batabi ta kansa ba itama ta shige dayan bangaren tayi wanka ta bude Jakarta ta dauki doguwar riga ta sanya tasa mayafinta ta sulale tabar part din ta nufi cikin gdan ta matsu taga Mom tana shiga falon Mom ta taso da gudu ta tareta da cewa “oyoyo oyoyo Aminah ta" dariya tayi suka zube a kujera tace “ashe kema kinyi kewata Mom Ina Sarki" juyawa tayi inda suke zaune shida babansa tace “au shine bazaka kulani ba" dariya yayi ya taso ya fado jikinta yace “kin tafi kin barni inata kewanki Dad dina ya dawo inaso kizo ki ganshi kullum na saci wayan Mom na kiraki sai najita a kashe"

Murmushi tayi me hade da hawaye tace “Allah Sarki My Son kana Raina ya kakeji game da dawowar Dad dinka?" Kwantar dakai yayi jikinta yace “happy Mom kinsan me Dad dina fah bashida Ify baya gane kowa harni" share masa hawayensa tayi tace “ka daina damuwa zai ganeka zansa ya ganeka kaji" daganta kai yayi Rasheed dake zaune yace “kuma itace qawata da nake baki Ibr Mom Kinga ashema tasanku tasan wannan yaron da yaketa cemin Dad" tare suka share hawaye da Mom Mom tace “hakanma mun gode Allah Meenah wai a hakan fah an samu sauqi  farkon Ikcn da aka tsintoshi abin baa cewa komai sai gdyr Allah Amma yanzu yaji dama"
Jinjina kai tayi ya taso ya dawo kusa da ita tayi saurin sanya Sarki a tsakiyarsu yace “dariya ma kike bani" dukkansu sukayi dariya Daidai Ikcn da Addah Abulle ta fito daga sashin Mai Martaba idanunta akan Meenah sukayi kallon kallo taja baya da sauri tace “na shiga uku ni Zainabu wato shegen yaron nan da yace sun zubar da cikinga ashe qarya yakeyi" murmushi Meenah tayi zuwa yanzu zuciyarta ta fara tsikewa tace “sannu fah Addah ya gda mun sameku Ify?" Wata uwar qwafa tayi ta nufi dakinta fuuuuu Meenah ta tabe baki ta mayar da hankalinta ga Mom sukaci gaba da hirarsu tanata dariya abinta shirmen da Rasheed yake buga musu ko Sarki bazaiyi ba   suna haka Fadila ta fito ta debesu ta watsar Meenah tayi murmushi tace “Allah Sarki wannan fah Mom?" Girgiza kai tayi tace “au Fadila auren ne yaqi dadi mijin neman mata har ksn gadonsu na sunnah shine tayo yaji ya aiko mata da takarda saki daya" dafe qirji tayi tace “ya salam Abin tausayi Allah ya daidaitasu" murmushi Mom tayi tace “kayyah dai itama Amrah jiya ta koma aure mijin ya qara shine zatayi masa haukanta ya korota uwar mijin tace ita dama batason wannan auren daidai ya nace ne daqyar dai aka sasanta ta koma kayy Meenah munga jarabawa dan ritsin nan " jinjina kai tayi tace Allah yasa ta zamo kaffara amsawa tayi da Amin sunata hirarsu ta yaushe gamo Kareem ya shigo suka gaisa da Mom ya dubi Juhud yace “bansan kin fito ba fah Saida na leqa dakinki naga bakinan" murmushi tayi tace “nazo mu gaisa dasu Mom ne"

Miqewa yayi ya nufi part din uwarsa yace “ok ku gaisa sosai Amma ki nemamin abinci yau girkinki nakeson ci....." Rasheed dake tura motar wasan yara shida Sarki ya dago yace “lahhh zaka sammin?" Tsayawa Kareem yayi ya juyo ya dubeshi da tausayawa yace “in kanaso ma kullum ka rinqa zuwa kana karba Aminah ta iya girki sosai" tsalle yayi ya dafesa yace “itama sunanta Meenah nima tawa Meenan ta iya girki nifa tunda Meenah ta mutu ban qara cin abinci me dadin nata ba"
Tsayawa yayi kamar zai juyo sai Kuma yasakai ya shige ciki sama² suka rinqa jiyo hargowar Addah Abulle basajin dai abinda suke cewa Meenah ta miqe tace “bari na koma Mom duhun magrib ya fara shiga saida safe" ta juya ga Rasheed daya zuba mata ido tace “Baffa'am Saida safe" daga mata hannu yayi yace “zanzo na karbi abincin naki ai" murmushi tayi ta juya ta fice ta nufi sashinta taji an bangajeta taja baya da sauri tare da cewa A'uzubillahi....." Tana duban Wanda ya bangajeta din Fadila ce qanwar mijinta tayi murmushi kawai ta juya taci gaba da tafiyarta a bayanta taji tana cewa “gayyar na ayyah gayyar tsiya an dawo zaaci gaba da dorawa uwarmu ciwon zuciya jarababbiya qalatacciya da wani shegen cikinki a gaba irin masifa irin maita......"
Kalamin sun daketa ta cije lebe tare da tsayawa batare data juyo ba tace “hakane saidai kin manta abu daya bani na liqe mawa dan'uwanku ma shine qalatacce jarababben daya liqemin wlh da zaku bashi shawarar ya rabu dani ma ya dauka da dadi nikaji domin zan yar da qwallon mangwaro na huta da qudaje"

Tana fadin haka ta shige tabar Fadila sake da baki lallai yarinyar ta riqa wato sune qudaje Kareem ne mangwaro tab yau da tashin hankali a gdannan, fuuuu ta shige ciki ta nufi sashin uwar tasu tana shiga ta fara karanta mata qarya da gaskiya aikuwa ta hau ta zauna ta dauki waya ta Kira Dada Hanne ta zayyane mata abinda ke faruwa Dada Hanne tace “ai Ni wannan jaraba na rasa dame tayi kama yarinya ta zamewa mutane qarfen qafa an kasa kwanceta a yar shima Mahfuz din kwanaki kamar abin arziqi aikin da mukayi ya fara cinsa yanzu Kuma yaqi kullum abubuwa lalacewa sukeyi"
Takaici ya cika zuciyar Addah Abulle tace “ni takaicina ma cikin nan da yake jikinta ashe bai fadaman lissafin daidai ba boyemin yayi yanzu kawai Ina ganinta naganta da tsohon ciki haihuwa kusa" wata uwar ashar Dada Hanne ta qunduma tace “au ke yanzu kina zaune sakarai kika bari tayi ciki kema zaa jorner miki tsiyar?" Da muryar takaici tace “to ya zanyi kefa kika sani na rinqa rabar da kudi tsakanin gurin malamanki dana Hajiya Bilki nidai banga wata nasara ba saita dawowa ta gdannan"
Qwafa Dada Hanne tayi tace “ai shegiyar gantalalliyar yarinyar ce masifar taurin kaine da ita bansan wanne irin shiri ne a jikinta ba Amma bari intasan wata batasan wata ba" sun jima suna saqarsu a mugun zare sannan sukayi sallama da shirinsu na cimma matsaya.
Meenah kam tana shiga part dinta idanunta ya sauka qasan tiles din taga wani garin magani duk an barbadar dashi kiyayewar Allah ce kawai tasa taga maganin saboda shima arsh ne kalar tiles din, taja baya da sauri tana a'uziyya a fili ta fara dube dube bataga Wanda zata Kira ba ta koma gefe ta tsaya tsam jikinta na tsuma tsoro ya cikata tana nan tsaye Allah ya jefo mata

Kareem taja ajiyar zuciya, qarasowa yayi da sauri yace “meye kikeyi anan Kuma?"  Dubansa tayi jikinta na tsuma tace “naje zan shiga naga wannan abun" idanunsa ya zuba a tiles din ya na kallon abin ya girgiza kai yace “ki shigo da Bismillah babu abinda zai sameki sai abinda Allah ya hukunta kiji haka aranki"..........

Kama hannunta yayi suka shiga cikin gdan ya janyota jikinsa yana sunsunar qamshin gashinta yace “kin wahalar da zuciyata yau" dagowa tayi ta kalleshi yayi mata murmushi yace “kiyi komai ba komai ya Ifyr babyna" ajiyar zuciya tayi tace “nima nasani" dariya yayi yace “kuma kina tare dashi?" Kautar da kanta tayi sukaji ana buga qofar suka kalli qofar tare ji sukayi anyi sallama gabanta ya Fadi ta janye yace “ina zaki?" Kallonsa tayi tace “Baffa'am ne ke buga qofar nan fah...." Janyota yayi yace “to me zaki bashi?" Tsayawa tayi tayi sororo sai Kuma ta juya da sauri tace “zan bashi hqr ne yace yau bazaici abincin kowa ba sai nawa"
Zama yayi ta bude qofar tana budewa ya shigo yace “ina abincin nawa?" Yana mgnr yana kalle kalle ta kalli Kareem tace “yanzu zan girka maka me kakeson ci?" Kallon kitchen din yayi yace “nima fah na iya girki muje na tayaki nawa ma sai yafi naki dadi" zaro ido tayi tayi dariya tace “habadai aiko Ya Kareem bazan sa girki ba balle kai da girmanka da matsayinka" nuna mata hanya yayi yace “ok aje abani abincina naci na kwanta sallar ma yau bazanyi ba" kitchen din ta nufa Kareem ya tashi yabi bayanta taliya ta dauka ta girkata fara  ta tace ta dauko kayan miya ta soya ta zuba kifinta bushasshe data gyara ta dauki hantarta ta zuba ta soya sannan ta zuba kayan dandano ta juye taliyarta ta cakuda a cikin man nan da kayan miya ta barsu suka dahu daidai buqatarta ta sauke.

Bata tsaya hada lemo ba ta dauko na kwali ta dora akai ta zuba mawa Baffa'am dinta nasa sannan ta zuba nasu ta fita yana zaune har yanzu Yana karkada qafa ta ajiye masa a gabansa ya dauka ya miqe yace “yawwa na gde" ficewa yayi ta girgiza kai ta dauko nasu ta jera a dinning ta nufi dakinta tayi wanka ta fito ba kwalliya take ba ita dama doguwar riga kawai tasa ta fito ta qwanqwasa dakin na Kareem tajishi yana karatun qur'ani ta bude ta shiga, Saida yakai simuni sannan ya  juyo ya dubeta yaja ajiyar zuciya tace “barka da hutawa" jinjina mata kai yayi tace “na kammala" murmushi yayi yace “kin bawa Ya Rasheed din?" Dagansa kai tayi yace “ya tafi?" Ta qara daga masa kai yace “ok sannu da qoqari"
Tashi yayi suka fita suka zauna a dinning din ta hada masa abincin ta miqa masa itama ta zuba yaja yayi Bismillah ya faraci itakam juya cokalin kawai takeyi gabadaya zuciyarta kwanakin nan a karye take akan lamarin rayuwarta ta dago tace “Ya Kareem" dagowa yayi ya zubanta ido tayi qasa da nata yace “fadi Mana" zuciya taja tace “ina tunanin wani abu fah zuciyata tana saqamin abubuwa da yawa nikam don Allah Ina neman alfarmar kabani damar kula da Baffa'am dina kamar yanda ya kula dani a baya" zubanta idanunsa yayi da suka fara canza kala ya aje cokalin hannunsa ya furzar da iska ya miqe ya juya zaibar gurin, yakai bakin qofar dakinsa tace “itace

alfarma ta farko dana fara nema a gurinka idan kaqi yimin ita to tabbas zanci gaba da ji a Raina na rasa damata na rasa yancina tun shekara goma baya Ikcn da Ina matsayin ya a gurin Baffa'am dina da shekaru shidda shudaddu da na kasance mata a gurinsa Kareem meye kake zargi don nace zan kula da Abu mafi muhimmaci a sashina?"..............

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏽 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane kada ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/13, 9:07 PM] Oum Hairan: Juyowa yayi ya zubanta idanunsa da suka jima da canza launi yanayi mata kallon sakarya ya sake juyawa zai shige ciki tace “idan kaqi aminta hakan ba Yana nufin zan barshi ya wofinta bane gareni shine qarshen....." Daganta hannu yayi yace “ya isa dalla kada ki tarwatsamin zuciya da wadannan shashashun kalaman naki da bazasu taba yuwuwa ba ke a qaramar qwaqwalwarki kin taba ganin inda wani sashi ya kula da sashi a halin wancan sashin ya kasance abin farautar dayan to ki nutsu ki dawo hayyacinki wannan shirmen bazaa yisa Dani ba Ni nasan kaina Kuma nasan ciwon iyalina"
Zabga masa harara tayi tamai da hankalinta kan flat din gabanta zuciyarta na angizota ta fada masa ba sugar shima wata na hanata tana cewa da ita tayi hqr ta qyaleshi hakanan ta miqe a gajiye ta shige dakinta tayi sallar magrib ta zauna tana addu'arta har Isha tayi ta aikata sannan ta miqe tayi Shirin kwanciya tayi hayewarta gado taja bargo tana me miqa lamuranta ga Allah baccin me dadi kuwa ya dauketa Wanda ta jima bata samu irinsa ba cikin baccin taji an bude qofar an shigo tanaji ya mayar da qofar ya rufe yazo ya kwanta kusa da ita ya janyota jikinsa ta janye tace “ko likita yace ake dagamin qafa don Allah ya Kareem ka rabu dani..." Rufe mata baki yayi da qirjinsa yaci gaba da luguiguitata bataso dole don Babu yacce zatayi dashi ta hqr ta gyaleshi itakam zuwa yanzun bajin dadin komi takeyi ba saboda cikinta ya tsufa sosai.

Da safe data tashi ta gama abinda takeyi tayi wanka ta nufi sashin su Mom a lilo ta tarar da

Rasheed kamar wani cikakken mutum yaci wanka harda su agogo su glass yana duba wata magazine tayi masa sallama ya dago ya zubanta idanunsa Yana wani lumshesu tace “barka da sfy Baffa'am" daga mata hannu yayi tayi murmushi tace “dama kacemin duk ranar death date din Meenah kana azumin mgn so yau ma azumin mgnr kakeyi kenan" zare glass dinsa yayi yace “kuma ma tace na gaisheki tace tanasonki kadan" murmushi tayi tace “amma kam na gde duk kishin Meenah da kake bani Ibr harta soni nikam inada saa" bai kulata ba yaci gaba da karatunsa ta juya tace “shikenan tunda kaqi kulani na daina qawancen" tafiya tayi batasan ya biyota ba tana shiga ta zauna sun fara gaisawa da Mom kenan ya shigo Yana sharar hawaye kamar yaro qarami Mom tace “subhana meye yayi zafi?" Nuna Meenah yayi yace “ba itace tace ta daina qawancen ba" murmushi Mom tayi tace “to Banda abinka Rasheed qawance da matar aure ta Ina zai yuwu?"
Saurin katseta Juhud tayi da cewa “tsokanarsa ma nakeyi ni ban daina qawancen ba" tsalle yayi zai rungumeta Mom tayi saurin tareshi tace “kayy kada ka illatata Mana bakaga yanda take bane" guri ya samu ya zauna Meenah ta miqe ta nufi dakin Addah Abulle ta tura qofar ta shiga da sallama Addah nakan sallaya da alama walaha ta idar ta samu guri ta zauna tace “ina kwana Addah" dibanta tayi ta watsar sukayi shiru na tsayin lkc kafin tace “EDD dinki yaushe ne?" Shiru tayi tana tunani can tace “17 January" qwafa tayi tace “nasa malam Musa da yake yima yaran gdannan rubutu ya rinqa yo miki qila ki samu sauqin naqudar"

Gabanta ne ya fadi hakana taji zuciyarta batayi na'am ba a fili Kuma sai tayi murmushi tace “na gde Allah ya dada girma" daga haka sukaci gaba da shiru har Fadila tazo ta ishesu a haka ta kallesu ta watsar itakam aikin da Addah ta bata batajin zata iya da fari ma ta yaya zata shiga jikin Meenah bayan tun farko basa jituwa balle har tayi nasarar bata gubar da zatasha ta kashe dan dake cikinta? Wannan tunanin ne ya Hana zuciyar Fadila sakat har Juhud ta miqe tana cewa dasu sai anjima dukka suka bita da kallo kowa da saqarsa a zucci.
Sashin Mom ta koma ta zauna tayi tagumi tana tunanin wannan al'amari Mom ce ta fahimci da matsala tace mata “yadai Aminatuh?" Dagowa tayi tace “mom Addah ce tace wai kullum zata rinqa karbar rubutu gurin Malam Musa tana kawomin inasha" da sauri Mom ta kalleta tace “akan me?"
Sunkuyar da kanta tayi tace “wai zan samu sauqin naquda" shiru Mom tayi can tace “miqon wayar nan" miqa mata tayi ta Kira lambar Malam Musa bugu biyu ya daga suka gaisa tace masa “Hajiya Abu tayi maka mgnr rubutun naquda ne?" Shiru yayi can yace “gsky ban tuna ba Ina tunanin ta sha'afene?" Murmushi Mom tayi tace “shikenan Meenah ta ce takeda ciki wata takwas ka fara yo mata rubutun kana kawomin" gdy yayi sukayi sallama ta kalli Meenah tace “to kinji dai sai kiyi takatsantsan koda wasa kada ki yarda su baki kisha wadannan mutanen babu Allah a ransu.

Jinjina kai tayi sukayi sallama ta tafi sashinta ta kwantaTunaninta Yana bata to da me Addah Abulle ta shiryawa cikinta da Mom ta ganota?" Tabe baki tayi ta juya baya suna chat da Ya'isha taji an turo qofar da sallama ta tashi ta zauna tare da amsawa Amrah ce ta shigo tayi mata murmushi itakam tsayawa tayi sororo tana kallonta ta nemi guri ta zauna tare da cewa Aunty Meenah Ina yini" fuzgo numfashi tayi tare sauke ajiyar zuciya tanajin abin wani bambarakwai wai namiji da suna Fatsum bata gama wannan tunanin ba taji Amrah tace.
“Abubuwa da dama sun faru da suka sanyani nadama tabbas ita gsky duk inda take sunanta gaskiya Ikcn da labari ya isheni cewa kedin yar yayar Mom ce jikina yayi mugun sanyi kunya ta lullubeni a Ikcn da Mom ta dawo take sanar da Mai Martaba cewar kece akwai yayarta data dade tana nema a 9ja tabi rugage ds dama domin gano inda zata sameta hakan ya faskara ta tabbatar bayan dogon bincike d ruwan da akakai Rana baffaninki da sukazo suka sanar damu kedin Mayyace sun kwatanta mata inda zata same kakanki harma da bata tsoffin hotunan Kati guda biyu na kakarki wacce ta haifi mahaifinki Aminatuh wadda kikaci sunanta da Kuma na mahaifiyarki, a jikin wannan hoton ne ta fara fusknta r wani abu"

Shiru Amrah tayi kana ta dago ta kama hannun Meenah tace “ganin kamanni da yanayi na jininta jikin wadannan hotuna yasata bin duk wata hanya ta roqi alfarmar wadannan baudaddun Fulani su rakata inda zata samo miki danginki ke Saida ta hada musu da qaryar cewa kin cinye mata yayanta biyu ne jin ba abin arziqine zai kaita ba yasasu yarjemata Amma da sharadin zata biyasu ladan bata Ikc hakan kuwa akayi suka dunguma ta biya musu kudin jirgi sai Senegal ga mamakin Mom sai taga sun nufi gidan sarkin birnin da suka sauka Wanda yake kakane a gurinta shine ya haifi mahaifinta itadai bata tofa ba har suka isa ciki sunata karbar gaisuwa suka Isa sashin kakarta wadda itace uwargida a gidan ta tsufa sosai tana ganinta tace “yar qaniya ashe kina tunawa da mutane" nandanan labarin isowarta ya cika gdan ta sallami Manga ya tafi masauki bayan anci ansha an huta komai ya lafa mom ta fito da hotunan nan ta miqawa Attajiri Dodda ya karba Yana ganin dayan ya tashi zaune yace “Aminatuh Aishatu Ina kika samo hoton babarki Aminatuh?" Hawaye ne ya zubo masa yace “Aminatuh ta mutu tun baa haifeku ba dama su biyu ns Haifa daga mahaifinki Garbu sai Aminatuh naso riqe dan Aminatuh wato Haruna Amma Ina sun hanani banason zumunci ya mutu na sake Basu auren Aishatu yayarki nidai tun daga auren nan ban sake sanin labarinta ba sunbar inda nasansu sun hanata nemanmu duk da hakan shi Haro yakan kawo mamu ziyara daga baya kuma mukajishi shiru shima bayan yan watanni na tashi yaje ya ganomin ko qalau Haro shekara uku an tafi hudu baizo ya ganni ba shima mukaji Ibrn mutuwarsa nayi kukan rashin Haro, babban  tashin hankalin sun sake tashi a inda mukasansu Babu Indo Babu dalilinta babu yarsu guda daya tun daga Ikcn na baza koma ta a Nigeria neman wannan yarinya saboda naji Ibrn baqin fentin da akayi masu ta dalilin kakarta data haifi uwarta Hamida   sun zama abin tsangwama ababen kyara wai ana musu kallon mayu"........

Dakatawa tayi ta dago ta zubawa Juhud da jikinta keta rawa ido tace  tana Shirin mgn ta miqe da mugun gudu ta nufi cikin gdan Kareem dake nufo sashin ya rufa mata baya tana shiga ta fada jikin Mom ta qanqameta ta rushe da kuka me sauti Mom ta dora hannunta akanta tana Shirin mgn Meenah tace “Ashe kin nemomin asalina Mom kikaqi fadamin kika barni cikin zullumin tunanin ta Ina zan fara nemansu Mom meyesa kikeson boyemin duk abinda ya kamata na sani"

Murmushi Mom tayi tace “wato Dana Hana a fada miki Saida aka samu Wanda ya gumtsa miki Meenah tawa yata ta kaina Ni dama bantaba jinki daban da jinina ba kiyi hqr bawai na boye miki don banaso ki sani bane aa na boye miki ne don inason idan kin haihu sai kisan komai na daukeki nakaiki har Senegal da Mali kiga dangin mahaifiyarki ke yar gata ce mu goma ne gurin mahaifinmu biyu sun mutu mahaifiyarki Indo da Abdulrasheed babbanmu Wanda shine yasa mukasa sunan yayanki dan'uwanki Rasheed yanzu saura mu takwas maza hudu mata hudu zakiga kowa zakisan kowa Kakarki mahaifiyar Ummanki Kumbo Hami tace tana tafe cikin satin nan zatazo tayi aikinta tamayi na gayyar sodi balle me dalili".......

Sosai yinin ranar Juhud ta yini da damuwa me gauraye da farin ciki yanzu hankalinta ya tattaru guri daya a baya Baffa'am dinta sunan mataimaki ya Amsa a gareta ya rasa mahadi ya rasa madadi yanzu Kuma matsayinsa ya nunku yayanta ne dan qanwar babarta shin meye sakayyar daya dace tayima wadannan mutane?" Ta rasa mafita ta rasa mahanga amfanin abokin shawara kenan yanzu da ace tanada mashawarci da ya bata mafita.

Yini tayi tana safa da marwa a falonta zuciyarta tayi baqi Rasheed kawai ke haskata shine keyi mata yawo a cikinta shaidan Yana raya mata abubuwa da yawa saidai tayi a'uziyya ta kawar da tunanin kawai da haka Kareem ya shigo ya sameta da kula a hannunsa ya zubanta ido yayi murmushi yace “duk kinbi kin takura kanki kwana biyun nan akan abinda baki isa canzashi ba am bama wannan ba wainar fulawa naga Fadila nayi nace Bari na taho miki da ita" zama tayi don tun shigarta da taji Fadilan na cewa tanason yin wainar taji tanaso nutsuwa ta kasa samu da tuni tayi aikuwa ta bude kular sai tiriri takeyi ta mangyada taji lawashin albasa da attaruhu ta hadiyi yawu ta gutsura zatakai bakinta tayi Bismillah kenan taji an tankwabe hannunta tana dagawa taga Amrah cikin hawaye tace “Karka barta taci wannan wainar sun zubanta guba ne don su kashe dan dake cikinta Ya Kareem nayi tunanin Ikcn da Addah ta tabbatar da cewa Meenah ba mayyah bace zata sauko ta dawo hanya Amma abin mamaki sai naga dawa ta qara shiga su Hajiya Bilki da Dada Hanne suna zugata, Ya Kareem meye ribarsu idan sun kashe dan dake cikin Meenah sunada tabbacin zaka qara samun wani ne kaida Meenah waye yafi asara tunda ita ko ba komai tanada Sarki junior kaifah?" Tunda ta fara mgnr gumi ke karyowa Kareem tana kaiwa nan bata Ida rufe bakinta ba taji an daki hancinta Addah Abulle tana huci tace “shegiya munafuka nayi danasanin Bari Mom ta shayar dake dana sani Madara na dura miki qila da bakiyi sakaryar zuciyar nan ba ni dama nasan haka zata faru to bari kaji na riga na tsani Meenah tun daga Ikcn da tabarka ta auri Rasheed bakuma zan taba sonta ba ban qaunarta ban qaunar jininta Abdulkareem zabi biyu zan baka kodai ka saki Meenah ko Kuma ka dawo da

Zahrah idan kaki zabar daya cikin biyun nan zan dagsnka nono nabarka da duniya da macen daka zaba akaina ka gani idan zaka qare qalau kanadai kallon yanda qarshen Rasheed ya qare daya zabeta yabar uwarsa da ubansa shima da takeso kenan bakai dan karere ba da ake maleji dakai a rashin uwa akai uwar daki dakai".................

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/16, 8:25 PM] Oum Hairan: Tunda ta fara mgnr Juhud ta zubanta ido tana murmushi har Saida ta ida kaiwa qarshe sannan ta tabe baki tace “dama zabi daki kika bashi na rabuwa dani da yafi muku Alkhairi dukkanku dama neman gaba nakeyi banji a Raina zan iya rayuwa ta har abada da danki ba saboda haka ki kwantar da hankalinki saura kadan lkc yazo....." Daganta hannu yayi da qaraji yace “Meenah ya isheki haka" dubansa tayi tayi murmushi tace “akanme zan shiga hankalina bayan nasan cewa ko nayi shiru din ba gwani zanyi ba Kareem nagaji da rashin mutuncin danginka wlh bazan dauka su doramin ciwo a banza ba...." Daga hannu yayi zai mareta ta riqe hannunsa tana murmushi tace “karka soma wlh ramawa zanyi" ji tayi an dauketa da mari ta dafe gurin tare da dagowa Mom tagani hawaye ya zubo mata tace “akan wannan mutumin zaki mareni Mom na rantse da Allah na gaji Mom nagaji ni nagaji...." Riqeta Mom tayi ta jata suka shiga ciki ta zaunar da ita tace “bana tunanin haka daga gareki Ina hqrnki yafara tafiya ne Meenah komai fah na duniyar nan lkc garesa don Allah kici gaba da kawar dakai akan lamarin gdannan huccewa zaiyi kamar baayi ba" haka Mom ta rinqa bata baki hardai taga ta russuna tace “ga rubutun an kawo miki" karba tayi tayi Bismillah ta shanye Mom taja numfashi tace “ki huta Rasheed ne yaje yacemin Yazo gurin qawarsa Kareem ya hanashi shiga" gdy tayima Mom ta tafi itakuma ta zauna tana tunanin Wannan rayuwa tata idan nan ta kau sai nan ta bulle tabbas akwai aiki a gabanta.

Har goman dare Kareem bai nemeta ba itama bata nemesa ba haka suka kwana washegari ya fice tun kafin ta tashi itama data gama abinda takeyi tayi tafiyarta sashin Mom wajen la'asar Kumbo Hami ta iso tana zuwa ta rungume Juhud tana kuka me tsuma zuciya tana shafa kanta tana cewa “tun ranar dana fara ganinki naji Ina qaunarki a jinina ashe kedin jinina ce kaicon rashin sani Meenah Ina tare da jinin Aysho bansani ba Ina tare da gudar jikata bansani ba Allah na gde maka daka nunamin wannan Rana duk da banga Aisha ba naji sanyi a Raina domin naga jininta" itama kukan takeyi tana qara shigewa jikin kakarta yau gata gata cikin gata gata ga kakarta data haifi uwarta sun jima suna kukan tuntunin kafin su samu nutsuwa suka balle sabuwar hira wasa² batabar sashin Mom ba sai taran dare data shiga bata isheshi a falo ba tayi shigewarta dakinta domin yanzu ba shine a gabanta ba mafita ta gaba take nema.
Sun shafe ya kusa kwana biyar suna kallon kallo ita dashi shi a izza irin tasa jira yake ta nemesa tabasa hqr ita Kuma tunaninta baima bata laifi tayi ba balle taji a ranta zata iya nemansa ta wani basa hqr, lura yayi da batama fahimci abinda yake nufi ba hakan yasashi dole ya nufi dakinta ya tarar da ita ta kwanta ya zauna a gefen gadon Yana shaqar iskar dakin data hade da qamshin turarensa yace “wato ke ban isa kiyimin laifi kibani hqr ba ko?" Tanajinsa tayi masa banza yasan tajisa hakan yasa yaci gaba da cewa koma meye Addah zatayi miki bata cancanci fada ki fada ba domin kinsan bazanji dadi ba Amma wai kece zaki tsaya gaban mahaifiyata tana fada kina fada"

Yunqurawa tayi ta tashi zaune ta zubansa ido yanata maganganunsa tana kallonsa qurrr har ya gama tunaninsa zatayi mgn sai yaga ta gyara kwanciyarta taja bargo tace “idan ka gama ka rufemin qofar" kallonta yayi da sauri Yana mamakin qeqashewar zuciyarta cikin dan qanqanin lkc tabbas Meenah akwai abinda take nufi a zuciyarta shiyasa takeyi masa wannan iskancin a zuciye ya tashi ya fice daga dakin yaja mata qofar da qarfi ta diro daga gadon ta sanyawa qofar key ta koma ta kwanta ashe yanzu wasan ya fara daga wannan gabadaya ya fita a harkarta idan ya shigo gdan bai nemanta idan zai fitama saidai taji fitarsa abun Yana qona masa zuciya itakam ko a jikinta harkar gabanta kawai takeyi da yan'uwanta da kakarta haka lkc ya rinqa tafiya har ubangiji ya kaita gabar haihuwarta ta shima Tasha wahala kafin ta haifo qatuwar yarta mace kyakkyawar gaske.
Wannan haihuwa ta mantar da Kareem abinda ya faru ya rinqa rawar qafa akanta da babyn komai yagani ya kwaso ya kawo musu dake haihuwar dare ce da safe aka sallamesu suka dawo gda wani abin mamaki daya soki zuciyar Kumbo Hami da Mom Addah Abulle da Fadila duka suna gdan Amma babu wanda ya leqo domin ganin mai jegon da diyarta hatta Amrah da Ya'isha da suke waje sunzo Aunty Hamida kuwa da ita suka kwana a asibitin ashe ba iyakar Mom da Kumbo Hami abin yayima ciwo ba Kareem yafi kowa jin ciwon abin aikuwa dif ya daukewa bangaren mahaifiyartasa qafa har akayi kwanaki hudu da haihuwar wannan karon Aliyah da Nana matan Ya Arman da Salman kunya ce ta ishesu irin abubuwan da suka rinqa yima Juhud ita Nana ashe ma Juhud jininta ce kullum dasu ake yini gdan Juhud sai yammaci

kowa ya kama gabansa.

Ranar kwana hudun ne ya fita yayo siyayya a mai jego ya dawo Urwat ya tareshi a parking space yake fada masa Addah na nemansa Saida ya shiga yaga babynsa sannan ya dauki hanya ya nufi bangaren Addah Abulle suka gaisa shiru ta ratsa ya dago yace “Urwat yace kinason ganina" dagowa tayi ta kafesa da idanunta kusan 6 minutes tana kallonsa sannan taja numfashi tace “ya mgnr da mukayi dakai? Meye makomar zabin dana baka?"
Gumine ya fara karyo masa ya dago zaiyi mgn ta daga masa hannu tace dakata ba shawara nake baka ba fah umarni ne Kuma ban baka don banasonka ba saidon nema maka mafita jin cewa Mom ta hada kutungwilarta tace Aminatuh yar yayarta ce bazai gamsheni daga abinda dangin ubanta suka fada akanta ba maita yanzu da kudi ma siyanta akeyi saboda haka wlh kaji na rantse a yau saika saki yarinyar nan ruwanka ka dawo da Zahrah ruwanka ka zauna a haka ba damuwata bace, tunda kunce rabo naji rabo Kuma gashinan an haifa saboda haka ayi komai a gama"

Miqewa tayi ta dauko masa biro da takarda ta miqa masa ya kawar dakai a zafafe tace “wlh muddin baka saki Meenah ba saina tsine maka...." “Abdulkareem karbi rubuta mata" muryar Mai Martaba suka jiyo ta bakin qofa ya tako ya shigo ya dubi Addah Abulle yayi murmushi yace “saki nawa kikeso yayi mata?" Shiru tayi tana hura hanci ya dauki biron da takardar ya miqawa Kareem yace “kayi mata abinda takeso hakan zai faranta ranta...." Hawaye ne ya zubo masa ya bude baki zaiyi mgn Mai Martaba ya dagansa hannu yace “kada kace komai kayi" hakanan ya dauki takardar ya rubuta mawa Meenah saki daya" Yana rubutawa Yana hawaye bayan ya gama ya dago ya rushe da kuka jikinsa na rawa yace “don Allah kubarni da matata wlh inasonta" murmushi Mai Martaba yayi yace “tayi biyayya a baya bata taba qin jinina ba ta faranta min itama tana buqatar farantawa Kareem kayi hqr, ke Kuma na juyo gareki daya yayiwa Juhud ke Kuma kije da biyu in an hada uku kenan"........

Dafe qirji tayi cikin tashin hankali tace “nashiga uku Mai Martaba...." Murmushi yayi ya fice yabarta da danta da yake neman ficewa a hayyacinsa har yakai bakin qofar ya tsaya yace “nayi miki hakane domin kina iqirarin kina da haqqi amma banson ki manta nima inada haqqi ga Kareem nan ciwon kai idan yayi ki dauki nauyinsa banida Ikc ko kudin da zan kashe abinda kikeso ne anyi miki fine"
Ficewa yayi daidai Ikcn da Kareem ya zube a qasa sumamme tayi kansa a guje cikin tashin hankali shikam Mai Martaba yana fita part din Kareem din ya nufa ya ishe Mom tana yima

takwararta Ayshatu baby wanka ya zubama jaririyar ido kyakkyawa da ita Masha Allah yayi ajiyar numfashi yace “idan kin gama inason ganinki"
Amsawa tayi da to ya fita Saida ta gama shirya babyn sannan ta kaiwa uwarta ita daki tana kwance tun safe batada walwala hakanan gabanta yake faduwa batasan dalilin ba tun kafin ta haihu rabonta da ganin Rasheed sai jiya takeji a gurin Kumbo Hami wai Yana gurin magani dauke hawaye tayi a fili tace “Allah ya baka Ify Baffa'am" murmushi Mom tayi tace “amin ya Allah Bari naje Mai Martaba yakeson ganina" jinjina kai tayi ta fice itakuma ta dauki yarta tana bata abincinta bayan kamar Awa daya taji Kumbo Hami tana salati tace “saki Kuma Aishatu me yayi zafi haka?" Bataji me Mom tace ba Amma Saida gabanta ya Fadi ta miqe Kumbo ta shigo ta dauki jaririyar tace “aikuwa shima Mai Martaba din bai isaba wlh sai tabar gidannan Mom tanason mgn ta katseta tace “karma kicemin komai idan zaki iya ki nemomin me kaini inda zani" a sanyaye Mom tace “Amma Kumbo magaruba tayi koma me kikeson yi kibarma gobe Mana" murmushi tayi tace “matsiyaci shine yake jira nikam bana jira" da haka ta dubi Meenah data kasa gane komai tace “muje Aminah" mgn takeson yi Kumbo Hami taqi sauraronta ta figi hannunta suka fito suna fitowa taga Muntaz yace “ina Kuma zaku tsohuwa da daren nan" kallonsa tayi tace “yo jiyemin fah dannan wannan Tataccen ne da gantalalliyar uwarsa suka wulaqantamin jiki wai saki a halin jego to debemin albarka gyatuma tayi da zan Bari mukai gobe a gdannan"

Jinjina kai Muntaz yayi yace “Ya Kareem din ne ya saki Meenah Kumbo...." Daquwa ta watsa masa tace “aa tatsunniya nakeyi maka ja'irin yaro zo ka kaini cikin gari akwai wata yar qasarmu mu kwana acan da safe saimu tafi" yasan rikicin Kumbo Hami idan ta fusata hakanan ya debesu da Meenah da taketa matsar hawaye batasan dalili ba sai taji abin yanayi mata yawo a kwanya ta tambayi kanta yafi sau goma ashe Kareem zai iya rabuwa da ita ashe dama duk abinda yake fada mata na ta rayu dashi forever itane zuciyarsa itane rayuwarsa qarya yakeyi mata?
Sosai takejin qunci a zuciyarta batasan zafin saki haka yake da qona zuciya ba hawaye ta rinqa daukewa Ikc zuwa Ikc har suka Isa unguwar da Kumbo tace akaisu dake tayima matar waya aka taresu gdane babba na masu hali suka shiga bayan Muntaz ya tafi komai ya nutsa Kumbo take fadawa qawar tata abinda ya faru sun jima suna jinjina lamarin Meenah binsu kawai takeyi da ido wani bangare na zuciyarta na ayyana mata lallai dole ta canza takunta Ikc yayi da zata tsayawa rayuwarta.

_Kuyi hqr da wannan naso yi muku typing me tsayi wani uzuri ya katseni ma hadu gobe._

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏽 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane kada ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/18, 2:25 PM] Oum Hairan: Batasan ya akayi ba da safe Kumbo Hami ta tasheta suka duma zuwa Kano kwanansu biyu a Kano ta Kira Muntaz tace ya kawo mata passport din Meenah ta bashi address na inda suke ranar ta kama kwanan yarinyar bakwai a duniya  hakanan Muntaz ya taho ya kawo musu passport din ya nan yake fadawa Meenah Kareem bashida Ify Amma fita dashi waje.
Fatan sauqi tayi masa da rangwame gurin me ikon bada sauqin ya dauko kudinsa Dubu dari yabawa Kumbo Hami yace “wai Addah ce ta bayar tace a siya rago ayima yarinyar hakika" murmushi tayi ta debi kudin ta watsar tace “kace mata mu harkar arziqi mukeyi bama ta tsiya saboda haka ragon dubu dari yayi kadan a hakikar jinin mu tabarshi ta rage zafi" da wadannan kalamai ya dauki hanyar Katsina sukuma sukaci gaba da abubuwan da zasuyi na tafiyarsu Mali domin taci alwashin Meenah ta gama zaman wannan gda da can a baya ma don bata da ikone da shi kansa Rasheed saita rabasu don sama mata salama da yancin rayuwa.
Sun qara kwana uku kullum suna waya da Mom suka dauki hanyar qasar Mali nan Meenah ta Raina kanta gdan kakanta mahaifin Mamanta ya rikita lissafinta yasata jin sabuwar izza ba gdan sarauta bane Amma barorin gdan sunfi dari ko Ina sukabi zubewa akeyi ana gaishesu har kawo suka isa asalin harabar gdan inda zata sadasu da asalin cikin gdan Hajja Kharimatu tayi tsalle ta rungume Juhud tana dariya tace “wayyoh dadi ga yata ga jikata. Narkewa tayi a jikinta tana murmushi suka zube a falon kafin kace wane wannan falon ya cika maqil da yan uwan mahaifiyarta kowa ta kalla fuskar Innatu take gani a fuskarsa ta share hawaye tace “na yarda na dawo cikin gatana cikin ahlina

Wani dattijo dake shigowa yace “kuma bazaki qara barin ahlinki ba har gaban abada Qanwa inayi miki barka da dawowa cikin zuri'armu bayan wahala da mukasha ta dogon lkc akan neman inda zamu samoki"

Kumbo Hami ce ta nuna matashi tace “tashi kije ga kakanki Meenah yayi kukan boye yayi na fili saboda rashinki ke kadai duk jikokinnan da suka kewayeshi" miqewa tayi da sassarfa ta Isa garesa ya rungumeta yana shafa bayanta tana kuka Yana hawaye yace “tsarki ya tabbata ga ubangijin daya rayani har naga Aminatuh na a raye cikin aminci" janta yayi suka zauna yace “naji quncin watsi da nayi da mahaifiyarki hakan ya jawo tabarbarewar komai naso na gana da Aishatu kodon na nemi gafirarta ita da mahaifiyarta ubangiji bai nufa ba saiya kawomin ke madadinta ajiyar numfashi tayi shima ya aje numfashi nan sukayita hidima da ita da Muneefanta har dare sannan aka kaita makwancinta sashine guda da yasha kyau da gyara sosai part din ya qayatar da ita Saida Kumbo Hami ta dafanta ruwan zafi ta gasanta jiki sannan ta qyaleta ta kwanta bacci kuwa me dadin da ta dade batayi irinsa ba ranar shi tayi.

Haka rayuwarta a Mali taci gaba da kasancewa cikin annashuwa dangin mahaifiyarta daga mazan har matan da yayayensu sunata nannan da ita sai janta sukeyi da nuna mata gata ta kuwa saki jikinta sosai duk da zuciyarta bata nutse guri daya, kaso mafi rinjaye na sinadarin tunaninta yana ga Rasheed Wanda kullum saita Kira wayar Mom taji Ifyrsa Abu daya take fada mata jiki ana samun sauqi itakam tanason sanin wanne irin sauqi ake samu gashi Kumbo Hami ta kasa ta tsare ta hanata wani motsi koda tasamu Baffa Garbu kakanta da mgnr tanason zuwa Nigeria don ta gano jikin Rasheed hanata yayi gashi shima Kareem yaqi Ify an fada mata ma Addah ta dawo masa da Zahra Amma don masifa yaqi qyaleta batasan inda yasamu number data sake ba kusan kullum sai ya kirata da farko Yana bata tausayi idan yana fada mata halin da yake ciki so batason yasa mata kokwanto akan qudurinta ta qudurce ko zatasha wuya zata rayu da Baffa'am dinta shi kadai a mind dinta domin yafi kowa cancanta da ragamar zuciyarta. Bata cikason takura ba hakan yasa sometimes tana ganin kiransa takeqin dagawa musamman data fahimci sosai Kumbo Hami ke fushi da ita duk ranar data fahimci sunyi waya da Kareem, Muneefah nata girmanta kwanci tashi har taci wata biyar da haihuwa Ikcn tuni Juhud ta hada iddarta hankalinta ya kwanta tayi wani matsiyacin kyau mai rikita isassun mazaje duk inda ta juya ido akanta yake a daidai Ikcn ne Kuma kawai Baffa Garbu ya shirya musu tafiya shaqatawa qasashe biyar don sangarta harda wani bata zabi su hudu zasuyi tafiyar shi Kumbo Hami Naila daya cikin jikokinsa sai ita Meenah da yarta Muneefah.

Yanayin yanda suka tsara tafiyar ne yasasu dole Saida suka bi ta Nigeria Kuma ma ba yini zasuyi su tashi ba sai sun kwana biyu qusqus taji sunayi wai zasu barsu a masauki suje Katsina su duba Rasheed daya dawo gida shekaran jiya, ai tanajin haka ta tubure musu kuka baji ba gani dole don basusan bacin ranta suka aminta suka shirya tafiyar da ita tanata murna zataje taganshi tare da addu'ar Allah yasa ya warke sosai tunda suka shigo gdan a mota taji gabanta na faduwa sunayin parking ta daga kanta ta ganshi tsaye saman benen part dinsa corridor din

daya zame masa tamkar gurin shaqatawa yanajin nishadin tsayawa a wannan guri musamman idan wani abu na damun zuciyarsa.
Suna tsayawa ta zame batare da ta jira sun fito ba ta saba Muneefah a kafadarta ta nufi hanyar shiga part din nasa cikin saa a bude yake ta shiga ta nufi inda zai sadata da corridor din ta haura da sauri fadi takeyi “Baffa'am wayyoh Baffa'am dina miss you too....." Tsayawa tayi a bayansa ta dafa kafadarsa tace “ayyah dai ubana yafi na kowa alfaharina a duniya bama haka dakai fah"  juyowa yayi ya kafeta da idanunsa dake cikin glass baqi ya cije lebensa har Saida suka fashi ya kama hannunta ya cire daga kafadarsa ya furzar da iska ya juya yabar gurin, binsa tayi cikin muguwar kidima tana Kiran sunansa baiko juyo ba Saida ya dangana da dakinsa
[8/21, 8:19 PM] Oum Hairan: Yana shiga tabisa dakin ya tsaya idanunsa na kanta yace “kije kawai banson hayaniya" dubansa takeyi da yanayin rashin fahimta tace “Ya Rasheed nice fah Meenanka" sake daure fuska yayi ya zura hannunsa cikin aljihun wandonsa yayi murmushinsa na isa da indai yayishi tasan ya shiryawa rashin mutunci yace “eh na ganeki fah Juhud Meenah Aminatuh Mom Sarki junior kinsan nasanki nasan wace ke fiye da sanin da kikayiwa kanki? Koda yake ba abin mamaki bane canzawar mutum cikin qaramin taqi Meenah kiyiwa Allah ki ficemin a daki kada kisa ruwa na ya hau wlh banson ganinki...."
Idanunta sosai ya ciko da hawaye ya fara tsiyaya a fili tace “meye nayi maka?" Zaburowa yayi kamar Wanda ta bugawa wani abu yace “zanc...." Sai Kuma yayi shiru jikinsa na Bari yace “ki fice nace da gaske ban qaunar ganinki Meenah kinci amanata kin ha'inceni kin yaudareni kin nunamin Babu wanda kikeso samana ashe qarya kikeyi dama ce kika kasa samu Ikcn da kikaga Babu idona kika dauko zabinki kika maye gurbina dashi Abu mafi ciwo wai qanina Meenah Ina raye ki auri Kareem Kuma ki dawo ki fadamin me nace meye zaki fadamin....."
Ya qarasa mgnr da ihu ta dago idanunta da tun kafin ya fara mgnr suke tsiyayar da hawaye tace “wlh ba laif....." Dauketa yayi da Mari yace “idan na qara cewa ki fita kikaqi Tabbas gangar jikinki zata riga Rana faduwa Meenah a yanda nakejin tsanarki tsaf ko zaa kasheni zan iya kasheki" juyawa tayi jikinta a mace bata taba tunanin haka daga gareshi ba tayi tunanin kamar yanda take a baya yafi kowa fahimtarta da bata Ikc yaji damuwarta ashe yanzun ta canza zani ba haka abin yake ba “to kodai bai gama warkewa ba?" Abinda ta tambayi kanta kenan Ikcn da take tafe kamar mahaukaciya zuciyarta na tafasa gabadaya duhu take gani a idanunta batasan inda take jefa qafarta ba.

Qara ta saki Ikcn data buga kanta jikin bishiya batare data sani ba tayi baya zata Fadi Kareem dayaketa mata mgn tun dazun ya tareta ta fada hannunsa tafi minti biyar komai Yana juya mata kafin duhun ya yaye ta bude idanunta ta zubasu akansa ta janye dasauri tare da gyara riqon yarta tace “tnks" daga haka ta juya taci gaba da tafiya yabita yace “Meenah Ina gurin Aiki akacemin kinzo nazo dominki ki tsaya Mana mu gaisa" hawayenta ta dauke ta juyo ta dubesa kamar zatayi mgn sai yaga ta dago Muneefah ta miqa masa yasa hannu ya karbi yarinyar ya cillata sama yanajin muguwar qaunarta na zaga ruhinsa Wanda ya tabbatar da tasamo asali ne daga qaunar da yakewa mahaifiyarta.

Juyowar da zaiyi yaga gurin wayam Meenah har takai qofar falon gdan ya bita da sauri yana kiranta Amma ko juyowa batayi ba ta fada dakin Mom ta zube a jikin Kumbo Hami ta rushe da kuka tace “dama saboda irin wannan ranar nace abarni na rayu ni kadai bazan aure ba aka kasa fahimtata yanzu ga irinta nan Ya Rasheed yaqi saurarona tuhuma yakeyi da naci amanarsa Kumbo wlh banci amanarsa ba ki fahimtar dashi ki zai gane....." Gabadaya hankalin Kumbo Hami ya tashi ta qufula an taba mata zuciyar cikarta daidai Ikcn Kareem ya shigo suka kalleshi Meenah ta kawar dakai ya zauna Yana share gumi yace “meye ya faru Kumbo?" Qwafa tayi tace “yo Wagga sakarar yarinya damuwarta tana wucce ta Abdulrasheedu ne komai Rasheed Komai Rasheed aiga irinta nan ga wulaqancin da kika jama kanki nan da kinyi zamanki a Kanon gdan Barrister Kabir aida baisamu damar cin mutumcinki ba"

Jinjina kai Kareem yayi yace “ayi hqr Kumbo kinsan halinsa shi dama fahimtarsa ba daidai take data mutane ba ni kaina gaba yakeyi dani a gdannan akan abinda bamu Isa mu canzashi ba Kumbo ya zanyi da rabon Muneefah ne dake tsakanina da Meenah itanma da taqini take kallona a matsayin maci amanar dan'uwa ya zatayi da ita wlh na tabbata inda Mai Martaba bai hada auren nan ba ko ta wacce hanya sai Muneefah ta fita ajikina ta shiga nata Kuma saita haifamin ita tunda haka qaddarar take a rubuce"
Shiru ta ratsa ta dogon Ikc Kareem ya dago ya dubi Juhud da har yanzu take kwance jikin Kumbo tanata matsar hawaye ya miqe yace “kiyi hqr komai zaizo qarshe Allah shine yasan abinda ke cikin qasa a binne" daga haka ya fice a dakin dauke da Muneefah ya nufi gidansa da ita Zahrah tana ganinsa da yarinyar ta zabura ta miqe ya dubeta ya kawar dakai itama saita waske ya shiga kitchen ya daukowa yarinyar biscuits da yourghut ya zauna Yana bata yana murmushi dadi yakeji a ransa rabonsa da ita tun tana jaririya gata har ta tafi shekara guda ji yake dama ace mahaifiyarta ce a gefensa.

Share hawayen daya tsiyayo masa yayi Zahrah na kallonsa tana kada qafa takaici yana qara kamata tace “waikai yar wace ka dauko?" Murmushi yayi yace bakisanta ba ko?" Tabe baki tayi tace “ya zaayi nasanta tunda baa cikin ahlinmu ta fito ba" sake kallon Muneefah yayi yace “qwarai kuwa baa cikin ahlinku take ba tunda kinada ikon canzata daga jinina Zahrah na dade da fahimtar Ina kika dosa koma dai meye a ranki kibi a sannu domin Aisha itace ya babba a gurina Kuma ko zaki haifi duniya bayanta zasu biyo abu na qarshe da nakeso ki sani a aurenki ma arziqin Meenah kikeci saboda haka ki taka a sannu"
Tashi yayi ya dauki yarsa ya nufi hanyar ficewa daga gdan tayi dariya tace “iska kuwa na wahal dame kayan kara wahalalle Meenah dai tafi qarfinka saidai kaganta ka hanga kayi sake dan zaki ya girma me ita ya dawo son maso wani qoshin wahala"

Bai saurareta ya tsaya bata Amsa ba ya fice ya nufi wani shop yayima yarsa siyayya ya juya ya koma gdan sarautar har sun shirya suna zaman jiran dawowarsa domin Alh Garbu yace ba kwana zasuyi ba a ranar zasu koma Kano Meenah bataso haka ba taso ta samu cikakken lkcn fahimtar da Baffa'am dinta gskyr lamari Amma batada wannan damar, tana kallonsa Yana kallonta ya dawo daga yawonsa a mota sukayi sallama da Kumbo Hami da Alh Garbu itakam ko kallo bata isheshi ba  wani takaici ya cika mata zuciya abin nasa harda wulaqanci juyawa yayi yayi tafiyarsa tabisa da kallo ta girgiza kai ta shiga motar suka tafi tana waiwayensa hankalinta baimakai ga Kareem da yaketa daga mata hannu ba.
Suna tafe tana furzar da iska a haka suka Isa Kano goma na dare suna Isa gdan da suka sauka ta shige daki ta kwantar da Muneefah dake bacci ta zauna zaman karatun wasiqar jaki batada mafita ta miqe ta shiga bathroom ta watsa ruwa ta dawo ta kwanta bacci ya gagareta sai juyi kawai da takeyi cikin dare ta lalubi wayarta ta fara neman layinsa ta kasa jurewa Kira biyar tayi baa dagaba ta rubuta masa gajeran saqo na ban haquri, tana qara Kira taji wayar a kashe taja fasali ta kashe tata wayar ta zubawa Muneefah idanu tana sharar kwallah Tabbas duk abinda yasa Rasheed daukan wannan matakin akanta ba qarami bane, da wannan tunanin bacci ya dauketa da asuba ta tashi suka fara shirye²nsu domin tashi zuwa Dubai, Tara suka tashi itadai badon tanajin dadin komai ba donma Naila tana dauke mata hankali da dan karen surutunta.

Kumbo Hami ta fahimci abinda yake damun jikar tata koda suka isa dinma bata wani saki jiki ba har suka Isa masauki sukayi sallah sukaci abinci sukayi wanka kowa ya nemi makwanci sai dare suka fice daga masaukinsu, suka shiga gari itadai Meenah yaqe kawai takeyi lkc zuwa lkc tana gwada layin Rasheed Amma har yanzu yaqi dagawa har dole tasa ta saduda ta qyaleshi.
Sai asuba suka koma gda sukayi sallar asuba suka kwanta rayuwar taci gaba da gudana a haka baqin naci ya hana Juhud daina kiransa shikuma yaqi dagawa kamar yanda Kareem yake nacin kiranta itama tana jizgashi idan abin ya dameta saidai ta Kira Ya'isha tasa mata kuka tace ta tayata bawa Baffa'am dinta hqr saidai Ya'isha tayi murmushi tace “wlh Meenah baqin kishine yake damun Ya Rasheed Amma Ni shaida ce bai daina sonki ba" da haka take dan kwantar mata da hankali  take samun nutsuwa.
Satinsu biyu suka daga zuwa Malay daga Malay sukayi India daga can sukayi Saudi sukayi Umarah daga nan sukayi Turkey daga Istanbul suka gangaro Nigeria daga Nigeria suka zarce Mali, watanni hudu suka kwashe a yawon nasu suna dawowa suka shiga bikin Naila da Hameen dake abin duka na family ne yayi armashi sosai.

Mom ita da Ya'isha da Aunty Hamida duka sunzo tunda sukazo take maqale da Mom tanata zubanta shaqwaba washegari suna gurin dinner Rasheed ya dira a qasar Basu dawo gida ba

sai wajen 12:30am suna kowa baccine akansa tana shigowa tana cewa “ni Allah Mom badon kin takura ba bazanje wannan dinner ba gara na kwanta nayi chat....." Mgnr ce ta maqale mata Ikcn da idanunsu ya sarqe ana juna ya wani maze tunaninsa zatayi masa mgn ga mamakinsa sai yaga taba banza ajiyarsa ta Kara wayarta a kunne tana cewa “double sorry na shiga yanayine wayar na jakka bansa ka kiraba sai yanz...." Iyakar nan Rasheed yaji ta shige daki yaji gabansa na mugun faduwa ya dubi su Mom da suketa faman dariya ita da yan'uwanta ya miqe zuciyarsa na tafasa yace.
“Gobe da wuri zan wucce Ghana ba lallai mu samu haduwa ba" bai jira amsar Mom ba ya fita ya ishe Alh Garbu da fadawansa sunata hira gda kamar kasuwa ya lura suma dabi'ar qasar kamar basa bacci sosai da dare, daquwa Alh Garbu yayi masa yace “dan boko dan qaniyarka shine ka shige cikin mata ga qannenka da yayyaenka da iyayenka duka bazakazo cikinsu ba" yaqe kawai Rasheed yakeyi ya isa garesu ya gaishesu wasunsu da yawa yasansu qannen Mom ne wasu Kuma jikokin gdanne nan aka baje sabuwar hira Nan Alh Sulaiman babban yayan su Mom ya kaikaice yace “Alh dama tun kusan sati uku nakeson yi maka mgn wai ya mgnr yaran nan Najeeb da Ameenah....." Tunda ya Fadi haka Rasheed ya zubansa ido duk da baisan wacce Aminan ake nufi ba Amma yaji saukar saqon faduwar gaba.

Zubansa idanu Alh Garbu yayi Yana nazarinsa can yayi murmushi yace “to ai lamarin Aminah ne akwai rikitarwa kaga mijinta na farko ko igiya daya bai yanke mata ba nemansa akayi aka rasa shari'a tabata damar aure ta auri qaninsa shikuma qaddara ta rabasu da saki daya to mijinta na farko din ya bayyana Kuma tanasonsa shima na shaida yanasonta wani dalili ne ya hanashi magantuwa saboda haka indai sunason juna to sunfi dacewa da juna wannan dalilin yasa nace da Najeeb ya hqr wannan abu duk na gidane dashi da Rasheed duk jikokin gdannan ne rashin zumincinsu yasa basusan juna ba"
Tunda Alh Garbu ya fara mgnr gumi ke karyowa Rasheed baqin kishinsa ya motsa ya dago idanun nan kamar gauta Yana Shirin yin mgn wayarsa tayi ring ya zaro ya duba aqogo daya na dare harta gota ganin number Ya Arman yasashi tunanin akwai dai wani abu daya faru daga wayar yayi ya Kara a kunnensa numfashi ya sauke me nauyi yace “ina Kareem din?" Huci ya furzar yace “Har matarsa aka kashe ko iya shi kadai ne?" Sake jan numfashi yayi yace “ok zan dawo gobe" daga haka ya kashe wayarsa.
Ya miqe ya nufi makwancinsa ya soma safa da marwa Yan fashi sun shiga gdan Kareem sun kasheshi shida matarsa? To akanme?" Tambayar da ya rinqa yima kansa kenan mara Amsa a hankali yaji wasu hawaye sun zubo masa ya nemi guri ya zauna Yana tuno haduwarsu ta qarshe da kalmar qarshe ta Kareem ya fada masa, “Kai dan uwana ne na jini Ya Rasheed a tunanina murna ya kamata kayi da  ya kasance nine na kula maka da iyalanka a halin bakanan ba gaba yakamata kayi dani ba! Ya Kareem har gobe inason Meenah bazan taba daina sonta ba har fitar numfashina na qarshe na hqr da Meenah ne badon zuciyata ta hqr ba saidon bata damar kasancewa dakai domin kaine zabinta, dani qaddara ta rubutawa bacewa ka auri matata idan na dawo gdy zanyi maka badon bana kishinta ba aa saidon nasan ta cancanta ne shiyasa ta zama matar gado cikin ahlinmu"..........

A daren nan Rasheed bai rintsa ba kwana yayi Yana tuna abubuwa da dama da suka faru tsakaninsa da Kareem tun daga ranar farko da suka fara qullah soyayya da Meenah kawo Ikcn daya aureta ta qarfi da irin wahalar da Kareem ya rinqa Sha ta ciwon zuciya duk akanta kawo yanzu yanayin da suke ciki da irin bibiyar da Kareem ya rinqa yi masa akan yayi hqr ya daina gaba dashi sosai yayi kuka da baitabayin irinsa ba a duniya tabbas ya tafka kurakurai masu wuyar gyarawa Kareem baya duniya labarinsa ya shude balle yaje ya nemi afuwarsa akan abinda yayita qoqarin ganar dashi yaqi bashi qofa.
Da asussuba kuwa ya dokawa Mom Kira itanma yanda ya kwana haka ta kwana saboda tun Daren itama aka fada mata abinda ke faruwa Meenah kam batasan meke faruwa ba Amma ranar ta kasance cikin wani yanayi domin a daren waya sukeyi da Kareem Yana mata wasu kalamai data kasa fahimtarsu can taji yace “Meenah kada ki manta wannan wlh tallahi duk duniya nafi kowa sonki ban barki don biyayya ga umarnin Addah ba nabarki ne don nasan kedin banine a zuciyarki ba Meenah in son samuna ne Muneefah ta rayu a qarqashin kulawarmu ni dake nasan hakan bazata samu ba wani abu yana gaf da faruwa dani, Ina kukan rabuwa da abubuwa biyu da nafi qauna ke Meenah da Kuma yarmu Muneefah Amma a wani sashin Ina farin cikin kasancewar zata rayu da cancanta madadina wato Rasheed Meenah ki komawa Rasheed don Allah don taimakon maraicin Aishatuna kinji......" Daga haka ya tsaya da mgnr taji wata qara can taji yace “ina zuwa zan kiraki kamar Yan fashi sun shigo unguwarmu" daga wannan tajishi shiru kalamansa sun tsayanta a rai zuciyarta ta karye tabbas lamarin Kareem akwai taqawa da tsoron Allah baitabayin Abu don jin dadin kansa ba komai zaiyi yanayine don mafitar Al'umma Kareem yakai masoyi a gurinta.
Miqewa tayi zumbur Ikcn da taji Ya'isha ta rushe da kuka tana cewa Innanillahi wa Inna ilaihir raji'un Allahumma ajirni fih musibati Mom da gaske Ya Kareem sun kasheshi ya mutu shikenan bazai qara dawowa duniya ba Muneefah ta zama marainiya....."

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane ki biya 300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/22, 8:04 PM] Oum Hairan: Da mugun gudu cikin fitar hayyaci Juhud ta fito daga dakin da take cikin gigita ta cacumi Rasheed dake shigowa idanunsa kamar garwashi ta jijjigashi tace “da gaske ko gizo kalamin Ya'isha sukemin Ya Kareem ya mutu....." Zubanta idanunsa yayi so yake yayi mata mgn ya kasa sai kawar dakai da yayi hawaye suna zubo masa yasa hannunsa ya janye nata, ganin yanda yake goge hawaye da tissue yasata zama a gurin dabar ta daura hannunta akanta ta rushe da kuka tana cewa Innanillahi wa Inna ilaihir raji'un" Ya Kareem kada ka mutu dom girman Allah ya kasance mafarki shudadde Wanda bazan qarayinsa ba har abada wlh na aminta da kai zan dawo gareka na qara Haifa maka qannen Muneefah nasan shin....shine burinka a duniya....." Dagota Mom tayi tace “kiyi hqr Meenah shirya mu tafi" Babu wani shiri ta sunkuci Muneefah da taketa bacci abinta baccin asara abin tausayi mota ta debesu gabadaya harda Alh Garbu suka nufi airport dake abin na manya ne nandanan suka Isa Nigeria kamar a qasar suka kwana goma na safe suka shiga Daura lkcn an gama shirya Kareem da Zahrah zaayi musu sallah mazan suka tsaya wajen jana'izar sukuma suka shige ciki.

Addah Abulle tana ganin Juhud ta miqe ta nufeta da sauri ta karbi Muneefah ta rungume ta qara rushewa da kuka tace “shikenan ya tafi Meenah yatafi yabar Mana duniyar Babu shi din Babu Zahra wayyoh Kareem dama inada dama Dana dawo dakai duniya nabarka da zabinka da yarka daya mafi soyuwa a ranka kullum kana fadamin bakajin dadin rayuwa baka tare da Muneefah ashe ita kadaice rabonka ita zaka tafi kabarni da ita Kareem wayyoh Ni Zainabu na cuci kaina na cuceka Kareem Allah na gde maka da bakabani saa ba lkcn da malam Mati yabani magani yace nabaki kici a waina da tuni Babu Aishatu da tuni Ni da kaina na kashe bayan dana kaicona Ni Zainabu Allah ya isa Dada Hanne da Hajiya Bilki kune kukayita dorani a keken bera ashe kaini zakuyi ku baro yau na rasa Kareem ban barshi ya rayu da farin ciki ba ya tafi da jin ciwon nice silar rabashi da matarsa mafi soyuwa a duniyarsa...."
Surutai taketayi kamar wacce ta zautu hakan yasa wasu mata daga cikin danginta sukazo suka kamata suka tafi da ita daki tana kuka tana kiran Meenah Kareem shikenan Kareem ya tafi yabarmim duniyar Ina nutsuwata da hankalina yayi na kasa gane nauyin qaddararsa?" Kowa ka gani a falon kuka yakeyi mutuwar Kareem tabar tambari ba iya Daura ko Katsina kadai ba hatta arewacin Nigeria baki daya duk Wanda yaji labarin mutuwar ko baisanshi ba sai yaji alhini a jikinsa duniya tayi rashin nagartaccen mutum me hqr da kawaici kunya da kara wannan dabi'ar tasa yake soyuwa a zuciyar duk wanda yayi mu'amala dashi ta kusa kota nesa ranar anyi yinin alhini Juhud kam zazzabi ne ya rufeta sosai bana wasaba hawaye yaqi tsayawa a idanunta tayi danasanin zabar Rasheed akan Kareem ta zabi Rasheed tabar Kareem Rasheed din ya

tattarata yayi watsi da ita yaqi saurarenta.

Haka suka yini yinin koke² da dare kowa ya nemi guri ya kwanta itakam koda ta kwanta kasa rintsawa tayi rayuwarta da Kareem zamantakewarsu da yanayin salon qaunarsa me tsayawa a rai shudaddiya wacce bazata dawo ba tanayi mata yawo a kwanya saidai kawai lkc zuwa lkc ta dauke hawaye, wajen 10:30 taji ana taba qofar dakin data shiga ta kulle kanta ta miqe a wahalce ta bude ta dan ja da baya a tsorace ganin Rasheed ne jajayen idanunsa akanta ya miqa mata Muneefah da tayi bacci tasa hannu ta karbeta ta juya ta nufi cikin dakin taji muryarsa data shaqe da alamun yaci isasshen kuka yace “Duk da bansan irin radadin da kikeji a zuciyarki ba na rashin masoyinki uban yarki nasan kinajin fiye da abinda nakeji tabbas akwai daci daci mafi dacin daci rabuwa da abinda kakeso a lkcn da kake tsananin buqatarsa yaune kika farajin kwatankwacin abinda naji lkcn dana rasa hanyar dawowa gareki kwanyata ta daina fadamin daidai aka rinqa nunamin ke cikin wani yanayi dana kasa ganewa har yanzu and end aka nunamin ke wani mutum ya hankadaki cikin wani dogon rami Wanda na yanke shawarar binki mu mutu tare Meenah bayan na biki bansake sanin komai da hankali zai tuna ba sai bayan shekara bakwai dinnan Amma ko a cikin yanayin zautuwar qwaqwalwata ban mantaki ba duk wani furucina kece bansan ya ake tunani ba Amma idan na zauna kece kikemin gizo da siffofi mabambata"
Numfashi ya sauke ya juyo idanunsa na zubar hawaye yace “meye kike tunani ranar da Allah ya Amsa addu'ar masoyana ya dawo dani hayyaci na laluba naga bakinan na tambayi kina Ina akacemin kina matsayin matar wani waninma qanina Meenah taya zan iya yafewa kaina bata lkcn da nayi na nakasa rayuwata saboda ke? Nakasa yafewa kaina kema na kasa yafe miki girman cin amanar da nakeji a Raina kinyimin domin bana mantawa kintaba yimin alqawarin zamu rayu tare zamu mutu tare ya akayi tun Ina raye kika zabi rayuwa da wani bani ba?"

Duk da kalamansa sun kashe mata jiki Amma yanayin da take ciki yasata juyowa a fusace tace “qaddara Abdulrasheed dukkanmu akanta muke rayuwa Babu Wanda ya isa ya tayani dakon tawa kamar yanda Babu Wanda ya tayaka Babu Wanda ya taya Ya Kareem Allah madaukakin Sarki ya sardanta ku biyun daka kuna cikin qaddarata kaine kakeja da lamarin ubangiji ni bana jayayya Ya Kareem ma baitaba jayayya ba kullum nunamin yakeyi bayin kansa bane girman rabone da hukuncin Allah saiya Sanya Muneefah tsakaninmu Kuma na dade da sanin tun baya ma shine akan daidai kai kana rayuwa ne a doron son zuciya saboda haka Baffa'am tun da sauran mutuncinka a idanuna ka fice cikin rayuwata kafin na keta alfarmarka na shiga nayi fata² da qimarka Meenah daka sani a baya ba ita bace yanzu yanzun Aminatuh ce a gabanka me taqama da asali kyawun nasaba arziqi da ilimi kada ka manta bayan tafiyarka na samu shahadar zama Barrister Aminah Haroon Moddibo so nasan yancina banason kowa cikin rayuwata ta yanzu"

Shigewa tayi daki ta banko qofar ta murda mata key ta haye gado ta zubawa yarta ido tana mata tunanin rayuwarta ta gaba babu bangonta na farko kwanciya tayi bacci ya qauracewa idanunta kamar yanda ya qauracewa idanun Rasheed sosai yake jujjuya kalamanta ya rasa a ma'aunin dazai sanyasu ta fada masa kalamai masu wahalar gogewa a zuciya tabbas shima saida ne daga yanda ta watsar dashi da lamuransa na rayuwa yasan tabbas da gaske ba Meenan daya sani a baya bace, to Amma meye yasa ita ta kasa gane tayi masa laifi me girman daya dace duk hukunci ya dauka akanta?
Busar da iska yayi ya gyara kwanciyarsa tare da dauko takardar da Mai Martaba yabashi dazu dazai shigo bayan ya fito daga dakin Meenah yace Kareem ne yabashi yace abashi kafin ya rasu. Tashi yayi ya kunna haske zuciyarsa na bugawa ganin yanda takardar ta bushe da jini ya warwareta ya fara karantawa da larabci yayi rubutun fassararsa kamar haka.
_“Assalamu Alaika ya dan'uwa mai albarka na rubuta maka wannan takarda ne a lkcn da Raina yake tafiya ga ubangijin daya halicceshi, badon komai ba saidon inason na qara baka hqr akan laifin da kake tunanin nayi maka na auren matarka Allah yasani ban aureta don cin mutumci ko tozarci a gareka ba, Ni Abdulkareem Mahfuz na zabeka na mallaka maka amanar yata qwaya daya tilo ta zama taka dama nasan takan ce don Allah Abdulrasheed kada kabari Meenah da Muneefah suyi kukan rashina musamman Muneefah ita kadai gareni Kuma na mallaka maka ita halak malak"_

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏽 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/23, 7:30 PM] Oum Hairan: Matse takardar yayi a tafin hannunsa jikinsa Yana tsuma zuciyarsa nayi masa wani zugi ya miqe a gadon ya rinqa zagaye dakin nasa a tsarinsa na gaskiya ji

yakeyi kamar bazai iya sake zama da Meenah ba yanajin ciwon abubuwan da suka faru a baya so yanzu ya zaiyi da wannan nauyin da Kareem ya dora masa a halin yana gargarar mutuwa? Tambaya ce da yakasa amsawa kansa ita dole akwai sarqaqiya cikin wannan al'amari komawa yayi ya kwanta ya kasa bama kansa mafita sai zafi da zuciyarsa takeyi kawai.
Abu daya da yasan ya zame masa dole shine daukar amanar Muneefah da Kareem ya damqa masa to Amma ta yaya zai karbeta a gurin mahaifiyarta bayan yasani yanajin yanda shaquwa take tsakaninsu ko giyar wake Meenah tasha bazata bashi yarta ba, da wannan tunanin ya samu bacci ya dan daukesa da safe yana fita falo ya ishe kowa suka gaisa yanata raba idanun ganin Meenah Babu alamarta hakan ya tabbatar masa tana dakin daya isheta jiya yaja fasali ya dubi Amrah yace “shiga ki daukomin Muneefah" miqewa tayi ta nufi cikin dakin ta tarar Meenah tayima yarta wanka tanayi mata kwalliya ta zauna suka gaisa tace “Big Cele yace akawo masa Muneefah"
Bataso ba saidai batada ikon hanawa ta gama shiryata Amrah ta riqema yarinyar hanu suka fito ya dauketa suka fice daga falon Mom tana kallonsa batace masa komai ba, kwanaki bakwai din da Meenah sukayi suna karbar gaisuwa ta fahimci abubuwa da yawa sosai Addah Abulle tayi laushi batada aiki sai kuka tunda ta haifi Muneefah bazata iya cewa ga ranar da Addah ta dauki yarinyar ba sai cikin kwanakin nan da taketa nan nan da ita danma Rasheed ya hanata sakat akan yarinyar duk wani motsin da Muneefah zatayi tana gareshi.

Kwanaki goma da rasuwar su Kareem bayan komai ya fara nutsawa Meenah da Kumbo Hami suka fara Shirin tafiya Rasheed baisan me akeyi ba sai a daren da zasu tashi Mom ta kirasa Ikcn bai dawo daga yawonsa ba kasancewar har yanzun bai koma bakin aiki ba yana hutune take sanar dashi su Muneefah zasu tafi, Saida yaji wata faduwar gaba yace “tafiya Kuma Mom na zaci sun dawo kenan?" Murmushi Mom tayi tace “basu dawo ba to yanzu haka ma Shirin kaisu airport mukeyi" tana Fadi masa haka ta kashe wayar ta dubi Meenah da hankalinta take kan Sarki junior da yaketa kukan sai yabita itama hawaye ta share tace “makarantarka junior kabari idan akayi hutu zanzo ko na turo a daukarmin kai kaji" daqyar ta rarrasheshi ta samu ta sulale ta shiga mota suka tafi abin mamaki wai harda Addah ayi musu rakiya ashe dama tunda suka rabu da Mai Martaba tayi aure batafi wata biyu ba ta kasoshi tanason Mai Martaba ya dawo da ita dakinta shikuma yaqi.
Ko a airport din daqyar aka karbi Muneefah a hannunta tanata kuka so take ta roqi alfarmar abata yarinyar take gani ko ta rinqa samun sauqi Amma tsoro ya hanata furtawa saboda ta fahimci suma dangin uwarta sunason kayarsu da hakadai jirgin su Meenah ya daga sukuma suka juya domin komawa inda sukafi wayo cike da kewar juna.
Wannan tafiya ta zamewa Rasheed tamkar famin tsohon miki a cikin zuciyarsa abubuwa sun fara dawo masa sabbi duk da cewa izza da dagawar da Meenah ta rinqayi masa ta girgizashi baitaba tunanin akwai juyin da duniya zatayi Meenah ta rinqa kallonsa watsi dashi kamar tunda Allah yayita batasan anyi ruwansa ba.

Wata biyu abubuwa suka zama tarihi akaci gaba da cudawa kamar yanda aka saba kowa yasa abinda yake gabansa a gaba Rasheed ya koma aikinsa gabadaya sun ajeshi guri guda a Lagos inda kullum tunaninsa zuciyarsa da ruhinsa yake Mali gashi tun a farkon da abubuwa suka lalace da Meenah ta rinqa kiransa yayi block na numberta itama tayi block nasa koya nemeta baya samunta wannan tasa dole ya nemi sabon layi dal saboda zuciyarsa taqi sabawa da rashin sauraro da jin abinda zuciyarsa take muradi saidai rashin saar da yayi daya Kira sai yaji layukan dukka a kashe girman kansa na masifa ya hanashi tambayar wani cikin yan'uwansa layinta yabari akan cewa idan ya koma yasan yanda zaiyi ya sata a wayar Mom.
Hakan kuwa akayi bai iya hqrn wata biyun da yayi niyyar yi a Lagos ba ya dauko hanya ya taho Daura bayan ya huta da dare suna hira da Mom a dakinta tanayi masa fadan zamansa haka yayi murmushi yace “mom kamar akanki nake duk kinbi kin damu nayi aure" jinjina kai tayi tace “to ai Rasheed nidai naga cikar kamalar mutum shine hade kansa da iyalansa guri guda kai Kuma na rasa inda kanka yake kunqi ku daidaita da yar'uwarka Meenah Kuma ka kasa samo madadi jiya ma Baffanmu yakirani yake tambayata akan lamarinka da Meenah ance mata aure tace karatu ance ta dawo hannunka tace har abada kaima ya tuntubeka kayi masa shiru wai meye yake faruwa ne"

Goge gumi yayi ya gyara zamansa yace “ni bawai Meenah ce bazan dawo da ita cikin rayuwata ba aa Mom abubuwa ne sun kasa gogewa a mind dina Kuma na fahimci kamar itama ba nine a gabanta ba yanzun" murmushi Mom tayi tace “hakane bakai ba aure ne ma bakidaya bashi gabanta so Amma idan kaje zaku iya daidaita kanku" shiru yayi yana nazartar kalaman Mom tace “zanji dadi idan hakan ta faru Rasheed Meenah tanasonka kanason Meenah ga yaranku guda biyu baikamata ku Bari shaidan ya raba kanku ba babu wanda ya isa cikinku ya canza wannan qaddarar kama godewa Allah da rabon Muneefah bai kasheka ba Rasheed rabon ya mace zafi gareshi shiyasa kullum yanada kyau karinqa yima kanka addu'ar Allah ya rabaka da auren mace me yayan wani a cikinta duk son da kake mata idan rabon nan ya yunquro to sai dayan biyun ta faru kodai a rabu ko Kuma a mutu"
Jinjina kai yayi jikinsa ya qara sanyi abinda Kareem yayita qoqarin fahimtar dashi kenan ya kasa fahimta yau kam ya gane Kuma ya fahimta wayar Mom ya dauka ya fice daga dakin nata ya shiga mota ya nufi gidansa ya shiga ciki Saida ya dangana da dakin baccinsa ya cire kayansa ya fada bathroom yayi wanka ya dawo ya kwanta gabadaya dakin manyan hotunansa ne shida Meenah saina yaransa Sarki da Muneefah ya zubawa hotunan idanu a fili yace “lkc yayi da yakamata da dawo da farin cikina" wayarsa ya dauka ya Kira Abokinsa Kamil suka gaisa yace masa “cikin satinnan kana free ne?" Amsawa yayi da “eh" yace “ok zamuje Mali ne jibi" bai boye masa komai ba khamil yayi dariya sosai yace “tsohuwar zuma kishin ya gushe kenan?" Ya lura tsiya ya shirya yi masa don haka ya kashe wayar ya dauki ta Mom yanabin contact din ya lalubo number ya danna kira lkcn tana sallar Isha Muneefah ce tana wasa da wayar ta danna tana gwarancinta yayi murmushi yace “daughter bakin yazo kenan?" Nan

sukayita shirmensu da yarinyar bayan ta idar ta karbi wayar tunaninta ko Muntaz ne ko Urwat tace “surutu ke gareta Mamana bata rabo da rigima" ajiyar zuciya yaja a hankali taji ya sauke numfashi yace “hakan yanada kyau ba lallai tayi kamar na Mom dinta ba" qamewa tayi a gurin jin muryar da batayi zato ba nandanan ta rinqajin zuciya na ayyana mata ta kashe wayar tana Shirin gimtse layin taji yace “ranar juma'a idan Allah ya amince zan shigo qasar ki fara Shirin zama amarya domin bazan kwana a garin nan ba saidake matsayin matata kamar yanda yake rubuce a allon qudura duk wanda yayi karambanin shiga wannan gonar ma saiya fice da kansa ko Kuma dole ta fitar dashi"

Murmushi tayi tace “tunaninka ne yake baka hakan nikuma inajin a raina qaddarata tayiwa taka nisa Ya Rasheed so don Allah kada mu wahalar da shari'a kayi zamanka a inda Allah ya ajeka idanma matsuwa akayi nayi auren naji zan fitar da miji tsakanin yau da gobe Amma kaikam nagama aurenka" murmushi yayi yace “au haba da gaske Kuma kikeyi? To ai kin manta da Abu daya ni idan nayi niyyar aiwatarwa yuwuwa yakeyi Meenah badon kanki da kaina ba don rayuwar yaranmu nayi niyyar abinda na furta saboda haka kada ki manta gyarane kawai Amma kedin matata ce domin da igiyar aurena uku akanki aka jingine aka dauranki wani.... Oh God banaso nake tunawa fah ki share kawai sainazo".......
Daga haka ya gimtse wayarsa yabarta da sakin lebe lallai wannan yazo da izala mara gemu dole ta takansa birki don bataji a ranta wannan tatsunniyar zata yuwu ba.

Ranar kwana tayi tana jujjuya kalamansa da safe kuwa bata sanar da kowa ba ta shirya nata ya nata ta gudu gidansa Aunty Kharimatu batare da kowa yasan inda ta tafi ba Kumbo Hami ta riga tasan me ta gudarwa saboda sunyi waya da Mom a haukan ma da takeyi tuni magana taje ga kakanta ya Kuma amsa har anyi duk abinda zaayi an wucce gurin da sahalewar Mai Martaba.
Tana zuwa gdan Aunty Kharimatu suka lalace da hira har dare tayi kwanciyarta dake mijinta matafiyi ne washegari ma sukaci gaba da harkokinsu har magrib batada niyyar tafiya suna falo suna cin dambum nama sukaji sallamar Jabir gabanta ya Fadi ya shigo yanayi mata dariya yace “girman kujera aunty babba kinada baqi a waje fah" harara ta zabga masa tace “munafuki suwa kak debomin?....." Bata gama rufe bakinta ba sukayi sallama suka shigo idanunsa na kanta ta kuwa hadiye fara'arta ta hade rai ta miqe ta nufi wani daki suka dubi juna shida Khamil sukayi murmushi suka zauna Aunty Kharimatu nata zolayarsa fadi takeyi lallai ango kasha qamshi ashe da gaske kana tafe"
Shafa sumarsa yayi Yana  cire hularsa yace “wlh Ina tafe nazo na dauke matata mu tafi nagaji da zaman gwaurontaka" hararadrsa tayi tace “aa kuwa baka isaba wannan abu Babu shiri nifa sai dazun Kumbo ke fadamin Shirin da akayi nace halan ma waccan uwar taurin kan bata sani ba don ko dazun Saida tace batada muradin wani aure"  numfashi ya sauke yace “tasan komai

ai dama barinta nayi ta huta saboda rayuwar batada tsayi Amma an fuskanci qalubale da suke buqatar dogon hutun brain"...........

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta baney ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/27, 9:03 PM] Oum Hairan: Dariya Aunty Kharimatu tayi tace "ah lallai to ubangiji ya kade fitina ya daidaitaku sai aje ayita hqr koda yake tsohuwar zuma ce Babu wani qalubale qalaunku zaku zauna wuyarta ku daidaita kanku......" Aunty Kharimatu bata gama rufe bakinta ba Juhud ta fito dauke da Muneefah da niyyar ficewa daga gdan Muneefah na ganin Rasheed ta fara zamewa a jikinta tana Kiran Dad sweet Dad biscuits...." Murmushin gefen baki yayi ya miqe ya nufi Meenah da takai bakin qofa yasa hannu zai karbe yarinyar ta juyo a fusace cikin bala'i tace "inada tabbacin bakada wata alaqa data wucce wan mahaifi gurin Muneefah domin kuwa qaddararta me qarfi ce itane ta sanya abubuwa da yawa suka faru a qarshe dai nida Kareem muka Samar da Muneefah saboda haka ikona ce"
Sakin yarinyar yayi yayi baya jikinsa na daukar sanyi yanajin saukar kalamanta na dukan zuciyarsa, batare da wata damuwa ba ta fice ta jefa yarinyar da keta kuka a mota ta shiga ta figi motar a mugun guje ta fice a harabar gdan tabarshi tsaye kamar dashe Yana qara maimata kalamanta, Khamil ne ya dafashi yace "nifa Ina mamakin yanda dangantaka tayi tsami haka tsakaninka da Meenah meye ya farune mutumin bakada dama ne fah qila Kaine ka tabo zuciyarta"  janye hannunsa yayi yace "koma mene ban cancanci wadannan munanan kalaman akan yar qanina ba Amma zan gwada mata haihuwa ce tata nafita qarfin iko" Yana fadin haka ya fice Yana huci ran maza ya baci Jabir ne yazo yajasu suka nufi gda ganin motar da ta hau ta fito yasashi tabbatar da gidan ta dawo, bai shiga cikin ba ya nufi sashin baqin ya cire kayansa ya zauna yana fitar da iska me zafi zuciya na raya masa meye zaiyi ya rama wannan wulaqancin da Meenah tayi masa?

Ya jima bacci bai daukeshi ba sai juyi yakeyi da safe ya fiçe ya nufi cikin gdan Meenah bata tashi daga bacci ba a zahiri ba baccin takeyi ba kawai juyi takeyi, shiga yayi part din kumbo Hami suka gaisa ya wucce bangaren Alh Garbu suka gaisa yayi shiru na dogon lkc kamo hannunsa yayi yace “meye yake faruwa ne Dan Boko?" Qasa yayi da kainai Yana shafa sumarsa can Alh Garbu ya sake dubansa yace bai wucce kace kanason tafiya da matarka ba ko?" Jinjina kai yayi yace “hakane Alh inason jibi idan zan tafi mu tafi gabadaya saboda dawowa zatayimin wahala kusa" jinjina kai Alh Garbu yayi yace “shikenan zan fadawa kakar taku inyaso saisu fara Shirin abinne yazo Babu tsammani Amma fah akwai abinda bazan dauka ba cikin lamarin aurenku duk wani cin Kashi da akayi mawa Aminah a baya yanzu ko ita ta daukeshi ni bazan daukaba" ya jima yana kafa sharrudansa shidai Rasheed jinsa kawai yakeyi har ya gama ya tashi ya fice.

Lkcn da Kumbo Hami taji Shirin da Alh Garbu yayi taso tace aa Amma ya hanata katabus dole hakanan ta hqr tana jiran ranar zartaswa aikam ana samun Meenah da mgnr tayi tsalle ta dire tace batasan zance ba duk Wanda suke tunanin zai fada aji ya fada tayi kunnen uwar shegu Rasheed kam abokin gaba ya zama batako kallonsa bai wani damu ba saidai ya kalleta yayi murmushi ya barta tayi duk abinda yasan na dan lkc ne da lkcn ya wucce shikenan, ana gobe tafiyar da dare ya shiga har dakinta ya tarar da ita itada Aunty Kharimatu da Kumbo sai aikin rarrashinta sukeyi suna ganinsa suka miqe suka fita ya mayar da qofar ya rufe ya nufota ta miqe tsaye ya tsaya Yana murmushinsa na isa tare da zura hannunsa a aljihunsa ya harde qafarsa ya jingina jikin bango yace “banzo domin na baki hqr Kona rarrasheki ba saboda Ni nasan banyi miki laifi ba hasali ma nine nake tuhumarki so inada abinda yafi haka muhimmaci kin fadamin wata mgn ne da nakasa jureta shine nazo baki amsa Meenah yes na amince keda Kareem kuka Samar da Muneefah Amma kada ki manta kafin Kareem ya baki da nine na fara baki na farko kika zubarmin na biyu kika haifamin gashi ya zama saurayi so wannan kadai ya isa ya tabbatar miki ni na wucce kiyimin gatsali akan Muneefah Kuma ko kinaso ko bakiso dole kibarni da ita domin ba saboda ke nakejin yarinyar a Raina ba saboda mahaifinta yayimin kyautarta ne"

Shafa gemunsa yayi yayi murmushin gefen baki yace “shekarar Muneefah daya da rabi ki shirya karbar qaninta kowanne lkc daga yanzun ni bana wasa da dama amfani nakeyi da ita sosai" ficewa yayi daga dakin yabarta tsaye da zubar hawaye takaici kamar ya kasheta taja qwafa ta koma ta zauna.
Duk wani shiri da Kumbo Hami taso yi mata taqi bata hadin kai sai huci takeyi kamar ta kashe kowa haka takeji batasan meye yasa takejin haushin Rasheed ba ko ganinsa batason yi sauqinta daya dake tunda ta haihu Kumbo take hadata da magungunan da tasan bazasu cutar

da itaba so data fahimci ba hadin kai zata bata ba saita tattara mata ta zuba mata cikin kayanta ta hade mata komai washegari kuwa da wuri suka dauki hanyar 9ja aikam anyi tafiyar kurame Babu me cewa wani qala garama shi da Khamil suna hira jefi² inda suka sauka ta tsaya tana kallo bata taba zuwa Lagos ba hakanan takejin to Ina ya kawosu?" Bai bata damar tunanin mafita ba motar office dinsa tazo ta daukesu suka nufi unguwar da yake da zama tasha mamakin gidan da aka kaisu ta tsaya tana qare mawa gidan kallo.

Plat ne me kyau sosai Rasheed akwai son qyale² ya qawata gidan tsaf ta tabe baki tajishi ya saqali hannun Muneefah ta sakar masa ita ya nuna mata dakunan yace gasunan keda yaranki duka sun isheku fatan nasara" dakinsa ya shige da Muneefah tabisa da kallon takaici ta gyada kai ta bude dakin kusa da ita ta shiga komai na dakin a tsare yake sosai abin gwanin birgewa gefe ga wasu manyan set na akwatuna guda 12 ta zubawa akwatunan idanu tana tunanin to na meyene?" Tabe baki tayi tace "nima dai da son wahalar da kaina kulle dakin tayi ta cire kayanta ta bude akwatun da ta taho da ita ta dauko wata qaramar riga Mara hannu ta shafanta turaruka ta nufi bayi tayi wanka ta fito ta shafa mai ta zura rigarta ta haye gado taja duvet tunda ba sallah zatayi ba nan take baccin gajiya yayi gaba da ita batasan sanda ya shigo ya kwantar mata da Muneefah ba sai wajen hudu ta farka taganta kwance ya cire mata riga daga ita sai Pampers tanata baccinta.

Yunwa ce ta fafareta ta miqe ta fito tana hamma ta nufi kitchen din taji qamshi na tashi ta qarasa da sauri ganinsa tayi dagashi sai boxes da headphones a kunnensa ya zage sai yankan alayyahu yakeyi ta juya zata tafi ashe ya ganta taji yace "kije ki huta idan na gama zan sammiki nasan cikinki ne Babu alert shiyasa kika fito
Yayi tsammanin zata kulashi yaga ta juya tayi tafiyarta ta koma dakinta yaci gaba da girkinsa Yana waqoqinsa bayan ya gama ya jera a dinning ya bude dakin ya isheta tana waya daga yanayin wayar yasan da Mom dinsa takeyi ya shafa kansa ya juya ya fice, koda ta idar bata nemesa ba har ya sake gajiya ya shigo ya tararta ta hade kai da gwiwa tanata jan zuciya ya matsa gabanta ya tsugunna yasa hannu ya dago kanta ta zame kannnata yayi mata murmushi yace "kinajin meye game dani?" Batace masa komai ba ta fara qoqarin tashi ta nufi parlourn yabi manyan bombom dinta da kallo yana lasar lips dinsa ya lumshe idonsa Yana tunano rayuwarsu ta baya da irin soyayyar da sukewa juna, zuciyarsa ce tayi baqi idanunsa ya kada yayi ja daya tuna Kuma fah irin abinda takeyi masa shine tayima Kareem shima ko?" Tuni hasken zuciyarsa ya disashe yaji wani qunci a ransa a fili da qarfi yace "Oh God meyesa hakan ta farune.........."

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/28, 8:41 PM] Oum Hairan: Dafe kansa yayi ya koma ya zauna kalmar Innanillahi wa Inna ilaihir raji'un tana kaiwa da komowa azuciyarsa shi kansa Yana jinjina baqin kishinsa baya iya jurewa abubuwa game da Meenah tun kafin takai haka, qwafa yayi ya miqe ya fito falon tana zaune Muneefah tana wasa ya nufi inda yarinyar take ya dauketa suka nufi dinning ya hadansu abinci yanaci Yana bata tanajan gemunsa Meenah na satar kallonsa har suka gama ya miqe suka fice ta Isa ga abincin ta diba daidai cikinta ta shige dakinta taci tasha yourghut dinta taje tayi brush ta sake kwanciya Basu suka shigo gidan ba sai Tara na dare tana kwance Muneefah ta shigo Yana biye da ita da qatuwar yar tsanarta ta fada jikinta ta miqe tana mata dariya tace “sarkin yawo kin sama abinda kikeso ko Ina kukaje"
Gwarancinta ta rinqayi ya nemi guri ya zauna batako kallai ba taci gaba da wasa da yarta shikuma Yana kallonsu ganin ba zai samu arziqin kulawa ba yasashi miqewa ya fice ya shiga dakinsa ta miqe tana murmushin mugunta ta nufi bathroom tayima yarinyar wanka tasa mata kayan bacci ta kwantar da ita ta kulle dakinta da key ta kwanta,. Ba wuyar bacci gareta ba nandanan bacci ya dauketa sai Kuma kashegari da safen ma shine ya tasheta ya shigo cikin shirinsa na tafiya office tunda ya shigo suka hada ido ta kawar dakai tare da lumshe idonta ya matsa kusa da Muneefah yayi kissing nata ya zubawa fuskar Meenah idanu yana ganin yanda take qifqifta idanu yaja fasali ya sauke bakinsa a kuncinta yace “kin tashi lfy" ajiyar zuciya ta saki wata kasala na saukar mata tace “normal" murmushi yayi yace “gud zanje office me kuke buqata"

Kada masa kai tayi ya zaro kudi a aljihunsa ya ajiye mata yace “is ok akwai ma'aikata a gidannan idan na fita zanyi musu mgn zasuzo kowa zai gabatar miki da aikinsa idan kina

buqatar wani abu ko baby akwai dan aike saiki bashi" jinjina kai tayi ya sake sunkuyawa yayi kissing Muneefah ya fice tana binsa da kallo ita mamakin sanyinsa takeyi cikin kwanakin nan ta lura ya sauko sosai don ita kanta tasan da Rasheed din dane rainin hankalin da takeyi masa da tuni ya ladabtar da ita Amma yanzun ta fahimci kamar bama abun na damunsa.
Da wannan tunanin ta miqe ta shige bayi tayi wanka ta gyara jikinta ta fito tasa kayanta ta sanya dankunne ta nufi kitchen ga mamakinta a dinning ta tarar da kayan Karin kumallo ta fara budewa ko baa fada mata ba tasan aikinsa ne doya ce da taji qwai sai miyar albasa da attaruhu sai ruwan tea a flast da kayan hadi a gefe  taja fasali ta zauna ta fara bawa cikinta haqqinsa taji dadin break din sosai tana Shirin tashi ma'aikatan suka shigo mace daya maza biyu suka gaisheta ta amsa musu macen tace “ranki ya dade ni sunana Jummai daga Daura  Yallabai ya kawoni nan aikina shine shara da mopping da wanke² sai kula da Muneefah yace tsarin gdansa baa masa girki shine yakeyi ko Kuma ke kiyi" jinjina kai tayi dayan yace “nikuma sunana Hadi duk abinda ya shafi fita unguwa da aike zuwa waje alhakinane" juyawa tayi da dayan yace “nikuma dan ruwa ne aikina shine kula da fulawa da wanki da guga ranki ya dade sunana Badaru" yanda yayi mgnr yabata dariya tayi murmushi tace “yayi kowa yaje yayi aikinsa"

Godiya sukayi suka fita kowa ya kama aikinsa Jummai ma ta fara gyaran falon ita Kuma ta shiga dakinsa ta gyaro ta kunna masa turaruka ta fesa na fesawa ta wanke toilet ta fito ta shiga nata shima ta gyara biyun da suke rufe ne kawai bata shiga ba ta koma tayi kwanciyarta ta rashin aikinyi har daya sannan ta fito ta dora girki Jummai nayi mata hira har suka gama suka Muneefah nata wasanta tayi wanka ta shirya cikin wata atampa blue tayi mata kyau dinkin doguwar riga me aljihu tayi sallar la'asar  ta kunna kallo tana kallo tana chat har biyar sannan taji tsayawar motarsa ya shigo da kaya niqi² a hannunsa Jummai ta miqe tana masa sannu da zuwa itakuwa hakimar kawar dakai ma tayi yasan tayi ne don yaji haushi yayi murmushi ya aje kayan yace “barka da gida ranki ya dade Allah ja kwana ya qara lafiya fulanin gobe" duk yanda taso da shareshi dole Saida yasa tayi murmushi tace “sannu da shigowa" cire rigarsa ta sama yayi ya rage dagashi sai singlet ya qarawa A.C gudu yace “nasha wahala yau inata qoqarin naga tafiyar nan bata ritsa dani ba Amma Saida ta fado kaina Meenah banson tafiya nabarki wlh....." Ai tuni ta fara hada gumi ta juyo da sauri tana cizge dankwali tace “tafiya Kuma Baffa'am tab wlh aa bazaa Kuma sakani a tara ba nikam qafata qafarka"

Murmushi yayi Yana kallonta a zucci yace yar iskar qarya zanyi maganinki ta ruwan sanyi ni zakiyiwa hauka! Amma a fili sai yace “to ya zanyi Meenah Babu damar tafiya da iyali Australia sunada mugun sanyi dole sai kaje kaga yanayin gurin tukunna ko zaka dauki iyalinka Kuma ma Banda abinki mu ai zaman gaba mukeyi Inna tafi dake amfanin me zakiyimin abinda bakaso ai

nesa kakeyi dashi ko?" Girgiza kai tayi ta zame qasan kujerar tace “nikam mubar batun wasa wlh nasha wahala a wancan karon har zaucewa Saida nayi Saida Mom da Mai Martaba suka rinqa sawa ana yimin addu'a sannan na dawo hankalina ya Rasheed don Allah ki million nawa ne kabasu subarmin kai a gida ni idan bamaka dashi zansai da shanuna da Kaka ya karbarmin gurin dangin mahaifi na nabaka kabasu subarmin kai kaji?" Tana mgnr muryarta na rawa. Shima zamowa yayi ya zauna a gabanta ya riqo hannunta yanajin wani spark na jijiyoyinsa saboda rabonsa da riqe hannun mace haka shekara an tafi takwas kenan, jan wani numfashi yayi yace “kinaso na ne?" Tambayar ta daketa ta dago da sauri idanunta ya kawo ruwa yayi saurin dora hannunsa a bakinsa yace “aa ba kuka ba tambaya ce my Meenah kinasona?" Daga masa kai tayi ta fada jikinsa ta rushe da kuka tana cewa “don Allah don Allah Ya Rasheed please kada ka sake tafiya kabarni wlh zaucewa zanyi....." Hade bakinsu yayi ya lumshe idonsa yanajin wata natsuwa na shigarsa shaidan na qoqarin tuno masa da abubuwa Yana yaqarsa daqyar yayi galaba akansa ya koreshi ta hanyar zarmewa wa tabe²nsa itakam lumshe idonta tayi banda hawaye Babu abinda takeyi ganin Yana qoqarin zaqewa Kuma tasan kowanne lkc Muneefah ko Jummai in sunji shiru zasu iya fitowa yasata janyewa.

Kafin ta gama daidaita natsuwarta ya sunkuceta sai dakinsa ya azata a gadonsa ya turmusheta tana tureshi tana komai yaqi barinta sai rawar jiki yakeyi da ta murya Yana cewa “Mee.... Meenah.... please..... Long time banci ba wlh tunda nabarki banqaraci ba banqara sha'awar ciba sai da kika dawo rayuwata kibarni naci naji da...din...ki...."
Batada mafitar data wucce qyaleshin duk da tanajin fargaba koda yake tasan duk masifar Rasheed baikai Kareem ba saidai shi dabanne Yana bata nutsuwar da takeji a ranta Babu me bata kamarta sambatunsa kadai ya isa gamsar da mace me gajeran zango, Rasheed ya mayar da qwalamarsa a wannan yammaci anci amarcin gaske taji a jikinta koda komai ya kammala gumi ta rinqa hadawa ga ciwon jiki tare sukayi wanka yanata narke mata kunyarsa ma ta kamaji saboda ta fahimci shi baya da kunya ko kadan akan wannan abun.
Bayan sunyi wanka sukayi sallar magrib da ake binsu sukayi Isha sannan suka nufi dinning sukaci abinci yanata zubanta shagwaba itakam duk jikinta yayi sanyi ta dago idonta tace “amma Ya Rasheed ka fasa tafiyar ko?" Murmushinsa na Izza yayi mata yace “sai yanda ta yuwu"

Miqewa tayi ta shige dakinta ta haye gado ta zauna ta zuba uban tagumi itakam ta tsorata da wannan al'amari batajin zata iya yarda ya tafi ya barta idan ta tuna da hakanma hawayenta nunkuwa sukeyi ita da kanta takeji ashe zuciyarta tashice har yanzu ashe Baffa'am dinta bashida na biyu har gobe a duniyarta to meye yasa da ta farajin haushinsa?"
Jinjina kai tayi tana qissima ta yanda zata fara rayuwa cikin zulumi sai ta dauki wayarta kamar ta kira Kumbo Hami ta fada mata sai Kuma taga kamar bai dace ba haka ta rinqa saqawa da

warwarewa har dare ya fara nisa ta shiga tayi wanka ta dawo ta kwanta abinka da farar fata idanunta har sun kumbura koda Jummai ta kawo mata Muneefah cewa tayi taje su kwanta tare ganin kwanciyar bazata kaita bane tasata tashi ta sake alwala ta dauki qur'ani tana karantawa tana hawaye.
Shigowa yayi dakin mamaki ya cikashi jin shassheqarta ya kunna globe din da sauri yaganta rungume da qur'ani tana rera kukanta ya qarasa gareta ya zare qur'anin ya aje ya dagota ya mannata da jikinsa yace “meye kikewa kuka Meenah kinsani ko a baya bana qaunar kuka ko?" Maqalqaleshi tayi tana qarawa kukanta gunji tace “ni don Allah kace ka fasa tafiya kabarni wlh zanyi maka duk abinda kakeso" dariya tabashi sosai ya shafa kanta yace “to na fasa saime Kuma?" Rungumeshi tayi tana ajiyar zuciya tace “shikenan idan sun matsa ka bar musu aikin kawai kaji?"

Daganta kai yayi ta shafa sumarsa tace “na gode Baffa'am...." Janta yayi suka zube a gado ya fara luguiguiceta ta saki masa jiki kuwa suka raya Daren da wata irin azababbiyar qauna me narkar da zuciya sun gurji juna sosai tanajin sabuwar qaunarsa na ratsata, tun daga wannan dare komansu ya fara saituwa cikin ruwan sanyi da dabara ya shawo kanta riritashi takeyi kamar qwai bata yarda ta tabashi saboda karma yaji yanason tafiya yabarta shima mugun tattalinta yakeyi Abu daya yaso Basu damuwa tanason zuwa Daura watanni sun fara nisa tanason taje taga Mom Amma fir yaqi tun tana lallabashi har Saida suka daina mgn ta daina kulashi da ya matsa mata sai ta kama kuka tace don yaga batada galibi ne batada uwa bata da uba shiyasa yakeson ya nuna mata Mom ba ita ta haifeta ba.
Sosai ya fahimci Meenah yar sharri ce ta qaro  wulaqanci dole ya shiryanta tafiya Katsina aikuwa tayita murna shikuma yayita kumburi zuciyarsa na basa kawai so take taje taga uwar mijinta ta tuno da ubar yarta Kareem idan zuciya ta raya masa haka sai kawai yaji koma me zatayi tayi bazai barta ba  ranar data shirya tafi tun asuba take shiri yayi kwanciyarsa yaqi fitowa harta shirya ta shirya Muneefah ta shiga dakin nasa da sallama ya Amsa mata a ciki ta zauna tace “Baby na shirya banga kana shiri ba Kuma kace kaine zaka kaimu airport" iska ya furzar yayi miqa yace “ina zakije ne?" Da sauri ta dubesa tace “Ban fahimta ba Daura Mana" hade rai yayi yace ba yau ba..." Ai baigama rufe bakinsa ba ta miqe tana cewa “haba don Allah Ya Rasheed kada kayimin haka wlh na fadawa su Mom dasu Ya'isha yau zanzo har Sarki junior fah na fadawa yanata murna hatta Amrah da Addah Abulle sunata murna zasuga Muneefah....." A fusace yace “shut-up Meenah nace bazakije ba yau ki fita ki bani guri dama nasan dokinki kije kiyi hirar tsohon mijinki kiji dadi ko? To bazaki ba idan kika matsamin ma wlh zan iya cewa keda Daura har abada muga ta tsiya"

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/29, 8:00 PM] Oum Hairan: Tsayawa tayi ta zuba masa idanu tanajin ciwon yanda yake canzawa duk motsinta fassara hadiye wani abu tayi me daci ta juya ta fice daga dakin ta koma nata ta hade kai da gwiwa tanajin baqin cikin wannan wulaqancin na Rasheed Shi komansa baya aikatashi da lissafi kawai abinda yayi masa dadi shine yake aikatawa, kwanciya tayi tanajin Muneefah na buganta qofar taqi budewa tasan abinda zatayi masa kawai ta bata masa rai kenan.
Ilai kuwa yarinyar ta riqa kuka ya taso ya fito ya isheta a qofar dakin taqi bude mata ya dauketa ya juya ya shiga dakinsa yasa kayansa suka fice so take y kulata bakuma zai kulata dinba, tun tana tsammanin dawowarsu harta hqr ta tashi ta shiga kitchen ta dora musu abincin Rana sai daya da rabi ta gama tayi wanka tayi sallah ta dawo parlour Kiran Mom ya shigo kasa dagawa tayi saboda takaici meye ma zatace mata? Da wannan tayi qarfin halin daga wayar suka gaisa tace “munjiku shiru" kukan da take hadiyewa ne ya kwace mata tace “mom zamuzo Amma ba yau ba" tana fadin haka ta sauke wayar a kunnenta ta kwanta taci gaba da karatunta.
Sai biyu da rabi suka shigo da tarkacen kayan wasansu ya aje yarinyar ya zauna a gefenta daga kallo daya bata qara kallonsa ba ya sanya hannunsa ya dage rigarta da sigar zolaya yace “ 4 mouths kinqi karbar ajiyata sai zuba miki vitamin nakeyi kina shanyewa Babu wani good result" sake dauke kanta tayi daga gareshi tama fara yunqurin miqewa ya saqaleta ta baya ya miqe ya hadeta da jikinsa yace “meye kuma ya faru My Meenah Baffa'am dinki baison fushinki kin sani"

Tureshi tayi tace “ai dama nasan bakaso Baffa'am ka rabu dani please kada kasa na fada maka mgnr da ubangiji zaiyi fushi dani" qwacewa takeson yi yaqi sakinta saima qwalawa Jummai Kira da yayi yace ta dauki Muneefah, itadai kunya kamar ta nutse shikam Babu kunya ya dagata cak ya nufi cikin dakin baccinsa da ita ya cillata a gado ya bita ya hade bakinsu tana kuka tana tureshi yaqi turuwa saima zuge zip na rigarta da yayi ya cafki boobs dinta ta rintse idonta bataso yake taba mata nono kwana biyunnan zafi sukeyi mata gashi shi Kuma mayensu ne tanaji ya

dora bakinsa a kuncinta yana tsotse hawayen har ya gangaro qasa ya sanya harshensa tsakiyar qirjinta Yana lasa zuwa kan nipples dinta, takasa qwatar kanta dole ta hqr tanajinsa yayita karakaina a sassan jikinta Yana bawa kansa nishadi taqi kulashi taqi tayashi sarai yasan yau dama tunda ya tabata itama saita tabashi shiyasa bai damu ba yayi abinda zaiyi ta kwanta masa kamar gawa ya gama ya sauka taja bargo ta rufe jikinta, waishi me zuciya ya rinqa jan tsaki tanajinsa tayi banza dashi yaje yayo wanka ya dawo ya dubeta yace “ki shirya jirgin biyar zamu bi zuwa Katsina"
Banza tayi masa tama sake gyara kwanciyarta ransa ya sosu sosai yace “wai meye yasa kika rainani mgn fah nakeyi miki Meenah" dagowa tayi ta watsansa wani matsiyacin kallo tace “bazani bane nakeso ka gane" murmushi yayi ya juya zai fice Saida yaje bakin qofa yace “ni nake baki umarni kike cewa bazakiyi ba ko Meenah lallai kin kawo qarfi saura qiris ki fara dukana" baiyi tunanin zatayi mgn ba yaji tace “idan iyakar dukan ma zan tsaya ai da sauqi"

Tsayawa yayi kamar zai dawo sai Kuma taga yayi gaba taja tsaki ta tashi tayi wanka ta koma ta kwanta har hudu da rabi Yana jiranta a parlourn baiji motsinta ba ganin lkc nata shudewa Babu ita yasashi nufar dakin a fusace ya isheta kwance abinta ya tsaya akanta Yana kallonta taji shigowarsa tayi masa banza takaici ya cikasa yace “kefa nake jira Tun dazu nayiwa Hadi mgn yanacan yana jiranmu" tabe baki tayi ta miqe tace “Allah ya tsare hanya ku gaishesu" zubanta ido yayi Yana qanqancesu cike da bala'i yace “kada ki fusata zuciyata ki tashi nace kafin ranki ya baci" murmushi tayi ta miqe tace “aini Raina ya dade da baci saidai naka ya baci zuwa ne bazani ba duk abinda zakayi kayi" duk yanda yake tunanin zata sauko taqi saurararsa ya rasa yanda zaiyi da ita baitaba tunanin kafiyarta takai hakanba ganin wankin hula na neman kaisu dare ya kira Kumbo Hami ya fada mata abinda yake faruwa ta Kira wayarta tanata yimata fada kan dole ta fito suka tafi har sukaje Babu me yiwa wani mgn.

Sosai kowa yayi mamakin zuwan nasu musamman Mom da ta gama fidda rai murna gurinsu baa cewa koma suna hutawa ana gama gaisawa ya dubeta yace su tafi gdansu shi ya gaji da dawo da safe, Babu yanda ta iya haka suka tafi Mom tanata Sanya musu albarka duk yanda Meenah taso ta gaisa da Addah Abulle hanata yayi sai Muneefah yabari anan a cewarsa ai itace dolensu.
Bata tankasa ba saboda ta lura sanadi yake nema suka Isa gdan batasan da ya ginashi ba ya qawatu sosai iyakar qawa anci uban naira s ginin gdan suna zuwa ta shige dakin da yayi mata ta kulle ita a dole har yanzu fushi takeyi shikuma gashi da baqin naci hakanan yabita suka kwana sunajin haushin juna dake yasan tun farko shine ya tabata bai wani damu ba da safe ma ya fice yabarta da sabuwar motar daya siya mata mahadin lefan da yayi mata na dawowarta yace idan ta gama abinda takeyi ta tafi shi akwai wani aiki daya bayar akeyi masa zaije ya gani.
Bayan ya fita ta gama abinda zatayi ta shirya ta fice can ta tarar da Amrah da Ya'isha suka baje

sunata hirarsu sunata yimata tsiya waitayi qiba ta zama uwar mata sai shirga qiba takeyi saidai tayi murmushi kawai.

Rasheed bai shigo gdanba sai dare turakar Mai Martaba ya wucce suka taba hira har goma sannan ya shigo suka qara gaisawa da mutanen gdan Sarki junior ya maqale yace sai antafi dashi suka fice dole nan tabar tata motar ta shiga tasa da yaransu biyu suka tafi suna tafe yana satar kallonta Yana hira da yaransa wai ita fushi takeyi har yanzu, da sukaje ya budewa Sarki junior dakinsa rakashi yaron ya kwanta bacci ya daukeshi ita Kuma ta shige nata tayi wanka tayima Muneefah suka kwanta cikin bacci taji wayarta na ring ta wawura ta dauka yayi miqa tare da cewa “Ina buqatar tea" miqewa tayi tayima Muneefah addu'a ta nufi kitchen din ta hadansa tea ta nufi dakinsa ta bude Yana kwance bisa kujerar hutawa ta aje masa ta miqe ya riqota ta fada jikinsa ya matseta yana shaqar qamshinta me ratsa zuciya yace “ya kamata a daina fushin nan haka please na tuba" turo baki tayi yasa harshensa ya lashi lips dinta yace “kinsan cewa idan kina fushi kyaunki qaruwa yakeyi idan Kuma kikayi murmushi wane Sarauniyar kyau my Meenah inasonki saman sosai meye yasa muke yawan samun matsala ne?"

Kwantar da kanta tayi jikinsa tace “idan kana bari zuciyarka na rinjayarka kana fassarani inda ban nufa ba zankejin ciwo Ya Rasheed naqi samun nutsuwa naqi kwantar da hankalina na kasa zama Ify da Kareem saboda kai Saida takai ko mgn idan ba taka Ya Kareem zaiyimin ba banida Ikcn hira dashi shi yasani ya zauna dani Kuma a haka a qarshe daka bayyana na dagansa hankali da taimakon mahaifiyarsa da bata qaunata dashi muka rabu badon yanaso ba, nasan Ya Kareem yanada yaqinin idan ya matsamin zan iya komawa hannunsa tunda bashi da haqqina Amma a hankali ya rinqa bina a qarshe ya fadamin ya barni ne saboda yasan kai nakeso bashi ba kuma bazan iya canza hakan ba saboda son ba shawara yayi ba wajen shigata, Ya Rasheed sai nake tuhumar kaina meye yasa kaidin Dana zaba Kuma ka kasa yarda dani kullum rigimarmu akan shudadden abune wanda yariga ya wucce har abada bazai dawo ba?"
Jikinsa ne yayi sanyi ya shafa dogon gashinta ya hura mata iska a fuskarta ta bude idanunta akansa ga mamakinta sai taga qwallah nabin kuncinsa tasa hannu ta share yaja numfashi yace “ina tsananin kishinki ne Meenah wato ubangiji yayi gaskiya daya zartar da wannan hukuncin tabbas da a gaban idona qaddarar rabon Muneefah yasa na rabu dake Kareem ya aura wlh tallahi zan kasheshi ne har lahira so sai Allah ya boye al'amarinsa shin waima kinsan cewa Hajiya Bilki tana gdan yari?"
.

Zaro ido tayi tace "Akan me?" Murmushi yayi yace “saboda ta cutar dani ashe duk abinda ya faru dani sa hannunta ne kawai don naqi auren yayanta Meenah ta rabani dake bayan ta rabani dake ta cillani duniya na tafi matsayin mara galibi bayan na bace Kuma rashinki ya sanya tunanina zama me rauni har takai na samu matsalar data zamemin tambari da bazai goge ba iyakar cewa da rubutawa cikin files dina na taba ciwon hauka da loosing memories kadai ya isa cutarwa balle rabanin da tayi dake"
Numfashi ya sauke yace kuma kinsan cewa  yarta Khadija itace ta tona musu asiri wai taji suna qulla zasu farraqa tsakaninmu susa Mana tsanar juna shine tazo ta zayyanewa Mai Martaba komai  shikuma baiyi wata² ba yasa aka kamesu yanzu haka shari'a zaa fara ranar Litinin" sosai lamarin ya tsuma ta tabbas duniya ta jima da cika da azzalumai da  Babu hisabi a lahira da anci bulus Allah ka tsaremu da imaninmu...........

Juhud is not free read... regular 300  VIP 600 via👉🏼 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank

Then you show ur evidence via WhatsApp 09013718241...

Juhud ba littafin kyauta bane ki biya  300 regular VIP 600 kafin ki karanta ta wannan account din 0255526235 Fauziyya Tasiu Umar GTbank ko katin MTN pls ban buqatar vtu hoton katin ko digit number ta WhatsApp number 09013718241.....

*Oum Hairan*
[8/30, 8:55 PM] Oum Hairan: Bai bata damar dogon tunani ba ya miqe ya fara Shan tea dinsa da biscuits bayan ya gama ya nufi bathroom ya watsa ruwa ya dawo daure da towel ya shafa mai ya kashensu fitila yaja masu labule suka tsunduma duniyar da duk wani masoyan ma'aurata suke kasancewa a ciki, tun Daren ta farajin yanayin zazzabi hakanan dai ta rinqa daurewa har zuwa wayewar gari bata Bari ya fahimta ba ya fice kasancewar zasuje anguwa da Mai Martaba ita Kuma ta fara hidima da yaranta Saida ta shirya Sarki aka daukeshi zuwa school sannan ta samu damar sake kwanciya nan sabon zazzabi yayi mata dirar mikiya.
Tananan kwance Allah ya jefo mata Aunty Hamida yanda ta tarar da ita a nade tana rawar sanyi yasata fahimtar da matsala. Tambayar ta tayi tayi mata bayani ta dubeta sosai tace “kuma ba cikine dake ba?" Saida gabanta ya Fadi da taji ta ambaci ciki lallai har yanzu da sauranta da sauri tace da Aunty Hamida “nawa ga watan musulumci?" Duba calendar tayi tace “bakwai ga sabon wata" dafe kanta tayi tace “ya Salam wlh akwai yuwuwar hakan ne  23 nake period fah....." Dariya Aunty Hamida tayi tace “banga na biyunki a rashin hankali ba Meenah har yanzu

baki hadu gabadaya ba to ai yanzun saiki fara lissafi" jan numfashi tayi ta koma ta kwanta tace “banso ba Aunty Hamida har yanzu Muneefah bata shekara biyu ba fah" murmushi tayi tace “ai kinja Ikc kiga fah su Ya'isha da akayi aurensu a bayan naki daga me yara uku sai me hudu kekam biyu haba Meenah ita haihuwa kayita tunda qarfinka"

Batada yanda zatayi dole ta tattara tayima kanta fatan Alkhairi sukaci gaba da tattaunawarsu wajen azahar Rasheed ya shigo Aunty Hamida tace “nice zan fara yimaka albishir mun samu qaruwa Meenah ta kusa sake sunkuto Mana baby kyakkyawa" wani ihu ya saki ya zauna kusa da Meenah yace “haba don Allah da gaske kike Wai hakane My Meenah" kawar dakai tayi cike da kunya ya dago kanta ya saukenta kiss a lips dinta yace “naso wannan Allah ya rabaku Ify Wife kinsan me?" Daga ginin makarantarki nake komai ya kammala primary da Secondary din an zuba duk wani abu da ake buqata na aiki yanzun sauran diban malamai"
Da rashin fahimta ta dubesa tace “Makarantata Kuma?" Murmushi yayi yace “Oh Sorry na manta ban fada miki ba diamond dinki da old gold dinki aka siyar diamond din ansai dashi 5.5 million gold din Kuma ansai dashi 2.7 million so sai mukayi shawari da Mom akan meye zaayi miki da kudin Wanda zai amfaneki ya amfani Al'umma so shine aka Gina masallaci a garinku kasancewar suna fama da matsalar rashin ruwa da rashin gurin ibada in akayi ruwa saidai suyi a dakunansu an Gina Bohol guda biyu a farko garin da tsakiyar Wandu masallacin Kuma a tsakiyar garin aka ginashi da niyyar ubangiji ya rinqa kaiwa iyayenki ladan, so abinda yayi saura sai aka yanke shawarar Gina makaranta Boko ce hade da islamiyya da Kuma tahfeez yanzu haka sun kammalu komai da komai kinada rarar 2.9 million a account din Sarki junior yanzu yau nasa gidan TV na NTA da AIT Da Kuma Arewa24 sunzo sun dauka tallan makarantar zaa fara tallatata mun Kuma fitar da sanarwar daukan qwararrun malamai domin samun abinda ake nema am kisan meye sunan makarantar?"

Girgiza kai tayi hawaye na kwarara a idanunta yayi murmushi ya goge mata hawayen yace “MahfAish academy sunan yayanki Mahfuz Aisha academy....." Rungumeshi tayi ta rushe da kuka tana kissing dinsa ta ko Ina tace “Banjin akwai wata kalma data saura a duniya da zanyi maka gdy da ita mijina Allah ya azurtani da mafi qololuwar alkhairin duniya daya hadani da miji na gari Ina alfahari da samunka matsayin uban yayana Allah yabarmin kai ka dade kayi qarko...."
Gabaki daya sun shagalce a gurin sun manta da anyi ruwan Aunty Hamida itadai data fahimci sun manta da ita sumsum ta miqe tabar musu gdansu suka shagalce a gurin dama tunda aka tafi da Sarki school aka dauke Muneefah
Kwanaki sukayita tafiya komai Yana tafiya cikin nasara rayuwa tanata albarka abubuwa duk suka rinqa shudewa Mom itane ta takura Meenah akan sai ta ziyarci dangin mahaifinta badon

taso ba haka Rasheed ya dauketa sukaje har Jos suka shiga rugarsu abin mamaki bata taba ganin rugar data samu ci gababa kamar rufar Wandu an gyara musu ita harda makaranta da hanya ga wutar NEPA ta aminta mutane duniya sukeyima bauta Wai yau itace Baffa Ribado da Baffa Bangel suke kuka suna bata hqr akan abubuwan da suka faru da irin sharrance sharrancen da suka rinqa yi mata.
Murmushi kawai takeyi tana share hawaye Ikc bayan Ikc da dare ne bayan komai ya lafa take tambayar Ina Hammah Manga nan aka zauna ana bata labarin Wai an kasheshi a dalilin kidnapping din wani Dan siyasa da sukayi sojoji sukaje sukayi barin wuta akansu ko gawarsa baa tsinta ba.

Sosai ta jinjina lamarin tare da yimasa fatan rahama ta kwana dayanta a dafe wai saigashi sune harda soya mata manshanu da tatso mata danyar Madara Baffa Moddibo yayima Sarki da Muneefah kyautar saniya aikuwa Sarki yace saidai a daukar masa abarsu dake ba wata babba bace Rasheed da taya bera Bari yasa aka daureta aka sanyata a mota sunata yi musu dariya suka dauki hanya cike da jin dadi zuciyar Juhud yan uwan da suke qyamarta yau itace suke qauna sunata Sanya mata albarka da abubuwan alkhairin da suka samu ta dalilinta.
Cikin wata biyun da sukayi suka juya Lagos hada kan yayansu suka tafi daga Muneefan har sarkin aka Sanya a makaranta taci gaba da rainon cikinta suna qara samun shaquwa da kula da juna da haka cikinta ya isa haihuwa ta dawo Daura Kwananta uku da komawa kuwa ta sunkuto yaranta uku wannan abu ya tsuma dangi ita kanta tayi mamaki saboda cikin nata ba wani shararren girma yayi ba sannan ko a hoto biyu suke cewa da ita sai gata da uku duk maza nan fah wannan family ya kacame kowa mgnr haihuwar yakeyi ranar suna yaran sukaci sunan Babban Haroon mai bi masa Abubakar sai Abdulkareem qaramin aikuwa ansha shagali kamar baa taba yiwa wannan Fam Haihuwa ba kama daga Daura Mali da Jos kowa yayi bajinta su Rasheed harda kyautar kujerar hajji yayima mutum uku Baffa Moddibo da Baffa Ribado da Baffa Bangel saboda murnar wannan haihuwa.

Bayan komai ya lafa yaso su koma Lagos ta kafe Saida tayi arba'in sannan suka koma da qarin me raino daya Ladi itama mutuniyar kirki sukaci gaba da rayuwarsu cikin gdyr Allah da amincewarsa Rasheed kullum likkafa ci gaba takeyi yau matsayin General Rasheed Gen Mahfuz yake amsawa inda makarantar Meenah kullum take qara habaka abin gwanin birgewa da hamdala shekara biyu Meenah ta qara haihuwar ya mace daga kanta tace ta gama abinka da yan bokon qarshen zamani suka fita India aka juyar da mahaifar gabadaya ta dawo taci gaba da kula da yaranta.
Sannu a hankali maqiyanta irinsu Fadila Dada Hanne Hajiya Bilki da wasunsu na boye sai gashi duk sun zama yan koranta idan taje Daura har zuwa sukeyi gaisheta musamman Fadila data zame mata kamar aminiya yanzu duk duniya bata da qawar data wucce Meenah hakan ya

samo asali ne daga yanda Meenah ta shiga ta fita taga sun daidaita da mijinta ya mayar da ita dakinta cikin yayanta, itama Addah Abulle daqyar bayan auren datayi Mai Martaba ya dawo da ita dakinta inda ta dauki soyayyar duniya ta dorawa yaran Meenah guda biyu Muneefah da take yar danta da Kuma Kareem qarami da yaci sunan danta duk wani tanadinta nasune sauran jikokin gdan har tsiya sukeyi mata wai ita ta fiye son kai, itadai Meenah saidai tayi dariya tana mamakin yanda komai ya wucce kamar ma baayi ba idan tai tsai sai kawai taji hawayena tsiyaya a idanunta da zaran ta tuna yanzun muma duka wataran shudaddu ne gushewa zamuyi a manta da tarihinmu mu dusashe kamar baa haliccemu ba, a wannan ritsin tsoron Allah yake qara ziyartar ruhinta takanji duk duniya tayi mata zafi kullum addu'arta Allah kada ya jarabci yaranta da irin jarabtarta Allah ya Basu qaddara me sauqin dauka ya Sanya musu albarka cikin cinsu da shansu da motsinsu a kowanne yanayi yabawa mijinta qarfin gwiwar nemo halal a ko Ina take.

_Tammat bi Hamdullah_

_Tabbas komai yayi farko zaiyi qarshe yau dai Juhud yazo qarshe Ina gdy ga ubangijin bayi me kowa me komai daya bani ikon farashi da kammalashi lafiya kamar yanda na tsara._
_Kurakuran dake ciki ubangiji ya yafe Mana badon halinmu ba amfanin ciki Allah ya bamu ikon amfana baki daya._
_Bazan rufe ba sai nayi gdy gareku masoya da baku qasa a gwiwa wajen qarfafamin gwiwa da kudadenku da Ikcnku tabbas Ina alfahari daku Ina fatan ubangiji ya sadamu a dausayin zumunci na masuyin soyayya dominsa._

_Kada ku manta next book dina _*YAFI ZAMAN AURE!*_ _yananan tafe da irin tasa rikita rikitar very soon insha Allahu._

_*Oum Hairan*_

. ************************⬇*********************
************   Ai Hausa Novels  ***************
************************⬆*********************

DOWNLOAD More complete Hausa Novels, Education Books, Adventure, Drama, Mystery, Religion, Fiction, Non-Fiction, Romance, Meimor, True Life Stories & Others from our blog.

Visit > https://www.aihausanovels.com.ng

Ka tura mana sako ta adireshinmu na email, domin tuntubarmu ko turo mana hausa novel ko kuma post.

Email > aihausabooks@gmail.com

******* FOLLOW US ******

Facebook: Ai Hausa Novels

Twitter: Ai Hausa Novels

Telegram Channel: https://t.me/Aihausanovels

Haka kuma domin shiga kowanne daga cikinsu za ku iya ziyartar shafin ku yi search na AI HAUSA NOVELS, hatta facebook group dinmu ma za ku samu.

********************** ⬇ **************************
*************** Ai Hausa Novels ****************
********************** ⬆ **************************